💗💗💗💗💗💗
YANCINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

*NA*

*AYSHA A BAGUDO*

DEDICATED TO
MRS ADAM
(YAR MUTAN KAGARA)

PAGE 1 to 5

......Mota ce kiran honda accord  ke sharara gudu akan titin ilupeju dake kan Express din mushi road ,yayinda wata mata  ke zaune abayan motar, sanye cikin wasu had'add'un kananan kaya ,wando jeans da Riga pinky, kanta  kwance da gashin attachement har gadon bayanta wanda ya sha gyara.

"wata yarinya wace bazata wuce kimanin shekara tara zuwa goma ba, ke kwance a saman cinyar wannan matar ,tana fidda numfashi sama sama tamkar me cutar asma .
kuka  sosai wannan matar take hannuta rike da gorar ruwan roba tana shafawa yarinyar a fuskarta, saboda  numfashinta dake barazanar  d'aukewa daga gangar jikinta .

Cike da matsanancin tashin hankali  wannan matar tace "Dan Allah malam ka taka motar nan sosai," kayi sauri dan Allah mu samu mu isa asibiti nan da wuri ,tun kafin wani abu yasamu yarinyar nan nashiga uku takarasa maganar tana sake yayyafawa yarinyar ruwa ,direban  yace "Baiwar Allah gudu fa nakeyi sosai ...

ganin numfashin yarinya yayi kasa sosai fiyye da d'azu  al'amunta numfashinta na daf da tsayawa ,yasa wannan matar sake yin magana a matukar firgice.
"Dan Allah malam k'ak'ara sauri kar kabari yarinyar mutane ta mutu a hannuna, dan Allah dan Annabi ka k'ara gudu idan yarinyar nan ta mutu zan shiga tashin hankali mara misaltuwa ....

A tsawace direban yace  " what are you saying?
"do you want me to be involved in a car accident because of you ?
"da kikewa wa mutane zancen banza...

"Wayyo Allah nashiga uku "wannan wani irin maseefa ne haka, ke kokari samuna?
"me zancewa iyayen yarinyar nan ?

" me zance yasamu 'yarsu?

"Dan Allah malam, ba dan halina ba saboda Allah kayi hakuri kayi sauri..

" see I have already gotten to my speend limit, how much did you me?
"da kike kokarin na kashe kaina akan matsalarku ya ja tsaki tare da meida hankalinsa da natsuwarsa kan tukinsa ...

Numfashin yarinyar sai sake yin kasa yakeyi gabadaya idanunta sun gama birkicewa yasa matar tace "oh my goodness God have mercy on me "malam ,kindly speend up plz !

Direban yace " I can't speend more than this in this area.

cikin zafin rai yacigaba da magana "Oh my God which kind of people boarded my car this morning .

"sai da zuciyata ta gargad'eni akan d'aukarku da zanyi, amman naki bin umarninta "me yasa na d'aukeki da irin me wannan ciwon alhalin ban makance ba ?

"gasky daga yau zan dinga lura da irin mutane da zan dinga d'auka most especial irinki, ko dayake na yi mark din face dinki bama zan sake wautar d'aukarki a motata ba.

Gabadaya matar nan tagama firgicewa ta rud'e iya rud'ewa sai gumi ne ke keto mata ta koina a gabadaya ilahirin jikinta, banda sambatu babu abinda take ", wayyo Allah hummm ...am..am "malam Dan Allah karkaji haushina kayi hakuri ka duba halin da yarinyar nan take ciki ,kayi gudu ko dan gudun abinda zai sameta..

"Dan Allah matar nan karki dameni , ki shafamin lafiya mana "ina kan yin iyakacin bakin kokarina ,I can't kill my self for you..
fly kikeson nayi akan titi ko me ? inji cewar direban .

Muryarta cike da matsanancin kuka tace" bance ka kashe kanka ba, ko kazama tsuntsu akan titi ba ,but at least ka duba yanayin da karamar yarinyar nan take ciki " karkayi silar shigata maseefa da tashin hankali ,na gaya maka idan wani abu yasamu yarinyar nan karshena yazo, domin zan rasa aikina akanta " kaga kalli ga wani traffic can gabanmu ..

"Eh nagani me za'a yi da trafic?

" idan kakaraso gurin ka karya hannunka na hagu .

"Na karya hannuna hagu kuma ya tambayeta a wulakance?

Tace "Eh .

shi kuma sanin da yayiwa hanyar bata da kyau, yasa yaki bin hanyar hagu kamar yadda tace

yasoma kokarin bin dama.

tasaka wani irin firgitaccen kara "Ina kuma kake kokarin bi ?
" kai da nace maka kabi hannunka na hagu .

"Wayyo Allah ni dai yau nashiga uka nashiga motar wahala , kana bukatar kabi hannunka na hagu ba dama ba ..

" wai me ke damunki ne wannan matar ?
"baki da ido da hankali ne ko me ?
" bakiga hanyar bata da kyau bane dazaki dinga min ihu akai ,wallahi idan kika dameni zan saukeku anan ku nemi wata motar.

" ni dai Dan Allah ka koma Kabi hannunka na hagu idan baso kake kayi silar rasa rayuka guda biyu ba alokacin daya acikin motarka ba..

" yaya kike son nayi I have told you this road is not good yayi maganar a zafafe ..

ihu da masefa take masa ganin yaki sauraronta sai tuki yake hankali kwance, cikin kankanin lokacin taga ya bullo wata hanya wanda yayi daidai da hospital din, take ta sauke wata irin naunayen ajiyar zuciya "yauwa a she dai kasan abinda kake, ga hospital din da zamu shiga can mun iso ta nuna masa da hannunta "ai na d'auka wawa ne kai bakasan hanya ba shiyasa kaji ina ta maka maseefa "kayi sauri tunda mun karaso plz .

"Dan Allah karki dameni da shirmenki din banza da wofi ,ba gashi kokarin danake yi ba kenan, yayi maganar tare da sanya hancin motarsa Cikin harabar hospital.

matar tace "Ni dai ban nemi jin wani dogon turanci daga gareka ba, ka..ka daidaita tsayuwar motar kawai ,gama daidai tsayuwar motar keda wuya ta bud'e murfin motar da sauri tana ihun kiran"doctor!nurse! "Dan Allah malam taimaka ka fito ka d'aukar min yarinyar nan..
dareban yace " Dan Allah gani nan fitowa karki dameni," ko ni ne ubanta?
yayinda ita kuma tashiga ihun kiran doctor da nurse jikinta na wani irin kirma ta zame Kan yarinyar dake kwance saman cinyarta, ta kwantar a kujera tasoma yunkurin fitowa tana kiran" hhh uhmm tana 'barin jikin fitowa da yarinyar ,a daidai lokacin da shima direban ya fito daga mazauninsa har ya bud'e bayan motar yace " kinga Dan matsa na taimaka miki ,da sauri jikinta na kyarma tabar jikin motar tayi baya .

Direban yashiga kokarin fito da yarinyar yana kai hannunsa jikin yarinyar yaji yanayinnta ya sauya tayi nauyi sosai,yayi saurin cewa " ai sai matso ki d'auketa kin wani tsaya kamar wata dolowa kina kallon mutane .
jikinta na rawa ta matso tasoma kokarin janyo hannayen yarinyar amman ta k'asa sai kyarma take tana kuka. "ki fito daita man kin wani tsaya kina rawar jiki ko ba yarki bace?

Cikin rawar murya tace "zan d'auketa tana sake kai hannuta amman tsoron ganin yanayin yarinyar yasa ta kasa d'aukarta, ta matsa baya da sauri "shikenan abinda nake gudu ne ke shirin faruwa dani.

direban ya dubeta a matukar firgice "naga alamun kina son sakani cikin tashin hankali ba?

" ,ki d'auketa daga cikin motata ki sallameni na kara gaba neman abincina, " kayi hakuri abinda nake kokarin yi kenan sai dai bazan iya d'aukarta ba tayi nauyi sosai .

Wani tunani direban yayi kar fa ya tsaya sanya yarinyar tazo ta mace masa acikin mota yashiga uku,wannan tunanin dayayi yasa ya tattara gbdy karfinsa yasoma janyo hannunwan yarinyar ya fito da rabin gangar jikinta yayin kafafunta ke cikin motar "oya kamata mu fito daita .

fito da yarinyar keda wuya, ta dinga yin wasu abubuwa tamkar macijiya yayinda matar nan sai ihu take tana kuka tana kiran sunan yarinyar "NASREEN dan Allah ki rufa min asiri karki mutu "domin idan wani abu yasameki madam bazata barni a raye ba, kuka take sosai tana biye da bayan direban "look at how she curling like a snake may God have mercy inji cewar direban .

gudu gudu sauri sauri suka iso bakin kofar shiga cikin reception " kin damu mutane da ihu ki matso ki bude min kofa mana .

da sauri takaraso jikin kofar ta bud'e masa kofar suka shiga nurse naganinsu suka yi hanzarin karasowa garesu ,tare da amsar NASREEN a hannun direba, kai tsaye d'akin babban likita suka nufa daita ,suka kwantar daita akan gadon likita dake zaune yana dudduba wasu file dake gabansa,likita ya mike da sauri yana gyara zaman farin medical glass dinsa, ya isa gadon da NASREEN take kwance yasoma kokarin bata taimakon gaugauwa .

********

Tsaye take cike da kamewa da natsuwa a tsakiyar maza ,wanda a kalla zasu kai guda goma zagaye daita sai mata guda biyar ,wad'an da ke karkashin ikonta , acikin conference room. kowanensu sanye yake cikin shigar black suit , yayinda ita kuma take sanye cikin wata had'ad'd'iyar doguwar rigar abaya baka har kasa ,wace akayiwa adon da green stone ajikinta tun daga zaren har duwasu, tayi rolling kanta da mayafin abayar wanda ya fidda ainihin sahihin Shep din fuskarta da sirrin kyawunta.
black hill Shoe ne sanye a kafafunta ,yayinda tsintsiyar hannuta yake d'aure da farin agogon diamond me matukar kyau da d'aukar hankali.
wani irin sihirtaccen kamshi na musamman jikinta ke fitarwa ,wanda ke sanya duk wanda ya shaki kamshin yaji yasamu wata natsuwar ta daban a zuciyarsa.

"me'ad kenan diya ga alhaji idris takai dake karkashin hukumar jahar kano ,alhaji idris takai hamshakin me kudi ne wanda ya rike mukamai daban daban agidan custom har zuwa yanzu dayake matsayin controller k'asa gabadaya .

me'ad kyakkyawa ce ajikin farko ta bugawa ajarida ,mace ce first class me tsananin kyau da kyauwun sura wace ta tattara duk wani abinda cikakken d'a nmj me jini ajika yake bukata daga diya mace.

"fara ce sol ko tabo daya babu ajikinta sannan doguwa ce sosai mara kiba, sai dai takasance irin matan nan ne masu shape din cokacola, wato daga samanta tana da cikar halitta qirji na dukiyar fulanin, yayinda cikinta ke shafe tamkar bata sakawa cikinta komai, daga k'asanta kad'an tana da wani irin Hip's na ban mamaki me tsayawa arai ,tana da doguwar fuska da hanci kamar yadda tsarin jikinta yake, sannan tana da karamin baki wanda ke zagaye pinky lip's , itace ta tattara dukkanin wani kyawun mahaifiyarta hjy Khadija da mahaifinta alhaji idris .

me'ad takasance shiru shiru ce ,kasancewar bata fiyye son magana ba, wanda hakan yasa mutane suke mata kallon me shegen girman kan tsiya da miskila ,sai dai fa idan kashiga track dinta zata zage ta shuka maka rashin mutunci ,sam bata d'aukar wulakacin ko rainin hankali, amman idan bakashiga lamarinta ba, zakuyi shekara dubu babu daita babu ruwanta da lamarin mutu .

babu cikakken d'a namji da zai kalli surar me'ad yace bai ga mace me cikar halitta ba, sai dai ya fad'i son ranshi. manage ce a M I K company's dake cikin ikoyi hotel.

ahankali take jujjuya jikinta tana magana a tsanake cikin harshen tsadadden turancinta " am taking about our new product ," all of you are a ware of the reason ,why we call this crucial and important meeting ,we are here to discuss about the company's new product in this market , the importance of this meeting is the product must to do well in the market ,not just do well.

" The product must be the very best in the market "ina fatan gabadayanku kun fahimci inda zancena ya dosa?

suka kad'a kai ala'mun suna sauraronta sannan tacigaba da magana ahankali.
" so the new toothpaste must be the very best in the market so that ....
kiran wayan daya daga cikin members din dake zagaye daita ne ,ya d'auki kara sauti wanda ya karad'e ilahirin conference room din, har ya katse karshen maganar me'ad wace tayi tsaye sororo tana dubansu daya bayan daya, cike da mamaki da matsanancin 'bacin rai kafin ahankali idanunta ya tsaya cak akan wanda wayarsa ke kara ,tacigaba da kallonsa tamkar zata cinyesa tsabar bacin rai, domin abinda tafi tsana kenan arayuwarta tana magana me mahimmanci ana damunta da hayaniya mara amfani .

A matukar tsorace shima ma'aruf yake dubanta kirjinsa na wani irin lugud'en baguwa da karfi, ya kai hannu ya shafa sumar Kansa sannan ya dane fargabansa yasoma kokarin d'aukar wayar ya manna a kunnensa batare da ya sake duban inda take tsaye ba yasoma magana "kana jina ina meeting karka damu kaje cikin dakin ka duba cikin wardrobe dina idan kagani ka d'auka kawai .

sake ware seyx eye's dinta tayi dan tabbatarwa kanta abinda ke faruwa "mafarki ne ko gaske ?ma'aruf wayar ya d'auka alhalin tana tsaye agabansa.
karewar d'aukar wayar ma ,har sautin muryarsa sun soma shiga cikin kunnuwanta suna mata kuwa , cigaba tayi da kallonsa cike da matsanancin mamaki da tashin hankali, "tabbas ma'aruf yana wasa daita tare da wasa da aikinsa , a daidai wannan lokacin, zuciyarta ce taitamata mata sake sake had'e da tsantsar tsanarsa acikin zuciyarta .

"wannan bashi ne karo na farko dayake mata haka ba, a duk sanda suke taro makamancin haka, akoda yaushe shine mutun na farko dake kokarin break din rule dinta ....
iya hassala tayi domin kuwa zuciyarta har tasoma tafarfasa akan sa, yayinda har lokacin ta kasa d'auke idanunta akansa ,wayarsa yake hankali kwance cike da izza da nuna ita din bakowa bace agabansa ." sai dai duk wannan abinda yake zuciyarsa cike take taf da matsanancin tsoron shugaban tasa......

mmn sudais ce
[11/3, 8:24 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 6 to 10

....."mr ma'aruf takira sunansa cikin zakakkiyar muryarta me dad'in sauraro da kashe jiki ,"can i please just have that phone of you's ......?

cike da jin shi ma wani shegen kansa ne "yace am really sorry ma ,tare da meida wayar cikin aljihun wandonsa ya sunkuyar da kanshi kasa yana duban yatsun kafafunsa .

"can you give me your phone now? ta sake yin maganar a fusace tana tsare gira.

"i said am sorry ya fad'a cike da izza ,runtse idanunta tayi ahankali sautin muryarta ta fito atsawa ce "can you give me ur phone?

ransa a had'e ya ciro wayar daga cikin aljihun wandonsa ya mike mata ta amsa tare da jan dogon tsaki ta d'aura wayar kan table tacigaba da maganar "now this is something I wil like to tell everybody.

"if i smash the phone on the floor because of this stupidty...it's the highest level disrespect for your boss to be talking at a meeting..

"idan ma ba rashin hankali da tunani ba ," ta yaya shugabanku na tsaye tana magana me mahimmanci zaku dinga shigowa da waya, har wani jaki daga cikinku wanda yake ganin shi tsagera ne zai dinga receive Call "let me tell you all ,for the very last time.

"me nace...?

gabadaya suka had'a baki gurin cewa for the very last time ma, amman banda ma'aruf da zuciyarsa ta kusan bugawa tsabar takaicinta.

"a tsawa tace "ina son ku sake had'a baki, ku maimaita abinda nace har kai mrs ma'aruf for the very last time .....
take suka sake maimaitawa ,tayi taku daya zuws biyu " let it be the very.. last time, that i wil cal a metting or you come to the conference room da zaku shigo da wayoyinku kai bama ring din wayoyinku ba ,hatta vibrating banaso jin , kai gbdy ma "i don't want to see your phones okay ..

"yes ma.

ta fuskanci ma'aruf sosai "mr ma'aruf this is ur last warning dakazo min da waya meeting .....

sannan ahankali ta fuskanci gabadayansu tace "akwai millions of people out there looking for jobs.. "basu samu ba ,masu kwalkwaluwa sannan suka san yadda zasu sarrafa tunaninsu da kwalkwaluwarsu acikin kasar nan ba irinku dakikai ba, ku kun samu amman kuke iskanci , abinda yakamata ku godewa Allah dayasa kuka kasance cikin wad'an da ke aiki acikn company nan.

ahankali ta sake juyowa matukar fusace gefen da ma'aruf ke zaune sunkuye da kansa "mr ma'aruf..

ya d'ago da kyar yana amsawa da "yes ma.

"ina gargadinka da wannan iskancin naka ya zama karonka na farko da karshe okay "ina nufin karonka na karshe you dare bring ur stupid phone to my meeting, " idan hkan takasance bazan koreka daga cikin meeting din ba, sai bayan nasa an tozarta min kai ,sannan nayi ratsaratsa da wannan banzar wayartaka sannan zanyi sack dinka daga aiki alright? takasara maganar a matukar hasale ."amshi banzar wayarka daga hanuna ta miko masa wayar tana me lumshe

idanunta cike da 'bacin rai ,yasa hannunsa ya kar'ba wayar tare da furta "thank you ma a dakile .

bata tsaya sauraresa ba tacigaba da magana cike da matsanancin bacin rai

"yauwa mukoma kan abu me mahimmanci da muke duscusing before..kafin wannan stupid din ya katse mana hanzari " muna magana ne akan sabbin product dinmu na toothpaste da zasu shiga kasuwa acikin tsakankanin wannan lokacin "atakaice dai duk nasan kusan yadda muke son kasuwancinmu yakasance da yadda contains din fluoride dinmu zasu zo hannunmu ko ba haka ba?

suka had'a baki gurin cewa "haka ne ma.

"there is menthoi in it
"we are hering very good report on that as wel dan haka kowanenku yaje yayi nazari akan tautaunawarmu domin yana da matukar mahimmanci....

can hospital kuwa, gudu gudu sauri sauri teacher chioma take a dogon korido din hospitar , kunnenta mane da waya ,cike da tashin hankali ta cire wayar a kunneta tana dubawa tagani ko kiran ya tsinke , ganin datayi har lokacin Number na tafiya yasa ta sake meida wayar kunnenta biyu biyu ta dinga taka matattakalar benen "wayyo Allah, Allah kasa ta d'auki wayar har ta karasa sauka akan step din kokarin neman layin mahaifiyar NASREEN take ...

bangaren me'ad kuwa tana nan tsaye tana cigaba da dogon bayaninta akan yadda take son company's dinsu zai samu cigaba takowani bangare "dan haka we need to........ karar sautin waya ne ya sake katseta ,kame ta kyam atsaye tana me runtse idanunta a matukar fusace tace "wayar wani tacencen d'an iskan ne ki ring kuma?
"waye wannan tantiri idiot din?
"waye wannan dolon daya bari wayarsa tayi ringing alhalin nace ko vibrating bana bukatar ji, take gabadayansu suka shiga duduba wayoyinsu, yayinda still wayar ke sake kara .
mr tahir wanda tun soma maganarta ya tsura mata idanunsa kawai yana kallon tare da cizan lip's dinsa yana ji aranshi dakace yana da iko da tuni ya tashi ya yaryarfa mata maruka tsabar haushinta dayake ji,a duniya babu macen dayake jin ya tsana kamarta ..

"wani jakin mara jin magana da disobey ne yabari tsinanniyar culcuting dinsa ke damun kwalkwaluwar mutane..takarasa mgnr a fusace ?

daya daga cikinsu ne yace "madam ,ai wayarki ce ke kara.

gabanta yabada wani irin rasssssss tayi tsurutsuru da kyakkyawan idanunta tana kallonsu daya bayan daya ,zuciyarta na wani irin hamaukacin beting , yayinda har lokacin idanun tahir ke kanta yana kallonta yana ta'be baki ,wani irin abu taji tun daga tsakiyar kanta yana yawo daita har zuwa sansar jikinta tamkar an mata wanka da ruwan sanyi, kunya ce ko kuma nadama ce

ta rufeta alokaci daya ita dai batasani ba cike da matsanancin mamaki ta tsurawa mutumin dayace wayarta ke ringa idanunta  d'auke da karin bayani "yes it ur phone ma tahir ya sake maimaita mata ,ta juya bayanta ahankali inda ta'ajiye wayar tana duban  screen din wayar jikinta na rawa rawa ,tabbas wayar ce ke cigaba da kara "kina iya d'auka madam watakilla kiran gaugauwa ne inji cewar mataimakinta...

tsawon minti goma tana duban screen din wayar batare da tayi kokarin d'auka ba , ta juyo jikinta a sanyaye tana fuskantarsu gabanta na cigaba da bugawa, tacigaba da mgn"muna magana ne akan fluoride da mentho  sai kuma abu na gaba , yadda zamu  shigar dasu  kasuwa da wasu bangarori acikin kasashen duniya ...
takasa cigaba da mgn"am..uhm ..am da kuma  wanda daman a kasuwa ta kasa karasa maganar saboda yadda jikinta da bakinta ke rawa ...

yayinda teacher chioma tacigaba da kiran wayarta babu kaukautawa  har takaroso harabar hospital din tashiga zariya " wayyo ni kam nashiga ukuna ta cire wayar a kunneta tana sake dealing "ina wannan matar ta ajiye wayar danaketa kira bata d'auka ba?
ta sake cire wayar a kunneta tana dubawa "ki d'auki wayar nan dan Allah ,still wayar ring take amman saboda tsautsauran ra!ayi irin na me'ad taki d'aukar wayar sai ma neman izini datayi agurinsu "one minti .. ta juyo inda wayar take still dai chioma ce take kiranta acikin zuciyarta take adduar Allah yasa wannan kiran ya zama kiran Ify, dan bata ta'ba kiranta irin haka ba .

tahir ne ya gyara zamansa tare shafa kasunbarsa yana kwa'be baki da fuskarsa yace "ranki ya dade ki d'auka mana killa zai zama kiran ne me mahimmanci.. tayi masa banza sai dai gabadaya ilahirin jikinta ya sake d'aukar rawa, ta d'auki wayar tana dubawa sannan ta mikawa daya daga cikinsu "can you take it to my office  and just put it there for me? "idan kuma kagama karka dawo akan lokaci har mugaba gabatar da meeting  kafin ka dawo, ya karbi wayar ya nufi hanyar fita ita kuma tacigaba da magana har yanzu dai muna magana ne akan flavor.. da kuma am uhmm   wasu daga cikin flavor Wanda zamuyi amfani dashi acikin product ..

chioma takalli gabas da yamma tana kuka tare da girgiza kai"bata d'auka ba  shikenan tawa tasameni ina cikin tashin hankali ta kwasa da gudu zata sake komawa cikin reception, direban da tun fitowar yake watsa mata harara cike da da jin haushin 'bata masa lokaci datayi ya biyo bayanta da sauri yana kiranta "ke ke ina kuma zaki?
" dawo nan ina kudina dakike kokarin wucewa?

"ga wawa kinsamu ko, sai wani zariya kike awa jigida "kaga kayi hakuri mlm yarinyar da muka kawo har yanzu batasamu lafiya ba tukun  mahaifiyarta naketa kira wayarta tayi ring ring amman bata d'auka ba dan Allah ka kwantar da hankalinka kaji zan baka kudinka.

"oho sai yanxu na fuskance inda kika dosa saboda ni wawa ne , nacigaba da tsayuwa agurin nan akan matsalarki har sanda wannan yarinyar me kama da macijiya zata warke kafin na tafi gidana ko"dan Allah malama ni bani kudina na kama gabana"kasan abinda zai faru yanxu ?
" dan Allah kabari naje nasamu doctor nagaya masa zai biyaka kudinka  .

ta juya zata wuce yasa hannuwansa duka ya janyota "na fahimta .."na fahimce maganarki amman miko wayarki nan "ka kwantar da hankalinka zan sa abiyaka kudinka.

direba yace  "ina wallahi bazan yarda ba ni dai miko min wayarki kawai najita a hanuna  idan kin koma gurin doctor idan yabaki kudin alabashi sai ki dawo ki karbi wayarki. ya kwace wayar ya koma jikin motar ya jingina jikinsa zaman jira , ita kuma ta juya da sauri tana magana "shikenan naji ai ba laifinka bane  kwata kwata baka da laifi ,laifin wancan shashar uwar tatace dataki daukar wayar ..

shi kuwa direba yacigaba  da tsayuwa agurin har ya daina hangota yana cike da mamaki "a'a wasu irin mugayen mutane ne wad'an nan mutane da suka haifi yarinyar kamar macijiya "ita kuma wannan stupid din tsamaninta nayita tsayuwa ne akan macijiyar nan har sai tasamu lafiya ko me ? yayiwa kansa tmbyr yana kwa'be baki.

a daidai corido chioma suka had'u da doctor wanda kad'an yarage bataci karo da dashi ba tayi saurin ja da baya tana kuka tace "doctor.

doctor yace "am ya'akayi ne yana duba agogon dake daure a tsintsiyar hannunsa "kinsamu mahaifiyarta a waya kuwa?

"uhmmmmm  ita naje kira a kasa  amman wayarta tayi ring sau ba adadi bata d'auka ba .

"ok dad dinta fa? inj cewar likita.

"mom dinta muke da kusanci banida number dad dinta.

"okay I will call thorough to her father  duk abinda ake ciki  i will let you know.

"nagode doctor.

ya wuce ita kuma takarasa zuwa d'akin da'aka kwantar da NASREEN .

********

mahaifin NASREEN zaune a makeken office din  me gidansa suna tautaunawa akan lamaran daya shafi yau da kullun akan  aikinsu. me gidansa sir malik yace "wad'an abubuwan suna da matukar mahimmaci  amman abinda nake son kamin shine ka meida hankalinka sosai akan lamarin aikinka  sannan ka sake meida himma ta haka ne zaka samu cigaban dakake bukata arayuwa.

"nagode sosai sir duk abinda ka fad'a  na fahimata ,zanyi kamar yadda kace zan meida hankalina kuma Inshaallahu zaka sameni kamar yadda kake so ,ni dai burina ka taimakeni

nasamu wannan karin girman.

sir malik yace "karka damu fu'ad ,kaima ai mutum ne me kwazo sosai kuma gashi kana da matukar mutunci da girma acikin idanuna dan hk baxa kata'ba neman alfarma agurona na hanaka ba, ka kwantar da hankalinka i wil know what i am supposed to do for you.

"akwai abubuwa na musamman danake son namaka bayan karin girma ni dai burina ka kwantar da hankalinka zuwa wani lokaci.. kirane yashigo wayarsa yayi sauri ciro wayarsa cikin aljihun wandonsa yana dubawa tare da cewa "excuse me sir zan daga kira.

"karka damu fu'ad ka amsa wayarka kawai

"hello .

daga can bangaren doctor " yace hello kana yasoma yiwa fu'ad bayani abinda ke faruwa da yarinyarsa, a matukar razane fu'ad yace "what?

"yarinta daga school meyasameta?

yayi masa tmbyr ajere cike da matsanancin tashin hankali "kaga ganin nan zuwa yanzu ya katse kiran me gidansa dake dubansa tun fara wayarsa yace"meke faruwa fu'ad ?

"kira nasamu daga hospitar wai anyi rushed din yarinyarta daga school zuwa hostopital "ok maza maza ka tashi kaje yanxu "ya mike tsaye cike da girmanawa yana me d'an rankwafawa "nagode sir.

*******

bayan sun kammala da meeting ,tahir da ma'aruf har ma da matakin me'ad suna tsaye abakin get din company kowanensu fuskarsa a dagule ala'mun 'bacin rai tahir ne yasoma magana cike da matsanancin 'bacin "wai ku meyasa wani lokacin kuke behave wani iri haka ?
" koda yaushe Ina kokarin nusar daku amman kamar masu kwalkwaluwar kifi bakwa fahimta, kwata kwata bakwa d'aukar shawarar da nake baku da mahimmanci akan yar rainin hankali matar nan ,abinda nake fad'a maku kenan kullun amman bakwaji
muna cikin meeting wayarka tayi kara ka d'auka kayi magana kuma ,taganka lokacin daka d'auki wayar , fine tarigada takamaka red-handed sai kuma tace maka kabata wayarka kuma ka mika mata saboda kai dolo ne "common woman.. common woman for that matter dayake kaima dakikin ne kmr yadda tace shine kabata wayar bayan tagama wulakantaka sai kabata wallahi idan nine bazan bata ba komai za'ayi sai dai tayi amman wallahi kaji na rantse bazan bayar ba "abin mamaki ma sai lokacin da kake mika Mata wayar kamar wani dolo "wai so.. sorry ma..." a common woman for that matter tahir yakarasa mgnr cike da matsanancin fushi yana furzar da iska ta bakinsa ..

ma'aruf yace" wani irin banzar magana kenan kake kokarin fad'a min hka ,da yake maka dadi abakinka?

"misali lokacin da madam ta
umarceni nabata wayar ban bata ba mekake tunanin zai faru dani?

"babu wani abinda zai faru da kai malam dan nasan babu abinda zata iya yi..

"tahir babu abinda zai faru kace ? inji cewar ma'aruf.

"wallahi bazata iya aikata komai ba duk cika baki ne kawai irin na mata.

"really? inji cewar ma'aruf

tahir yace "yes.

"tahir kace babu abinda zai faru ko,? "amman bari nagaya maka wata mgn dabakasani ba,shekara da shekaru ina zaune zaman banza batare da nasamu aiki yi ba ni kadai nasan halin tashin hankali dana ciki a dalilin rashin samun aikin yi dakake kokarin ganin na aikata abinda zai sa wannan bazar matar takoreni a aiki .

tahir yace " sai akayi idan takoreka ?

"baka da hankali na zauna tsawon lokacin ina zaman jobless daga baya naxo nasamu aiki sai nayi focub akan aikina it's possible "nasan ka fahimci inda na dosa "yadda kake magana kamar wani d'an me arkizi alhalin ubanka ba kowa bane a kasar nan, bai ma da aikin a hanunsa ballanatana kace "a'a oo bari kayi masa magana yasamammin aikin Akarkashinsa dakake kokarin zagina , haka kawai na kwabsawa kaina a koreni abanza bazai yiwu ba wallahi gara dana bata na huta .

mataimakin me'ad ne ya kwashe da wata mahaukaciyar dry har da buga kafasar daya a kasa .

ma'aruf ya dube tahir yace "karamim dan iska ina fatan ka gamsu da maganata?

tahir had'e rai tare da cewa " jima mana Karka nemi raina min hankali ta hanyar zagar min uba "babana yanabawa mutane maching din haya domin su dinga yi aiki suna kawo masa deliver, idan kabar aikin nan ,zan masa magana ya siya maka kaje katayin aikinka cikin kwanciyar hankali babu tsamgwama balle wulakaci...i wil ask my dad to buy you a motorcycle on an installment plan yakarasa mgnr yana hararar, ma'aruf ya
had'e rai kamar zai fashe , zuciya taxo masa iya wuya mudarsir ya sake kwashewa da wata dry yana dafa kafad'ar ma'aruf "kayi hakuri ma'aruf nasan abinda tahir ya fad'a bai kai har cikin zuciyarsa ba ,kar kabari wannan maganar ta sake dagula maka lisafi ,how could his dad give you a job?

"wani irin magana kake fada kenan mudansir? inji cewar tahir
"wallahi ni har cikin zuciyata na fad'a masa haka, "ya daina daukar wulakacin daga wannan matar ,yasa a zuciyarsa ko babu taimakonta zai yi rayuwa .

mudarsir yace "kai kai malam dakata "babanka na bada aiki me daraja meyasa kaxo kake aiki a karkashinta?

"amman ku natsu kuji abinda zance muku yanzu duk wannan rawar jikin da kuke da zafin rai nifa ban d'aukar lamarin matar da girma ba ballanatana har ya tsaya min arai daga baya yaxo yana damuna "ba dai tamaka take da matsayinta ba,wanda yasa take jujjuya mu tare da gayamana duk abinda yazo bakinta ba?
"kubarta tayi iskancinta son ranta tagama mu kuma sai musan ta inda zamu bullo mata "zamu 'bata mata rayuwa ta yadda zuwa gurin aikin ma zai gagareta "listen friend inji cewar tahir "me ya faru ne haka?
" tun sanina da kai mudarsir banta'bajin ka fad'i maganar arziki ba ko shirya planing yadda mutun zaiyi arziki a duniya ba, sai dai yadda rayuwar mutan zai tagayyara ,yadda mutun zai daidaice da lalacewa ko raba mutun da rayuwarsa da makancinsu kawai ka iya.

"yanzu dai mekake tunani zamuyi yanzu akan wannan matsalar?

mudasir yace "inada master akan makarci ba "ba dai takamarta rike biro ba? nasan abinda zanyi akan wannan matsalar ta yadda aikin ma zai bar hannunta.

"ma'aruf yace wannan tsarin yayi sosai gsky ni zanbaka had'in kai sosai duk abinda zakayi kayi ni zanbaka hadin kai ta 💯ta yadda zamu kai ga ci .

"ku tsaya kubani minti goma ina da abinda zan fad'a "if it eventually happen Is, i might be asked replace her post saboda shine abinda nafi bukata.. kar daga baya, bayan komai ya kankama kuzo kuna min bakinckin kar abani ,ni dai idan za'a bani matsayinta nasa hannuna har ma da jikina gbdy gurin aiwatar da abinda za'a yi mata sai dai ni dai bazan biku inda za'a yi aikin ba duk abinda ake ciki kwa sanar min inji cewar tahir yana dryr mugunta, nan dai suka maganar akan mudasir da ma'aruf ne zasu je inda za'a raba me'ad da aikinta ....

********
kallo daya zakayi masa ka tabbatar da cewa ba cikin natsuwa da walwala da kwanciyar hankali yake ba, tunda ya yashigo asibitin bayan kiran daya samu na gaugauwa daga doctor.

idanuwansa kawai ya tsurawa tilon diyarsa yana kallonta kirjinsa na tsananta bugawa da karfi "me ke shirin samun diyarsa dhaka ,da har ta fice cikin haiyacinta bata gane kowa?

"yana son yasan kan matsalar yarinyarsa da dalilin kamuwa da wannan ciwon domin yasan ta inda zai shawo kan abun. "babban abinda ya d'aga masa hankali shine bai wuce har zuwa

wannan lokacin    me'ada batakaraso hospilata din ba, ya jima zaune akan dayan gadon yana fuskarta yadda diyarsa ke kwance iskar oxygen na taimakawa numfashinta, yaji an banko kofar da karfi an shigo, a sukwane ya dago tsumammun idanunsa ya watsa mata ita kuwa ko kallon inda yake zaune batayi ba, takarasa gadon da diyarta ke kwance .....

mmn sudais ce💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 11 to 15

..."wayyohlly Allah yarinyata  ! wayyo  tillon diyata  farincikina " me yasa me ki kuma?

"NASREEN dina ki bud'e idanukin ga momy'nki  tazo, dan Allah karki min haka "what's it's?
" please NASREEN talk to mummy .

"mummy is here now, please open ur eyes and look at me ..  gabadaya ta rud'e had'e da gigicewa ,cikin haka wata nurse tashigo d'akin sanye da kayan aikinsu na likitoci takaraso bakin gadon ta tsaya tana duba yanayin lafiyar yarinyar.

"madam please don't disturb her  she need rest  .
tsam me'ad ta mike tsaye ,jiki a sanyaye tana duban inda fu'ad ke zaune yana dubanta  , tasoma takowa ahankali ta iso har in dayake, "honey what did  doctor say?

shi dai fu'ad  zaune  kawai yake a gurin tare da tsura mata tsumammun idanunsa yana kallonta cike da matsanancin takaicinta acikin zuciyarsa, har ta iso gareshi ta samu guri kusa dashi ta zauna tamkar kazar da kwai ya fashewa a ciki tana sake tambayarsa abinda likita yace.

ya kalleta a kaskance a wulakance sannan yace "what did doctor say fa kike tambayata ?

ta kad'a masa kai tana tsareshi da kyawawan idanunta batare da tace masa komai ba.

a matukar harzuke yace "ke ..ina kike tun safe da'ake ta faman kiranki a waya baki d'auka ba?

tayi sororo tana dubansa kirjinta na wani irin mahaukacin bugu..

"ko zaki ce ba'a kira wayarki bane da kike kallona kmr wace akayiwa karya ?

"wai ke wace irin uwar banza ce ke , da bakinsa ciwon kanki dana yarinyarki ba?

"nace wace irin uwar banza ce ke..?

ta ware idanunta a waje saboda jin furucinsa gareta, dan bata taba jin yayi mata irin haka ba a tun iya zamasu tare . duk da furucinsa yayi mugun ta'ba zuciyarta amman haka ta danne ta rarrashi zuciyata domin batason su nuna hali agaban nurse gashi yarinyarsu na bukatar natsuwa , ahankali muryarta gurin cewa.

"please honey don't say that to me ,you should know there must be a reason for me not to have picked my calls ,i was in a meeting ..

"meeting .....ya fad'i hkn a fusace kana yashiga girgiza kansa cike da matsanancin takaicinta, sannan yacigaba "so the meeting was important that you couldn't see the call from ur daughter's school and call them back.

"banzar kwalkwaluwarki bata gaya miki abinda ya dace kiyi ba ,bayan kin ga kira daga teacher din yarinyarki, "meyasa bakiyi tunanin ki kira wayar daga baya ba kiji meye matsalar , alhalin kinsa yarinyarmu na tare da lalura wanda at anytime za'a iya kiranmu a waya ?

zaune tayi aguri daya tamkar wace aka dasa tsabar tashin hankali datake ciki.

"wallahi kwata kwata me'ad baki da hankali ballantana abinda ake cewa t...

a matukar tsawa ce ta daga masa hannu ta hanyar tadakar dashi "please stop stop doing that fu'ad "don't dare to do that to me "me kake nufi da nuna kanka da kakeyi kana min magana irin haka kmr kai da wata yarinyar cikinka duk ma me akayi daka d'auki zafi hk?

"gaskiya bana son irin haka kad'ai na min domin yana maseefar 'bata min rai har naji brain dina ya fara craking ka daina dan bana bukata ...

"even if you want to chastise me, not not in the presence of a woman ..

"you are a disappointment woman to me me'ad, "wallahi nayi danasani aurenki arayuwata kwata kwata baki cancaci zama uwa arayuwarki.....

rai 'bace nurse tak'ara gyarawa NASREEN kwanciya tare da lullu'be mata rabin jikinta ,sannan tasoma kokarin karasowa inda suke zaune "madam wai me ya faru haka kuke hayaniya.. ..?

"ihunku na dustub  din yarinyar nan ,gsky bama bukatar yadda kuke kokarin hana yarinyar samun natsuwar datake bukata,dan haka kuje doctor nasan ganinku ...

me'ad ta juyo ta kalli nurse tana yatsin fuska sannan tace "kiyi hkr  ba yin kaina bane tunzira zuciyata akayi.
ta juyo ahankali gefen da fuad yake zaune "honey kaje doctor nasan ganinka..

bud'e bakinsa yayi cike da matsanancin mamakinta  km at the same time yana dubanta..

"ya ka bud'e baki kana kallona ko bakaji abinda nurse ta fad'a  mana bane cewar doctor nasan ganinka..

"what ?

"idan ni naje gurin doctor ke fa ,zaman me zakiyi  ?

a matukar tsorace itama ta bud'e baki tana dubansa domin bata tsamacin jin haka daga garesa ba..

"i have been here since morning you go and see the doctor ...

"honey what do you mean by you go.. you go ?
tayi mgnr a fusace tana zabga masa uwar harara,
"  yanzu idan muje gurin doctor yace za'a siyawa yarinyarmu magani ni kake expecting zanje ko me   ?
"da kake wani cewa you go , kai   zaman me zakayi idan ni naje?
",karka manta wannan bangaren hakinka ne  tunda NASREEN ba shegiya bace kaine kayi  silar zuwanta duniya..

"can you imagine  what you are saying?

"kai kai wallahi kwata kwata ba laifinki bane.. laifina ne da banzabawa yarinyata uwa ta Gari abin alfaharinah va, jifa abinda yake fitowa daga bakinki.. "ke yanzu baki ji kunyar abinda kike fad'a min ba?

"dan Allah dan annabi ya issheni hk ... kacika min kunne da maganganunka marasa dadi i think bani kad'ai na haifi NASREEN  ba tunda karigada karigani xuwa ,karigani kenan ..

Ya tsurawa karamin bakinta idanunsa yana kallonta cike da matsanancin takaicinta Yana girgiza kai..

nurse dake tsaye tazama tamkar picture agabansu tana dubansu  ta d'an waiga taga har lokacin NASREEN bacci take, ta juyo ta fuskancesu sosai kana tace "kunga ku daina jayayya akan

wannan matsalar  gabadayanku doctor yace yana son gani dan kuje office din doctor yana jiranku.

ransu a'bace suka mike atare  batare da kowanensu ya dubi d'an uwansa ba, domin kuwa cike suke da  tsantsar jin haushin juna ,ita me'ad najin haushin fa'ud akan insult dinta dayayi agaban nurse ,yayinda shima zuciyarsa ke tattare da bakinciki abinda tayi masa na yana fad'a tana fad'a kuma agaban nurse, bugu da kari rasa tilon diyarsa dayaso yi  adalilin sakacinta na  rashin d'aukar wayarta," yanzu da wani abu yasamu yarinyar su "me zatace masa?

"yasara wace irin mata yake  aure data fi bawa aikinta mahimmanci akan diyar cikinta dashi karon kanshi, a tun sanda ya aureta har zuwa  lokacin data haifar masa NASREEN  bai da kwamciyar hankali, kasancewar aikinta data fifita akansu ,yayinda su kuma suke matukar bukace da kulawarta ,a matukar fusace ta suri hand bag dinta tayi hanyar waje  tabarshi tsaye yana sake  duban gadon da NASREEN dinsa ke kwance tana fidda numfashi ahankali hawaye na bin gefen idanunta, ahankali ya karasa bakin gadon yana cigaba da dubanta ya kai hannunsa  ya shafa sumar kanta yana me jin wani irin ajikinsa, yana jin ina ma yana da hali,wallahi  daya cire ciwon ya meida jikinsa domin shi yafi dacewa da wannan ciwon bakaramar yarinyarsa ba.
" yana matukar son NASREEN arayuwarsa baya son bayason abinda zai ta'ba masa lafiyar jikinta ita kad'ai garesa.. ita kad'ai Allah yabashi a tun tsawon shekara goma dayayi aure ,kusan minti goma  ya d'auka  tsaye agurin yana kallonta yana Shafa sumar kanta hawaye na gangarowa ta gefen idanunsa ,ya ciro  hanky  cikin aljihun gaban rigarsa ya goge hawayen sannan ya gyara gashin daya zubo  wanda ke kokarin rufe mata fuska sannan ya fito daga cikin d'akin.

" abinda yabashi mamaki ba wuce ganin me'ad tsaye abakin kofar d'akin tana jiran fitowarsa ba, wanda shi a tsamaninsa ta dad'e da isa office din doctor, dogon tsaki yaje a fusace ya wuceta yana Allah wadai da halinta har ma da mata masu irin halinta.

har suka Isa office din likita tunani yake ta yadda zaiyi da al'amarin me'ad gabadaya  zuciyarsa tasoma tsirewa da halaiyenta  abubuwa dayawa zuciyarsa ke raya masa  akanta....

doctor najin motsin shigowarsu ya d'ago  yana nuna musu gurin zama sannan ya sake meida kansa kan file din NASREEN dake gabansa, ahankali fu'ad yaja daya daga cikin kujerun dake gaban doctor ya zauna yana ware kafafunsa tare da jijiga kafarsa daya, itama  dayar kujerar kusa dashi taja ta zauma  tana cicci magani..

zaune suke gaban doctor  suna jira daga garesa, doctor ya numfasa kana ya sake d'ago idanunsa yana dubansu  daga bisani ya mikawa fu'ad hannu suka gaisa .

doctor yace "ammm ..i salute ur courage for all your effort on your child, Allah yabata lfy yasa muci amfanin yaranmu gabadaya..

ahankali suka had'a baki gurin amsawa da "ameen kana suka ja bakinsu sukayi shiru suna sauraron doctor.

doctor yacigaba mgn "amm thank God NASREEN has been responding better to treatment now, better than before but her condition now is some what critical than before.

me'ad ta zaro idanuwanta waje tare da dafe daidai saitin zuciyarta tana duban doctor "inna lillahi wa inna ilaihi rajiun ," wannan wani irin tashin hankali hk ,ya Allah karkasa nashiga uku akan yarinyar nan .... takarasa mgnr jikinta na wani irin rawa, take kuma hawaye yasoma ciccikowa a idanunta .

fu'ad batare da ya kalli inda me'ad take ba yace "doctor ban fahimci zancenka ba .

doctor yace "no, just calm down okay , it's not as if her condition is that critical but you know she's a sickle cell patient ,there for, she need a lot of attention.. wanda nake tunani dole daya daga cikinku zai ajiye aikinsa at least for a mouth domin bawa NASREEN kulawar data dace . atare gabansu yaba wani irin rasssss saboda jin abinda doctor yace...

"saboda zaman daya daga cikinku yana da matukar mahimmanci domin irin magungunan dazamu bata yana bukatar kaida,domin ana bukatar ta dinga shan maganin akan lokaci zuwa lokaci ,and most importantly, she need ur care, love and attention more than before...

" atakaice dai yarinyarku na bukatar kulawarku da duk wani abinda iyaye yakamata suyi domin kwantarwa ya'yansu da hankali, me'ad tayi tsuru tsuru da idanu tana sauraron doctor daki daki tamkar zata shige cikin tunaninsa, yayinda fu'ad yayi shr kawai a tun sanda doctor yasoma bayani kai kawai yake girgizawa tare da had'e hannuwansa guri daya yasanya tafukan hannunwansa ya rufe fuskarsa dashi, shi kad'ai yasan irin rad'ad'in da zuciyarsa take ciki akan wannan matsalar...

fu'ad ya cire hannunwasa yana duban doctor da idanunwasa da suka gama canza kala "doctor idan na fahimci zanceka sosai wani daga cikinmu zai natsar da zuciyarsa ya zauna tare daita ?

doctor yace "haka nake nufi saboda kulawarku is very important agurinta.

"saboda ina yawon samum masu irin lalurarta amman yadda nayi muku bayani haka nake treated a similar case dinta, before wani lokaci sai kuga yaro yasamu lafiya ,ina tunanin wannan tsarin dana kawo muku ,zai samu kar'buwa domin itama ina son tasamu irin wannan kulawar daga gareku ,ina me tabbatar muku matsawar daya daga cikinku zaiyi kokarin bata gudumuwarsa wallahi zakuyi mamakin yadda yarinyarku zata dinga samun saukin ciwon ...

"dan haka atsakaninku sai ku zartar da wanda zai zauna gida tare daita, ka ko ba dan komai ba dan Allah kod'an saboda ni ku taimaki rayuwar tilon diyarku dan Allah you guy's should do this.

murmushin fariciki me'ad tayi tana duban doctor "no no karka damu doctor da wannan matsalar Inshaallahu zamu san abin yi ,ai wannan bazai zama wani abun damuwa ba ,dan tabbas zamuyi yadda kace zamuyi magana da juna idan muje gida..

docto yace" thank you.

shi kam fu'ad shiru yayi yashiga duniyar tunanin yadda abinda Doctor yace, gabadaya ya kasa magana saboda cajin da kwalkwaluwarsa ke yi, yana jin kmr ya zubda hawaye ne akan NASREEN yana matukar tausayawa rayuwar yarinyar ahankali ya juyo ya dubi me'ad dake zaune a gefenshi ,ganin murmushi kwance akan fuskarta, ya d'an sanyaya masa zuciya ,hannusa me'ad ta riko cikin tafin hannuta tana murzawa, da kyar yasamu ya mike tsaye suka fice daga office din likita zuwa d'akin da NASREEN take kwance , tare da sanyata gaba suna dubanta gabadaya ta sake ramewa , ji suke ina ma ciwon ya dawo kansu ta tsira da lafiyata...

daren ranar sam me'ad da fu'ad basu samu damar runtsawa ba ,hatta bacci barawo wannan karon baiyi nasarar d'aukar daya daga cikin iyayen NASREEN ba, tunani kawai suke ta yadda al'amarin zai kasance, "cikinsu waye zai ajiye aikinsa domin bawa yarinyarsu faricikin da kulawar data dace ?

"shi ne zai tallafi rayuwar diyarsu ya zauna agida ko me'ad da rayuwarta ce kawai ,bazata iya bawa aikinta ba, saboda mahinmmacisa gareta? fu'ad ya tambayi kansa yana satar kallon inda take . har kusan asuba fu'ad na zaune rike da hannu NASREEN ya tasata gaba yana kallonta still hannunta daya cikin nasa, yayinda me'ad ke tsaye bisa kafafunta tana kaiwa allah kukanta daman ita macece me yawon ibada, kullun daren duniya bata runtsawa batare da tayi ganawa ta musamman da ubangijnta ba, ita din mace me yawon ibada da kamewa tare da tsayuwar dare ,a duk inda ta tsinci kanta zata tabbatar da ta tsaya bisa kafafunta gurin bautawa Allah, illarta daya saurin d'aukar zafi akan abinda bai kai yakawo ba, da kuma d'aukar aikinta da mahimmanci datayi akan bawa yarinyarta kulawar data dace ..

kwanansu daya aka sallamosu daga hospital suka nufo gida tare da jakar magagunguna ,yinin ranar da suka fito daga hospital me'ad na d'aki tare da NASREEN rungume ajikinta tana shafa sumar kanta tana zance zuci kasancewar week end ce ranar babu aiki "Allah sarki haka hukuncin Allah yake gashi dai daga ita har mahaifinta lafiyarsu kalau basu d'auke da wata lalura sannan su ba ss bane balle as, gabadayansu aa ne , gashi sun haifi sickle cell ..
"ina matukar sonki NASREEN dina ,Allah ka raya min ita,saboda banason rasata arayuwata duk da kasancewarta sickle cell kabarni na rayu daita ,Allah karka jarabeni darashinta " hakika wannan matsalar yancine gab iyaye mata akan yaransu naganin sun kula dasu sosai fiyye da komai hawaye ne ke gangaro mata daga cikin kwarnin idanunta .
ganin baccin NASREEN yayi nisa sosai yasa ahankali ta lalla'ba ta kwantar daita tare da sanya pillow tayi mata makari dashi had'e dayi yi mata kiss a goshinta sannan ahankali tashiga shafa sumar kanta tana jin wani irin tsantsar tausayin yarinyarta me gauraye da kauna mara iyaka, ta lullu'beta da blanket me taushi , sannan ahankali ta sauko daga kan gadon tasanya

takalmanta ta d'auki tire dake ajiye akan bed side Wanda ke d'auke da ruwan databawa NASREEN magani ta sha, bud'e kofar d'akin tayi ta fito, kai tsaye main parlour'n din gidan ta nufa yayinda fu'ad ke zaune akan doguwar kujerar dake zagaye da parlour'n ,sanye cikin jallabiya ash colour kafarsa daya ya lankwasashi karkashin dayar kafarsa, yayinda dayar kafar ke mike system ne agabansa wanda ya d'aurashi akan cinyarsa ,yana dane dane tare da tura sakonnin , tazo ta wuce shi tashige kitchen sanye da wata yar karamar riga iya cinyarta da hula net wanda ya bayyana gashin kanta .

ta ajiye tiren hannunta sannan tasoma
gyaran kitchen tare da goge koina daga karshe ta isa gurun gas tana gogewa tana tunanin wanda zai ajiye aikinsa acikinsu domin bawa yarinyarsu kulawa ,aiki take sai dai zuciyarta na can ga satar kallon fu'ad dake zaune yana aikinsa, saboda farin glass dake tsakanin kitchen dinta da parlour'nta bai hanasu ganin juna ba, duk wanda ke zaune a parlour'n tabbas zai hango wanda ke cikin kitchen, haka zalika wanda ke cikin kitchen zai hangi na parlour, yayinda har wannan lokacin fu'ad na zaune wanda ya mike kafafunsa yacigaba da aikinsa hankali kwance yajiyo sautin muryarta daga cikin kitchen "honey .
batare daya d'ago kansa daga abinda yake yi ba yace "yes love...

"should i serve you food now?

"no just give me 5 minnutes i must finish this project, it's due on Monday....

cak ta saida abinda take yi tare da shiga wani yanayi na bugawar zuciya kana a tsanake ta juyo tana fuskartashi "zakayi sumint dinsa on Monday fa kace?

yace "eh zanyi sumint dinsa ranar monday saboda mahimmancisa .

da auri tasoma kokarin fitowa daga cikin kitchen bakinta bud'e sannan cike da matsanancin mamaki tasoma magana jikinta har rawa yake " honey wace monday kenan kake magana akai?

"Monday jibi mana ya bata amsa, batare daya d'ago ba yacigaba da danne dannesa.

"ta dubesa a kaikaice tana sake mamakin jin abinda ya fad'a tayi kusa dashi sosai ta yadda kowanensu zai iya fuskantar d'an uwansa "meyasa zakace zaka gurin aiki ranar monday ?

"ko ka manta abinda Doctor ya fad'a mana ne ?

"me doctor yace mana ?
yayi mata tambayar yana me dakatar da abinda yake sannan ya d'ago ya fuskanceta .

"haba ya kake kokarin ka manta, akan NASREEN mana.

"eh doctor yace dole cikin ni dake wani ya ajiye aikinsa ya zauna gida tare daita .

"yauwa a she baka manta ba.

fu'ad yace "so what are you talking about?

me'ad ta soma fusata dan haka a zafafe tace "what do you mean by.. that, dole mutun daya zai ajiye aikinsa ya zauna tare daita agida ..

"uhmm wannan kuma ai aikinki ne, ki zauna gida tare daita, ta yaya kike tunanin ni na ajiye aikina na zauna gida?
"this is common sense now it's your duty  a matsayinki na mace" ni me zan zauna nayi a gida?
 yakarasa mgnr ahankali yana kallon cikin kwayar idanunta, gefe daya kuma wani irin bugawa zuciyarsa keyi da sauri sauri .

ahankali ya numfasa kana yace " kiyi tunani sosai me'ad akan wannan lamari kodayake bai zama lallai ki gane, abinda nake nufi ba tunda baki aiki da kwalkwaluwarki ya fad'i hkn yana nuna gefensa kansa..

"no no fu'ad banason irin abinda kake min "and you know I don't like all this can of thing  kasan sarai banason kana min magana kana ta'ba kanka domin kokarin meidani mahaukaciya mara tunani..

ya sake kai hannusa daidai gefen kansa "wannan ai common sense ne ,kema kuma kinsa da haka ,yakamata amatsayinki na mace tunaninki yagaya miki akan kece zaki zauna agida  bani ba .

dakata fu'ad "automatically, its your duty to stay with her .

"for what?

"me kake nufin akan saboda mai?

"okay  tunaninki nabar aikina na zauna agida alhalin ga ki ....

"me kake nufi da bazaka bar aikinka ko me ko me?

"kai kanka kasan kai yafi dacewa ka zauna agida tare da yarinyarmu kasan wannan.

"gsky bakida hankali da tunani wallahi ,kwata kwata tunaninki baya gaya miki gasky da har kike expecting ni yakamata na zauna gida tare da NASREEN alhalin gaki mace kina nan baki mutu ba .

"nasan aikina nane,  ba sai ka gaya min ba, ta hanyar meidani  tamkar mahaukaciya  ,"amman

ni aikina yana da matukar amfani ga rayuwarmu gabadaya, dan hk ko kaki ko ka so you will be the one that wel stay at home with  our daughter......

"wannan ai akinki ne me'ad meyasa kike kokarin meidashi kaina. ?

"i know  but my job is mo..re more important you just can't tell me to what's my du...

sautin  tarin NASREEN ne yakatse mata hanzari ..tarinta  kawai suke jiyowa babu kaukautawa da wani irin sauri fu'ad ya zabura ya mike  tsaye jikinsa na kyarma "kingani ko kinga abinda maseefarki zai haifar ko dan.. ..ai kafin yakarasa fadar abinda yake son fad'i  tarin ya sake yin karfi ai da wani irin mugun sauri tayi hanyar d'akin NASREEN aguje tana ihu kiran sunanta .....

mmn sudais ce💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 16 to 20

.......aguje  suka karasa shiga cikin d'akin, kowannensu na rige rigen isa inda take zaune dafe da kirjinta tana cigaba da tari tamkar ranta zai bar gangar jikinta, da sauri fu'ad ya haye saman gadon ya janyota zuwa jikinsa ya rungumeta yana kiran "sorry baby!!!

yayinda gabadaya ilahirin jikin me'ad ya d'auki rawa  "tarasa me ma zatayi ,sai sambatu take "me kuma ya sameki baby nah ?
"some one should help me plz "wa meye hk ne.. ..?

zagayowa tayi dayan gefen  ta haye gadon tana  maimaita "me yasa meki baby nah ?"dan girman allah ki sausautawa zuciyarmu bazamu iya jure kallonki cikin wannan tashin hankali ba.
"ya ubangijin ka taimakeni kabawa yarinyata lafiya tayi rayuwa kmr sauran yara.

NASREEN tayi tari da karfi tare da cewa "da..dady wa...water..

a matukar  firgice yace  " watare me'ad give me water plz .....

me'ad wace ta sake rikicewa tace uhmmm water ?

"dan Allah malam kije ki kawo min ruwa yanzu yayi maganar a fusace .. "sorry honey, ta duro daga kan gadon ta tsaya sanya takalmanta .

"a fusace yace run now.

" i am runing "im runing !!

ta bud'e kofar da karfi ta fice batare da ta tsaya rufo kofar ba.

"matakin da kake son d'auka, shine daidai amatsayinka na mijinta, domin barin dakayi tana taimakawa acikin al'amura rayuwar aurenku, shi yasa ta rainaka dayawa ,kaga mata sam ba'a sake musu dayawa sai su nemi su rainawa mutun wayo, sannan karka zauna komai mace ce zatayi agida, Duk k'ank'atar albashinka kayi amfani dashi ,karkayi kuskura ko omo wanki ne matarka ta dinga siya da kudinta ,domin karshen abu wulakanci ne da iko har ma da gori sai ta maka ."sai abu nagaba da zan sanar maka, ka d'auki kowani irin mataki kanta ,amman ban da matakin sakinta saboda nasan kana son matarka har yanzu ...

fu'ad yayi shiru yana sauraronsa har sanda ya dasa aya sannan ya d'an rutsuna tare furta "thank you so much sir Allah ya bar girma .

"karka damu fu'ad allah ya shigemana gaba" ammen ya amsa tare da mikewa tsaye .

a mota ma tunani yake yana tuki yana tunanin abinda zai je y iske agidan ..

mmn sudais ce
[11/3, 8:25 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 31 to 35

.........diraving kawai yake cike da matsanancin tashin hankali ,yayinda gefe guda na zuciyarsa ke wani irin harbawa, saboda jin bugun zuciyarsa yake tun daga tsakiyar 'kirjinsa har ilahiri

sansan jikinsa. wanda hakan ya haddasawa gefen kansa sarawa da 'karfi, gaba d'aya ji yayi jikinsa ya mutu, tu'kin ma na neman gagararsa.

A hankali ya gangara gefen titi yayi parking tare da dai-daita tsayuwar motarsa ya rungume sitiyarin motar had'e da d'aura kansa bisa hannuwansa yana fitar da numfashi me tattare da hucin zafi.

tun daga nesa Sajida wace daga gidan me'ad gidan misna ta wuce, ta hango motar fu'ad parke a gefen titi cike da matsanancin mamaki ta soma rage gudun motarta har sanda ta iso daf da inda motarsa take .
tayi parking ta fito da hanzarinta daga cikin motarta ,hankalinta a matu'kar tashe ta doshi inda yake, tana kare fuskarta da tafin hannuta saboda hasken ranar daya dallare mata idanu , jiki a sanyaye ta 'karasa jinkin motar ta tsaya tare da kai hannuta ta k'wank'wasa glass d'in motar, wanda hakan yasa fu'ad 'ko'karin d'ago idanunsa domin ganin kowaye.

A hankali ya sauke kyawawan idanunsa a kan fuskarta dake cike da mamakin ganinsa a gurin , runtse idanunsa yayi sosai yana jin wani irin d'aci a ransa mara misaltuwa ....

da hannunta tayi masa alama yayi warning glass din motarsa, sai da ya furzar da iska me zafi ta bakinsa sannan yayi 'kasa da glass din, kana ya mai da kansa kan sitiyari kamar yadda yayi da farko , shi kad'ai yasan irin rad'ad'in da zuciyarsa take ciki a kan wannan matsalar dake shirin kunno kai cikin rayuwarsa da al'amuran gidansa.

sautin muryarta yaji ta doki dodon kunneshi "lafiya Abban NASREEN kayi parking a gefen titi haka?

"idan ma wani abu ne ke damunka, kamata yayi ka samu ka qarasa gida first, domin samun natsuwar zuciya saboda tsayuwarka a nan is very very risking.. ta 'karasa mgnr tana zagayo wa d'ayan gefen tana me k'wank'wasawa alamun ya bud'e mata .

da 'kyar ya samu ya danna wani abu a cikin motar domin bata damar shigowa ba tare da yace mata komai ba saboda kansa dake cigaba da sarawa.

ta bud'e murfin motar jikinta na rawa tare da janye jakar briefcase d'insa dake kujera me zaman kanta, ta zauna tana masa fari da ido muryarta a sanyaye tace " sannu Abban NASREEN na san duk damuwar nan taka ,baza ta rasa nasaba da matsalar kawata ba?
,"amman ka yiwa Allah kayi hakuri Insha Allahu komai zai zo da sau'ki, me'ad ce bata d'aukar shawara na rasa abinda ke rud'arta....

A hankali ya d'ago idanunsa tare da waigowa gefen da take zaune ,idanuwansu suka tsarke cikin juna, suna had'a ido kowanensu ya kafe d'anuwansa da kallo zuciyoyinsu na ayyana musu abubuwa da yawa .

kallon cikin kwayar idanunsa ta cigaba da yi tana jin wani abu na yawo a jikinta ,had'e da hango wani irin  tashin hankali  kwance a cikinsu  , a hankali ya soma kokarin motsa bakinsa " kika ce kin rasa abinda ke rud'ar ta ?

ta d'age masa girarta d'aya tana sake masa fari da ido muryarta a sanyaye tace "eh Abban NASREEN ni dai gsky bansani ba, amman idan kasan abinda ke rud'arta ka taimaka ka gaya min ?

" girgiza kansa kawai yayi ba tare da ya sake cewa daita komai ba, ita kuma ta bishi da mayataccen kallo tana yaba kyawun halittarsa, ganin yadda jikinsa yayi matukar amsar kayan dake sanye ajikinsa  ya kara hura wutar  soyayyarsa acikin zuciyarta ,ji take tamkar ta shige jikinsa ta rumgume shi sannan ta rarrashsshi a kan tarin damuwarsa .

A hankali ta sauke nannauyen ajiyar zuciya tana furta" hamson kenan .....yau dai gani ga ka kyakkyawan mutumin da zuciyata ta dad'e da kamuwa da matsanancin sonshi, kyakkyawa son kowa 'kin wanda ya rasa ..." am very sorry  da abinda kaji yana fitowa daga cikin bakina , domin na dad'e ,ba tun yau ba nake son amayar maka da abinda ke cikin zuciyata, "a gaskiya fu'ad na dad'e da afkawa cikin duniyar kaunarka ,idan ba zaka damu ba zan so ka bani damar kawo farin ciki cikin rayuwarka.

" fuad ina tsanin sonka tun a ganin farkon dana maka a rayuwata, wasu dalilai ne suka hana ni fahimtar da kai tsantsar 'kaunarka gareni, amman yanzu ga dama ta samu ," ka natsu ka saurare ni ,ina son ka aure ni na maye maka gurbin da k'awata ta kasa cikewa a gidanka.

bai san sanda yayi saurin dafe kanshi ba cikin matsanancin 6acin rai sakamakon jin abinda ke fitowa daga cikin bakinta, wani tsaki ya ja da 'karfi kana yace  "kin zo ne ki 'kara min damuwa  a kan wanda nake ciki ko me?

"calm down my hamson i thoueght you feel of fended that I m disturbing you, wanda ba haka bane, ni nasan abinda nake yi, gaba d'aya nasan halin da kake ciki , nasan kana cikin damuwa fu'ad, dan haka nake neman alfarma da ka bani dama na nuna maka kalar tawa soyayyar plz....

A matu'kar firgice ya sake juyowa ya kalleta "me take nufi da shi da rayuwarsa gaba d'aya?

"lallai duniya abin tsoro, haka mutane cikinta, "me yasa sam wasu matan basu da tunani da hango abinda zai je yazo?

"ita din fa tamkar yan uwan junane suke da me'ad, tare ya sansu komai nasu tare tun daga kan sutura da komai, amman take furta wad'annan zantuttuka gare shi ,ba tare da wata shakka ba ko tsoro , "kai tur da mata masu irin wannan hali...

kusan minti goma suna zaune haka tana gaya masa zantuttuka masu sanyi da shiga jiki ba tare da yayi yun'kurin sake cewa da ita komai ba, illa zuciyarsa dake bugawa cike da mamakinta

,duk wata kalmar soyayya da zata fito daga cikin bakinta sai tayi silar bugar masa da zuciya, har zuwa sanda zuciyarsa ta kawo masa mafitar da zata tunzura zuciyar me'ad dinsa akan wulakacinta garesa zaiyi amfani da sajida ko hakan zai kawo cigaba arayuwarsu , take ya amince da shawarar da zuciyarsa ta bashi na ya amince mata kawai ko dan koyar da ita darasin dake cikin duniya .

"sajida ta kira sunansa cikin sanyayiyar muryarta me tsananin dadin sauraro "plz Abban NASREEN kace min wani abu mana, da alamun akwai abinda kake son cewa gareni ....

"zaki iya maida ni gida yanzu i think bazan iya 'karasawa da kaina ba ?
yayi mganar muryarsa can 'kasa, jikinta na rawa tace " me zai hana bari na kira Hakim direbana yazo ya same ni a nan, domin ya biyo ni da tawa motar .
kansa kawai ya iya d'aga mata tare da juyar da kansa gefe yana kallon gefen titi , dan kwata-kwata baya son cigaba da dubanta, yana jin idan ya cigaba da kallonta komai zai iya faruwa a tsakanin su ,saboda kyawun surarta, jikinta me matu'kar kyau da hargitsa lissafi ga shi tana cikin irin shigar da yafi son mace ta kasance ciki, doguwar rigar atamfa, java gold me adon flower's ta yane kanta da 'karamin mayafi baki ,doguwa ce sosai kamar me'ad dinsa, sai dai ba fara bace sai jikinta irin karuwan jikin nan gareta kirjinta cike yake bammmm da ruwan nono , dan wani lokaci yanayin jikinta na sauyawa musamman idan tana cikin farin ciki, ba dai wani tsagwaron kyau gareta ba amman akwai kyawun halittar jiki, a kallo d'aya mutum zai iya afkawa cikin tafkin 'kaunarta, katse shirun sa tayi ta hanyar cewa kad'an yi ha'kuri yanzu zai 'karaso.

kasa amsawa yayi saboda wani abu da yaji yana yawo a gaba d'aya ilahirin jikinsa me kama da shocking wanda ke haddasawa kirjinsa dokawa, cikin mintunan da basu wuce goma ba sai ga Hakim ya 'karaso a kan okada ,tana hangosa ta bud'e murfin motar ta fito a dai-dai lokacin da ya 'karaso gareta yana me rusunawa, ta mi'ka masa key'n motarta bayan tayi nesa kad'an daga jikin motar fu'ad "ka biyo mu a baya, abinda ta iya cewa kenan ta juya wanda a lokacin har fu'ad ya samu damar komawa d'ayan bangaren sannan ta shiga ta zauna mazaunin direba taja motar a guje Hakim ya biyo bayanta kamar yadda tace.

fu'ad yayi shiru yana saurarон abinda take fad'a masa a kan matsanancin 'kaunar da take masa, amman ya kasa furta mata dai-dai da kalma d'aya domin maida martanin maganar data ishe shi dashi ,saboda bacin ran da yake ciki dan gaba d'aya haushi tare da mamakinta ne ya addabi zuciyarsa .

A bakin get din gidan taja ta tsaya tare da yin hon,me gadin ya taso da sauri ya bud'e musu tasanya hancin motarsa ciki harabar gidan , kai tsaye inda aka tanada domin parking din motoci ta nufa tayi parking tana sake yi masa nacin ya taimaka ya amshi tayin soyayyarta ,a tare suka fito daga cikin motar sannan ta kulle ,ta tsaya a gabansa tana fuskantarsa tare da mi'ko masa key , wanda dai-dai wannan lokacin me'ad dake zaune cikin d'akin ta mi'ke tsaye da niyyar zuwa d'akin NASREEN kamar ance ta waigo zuwa harabar gidan, idanunta suka sauka, a kansu tsaye ,sai dai duhun daren da ya soma shigowa ya hanata gane kowace tsaye a gaban

mijinta tana mi'ko masa hannu buga da k'ari  fadadden kirjinsa ya kareta , 'kirjinta ne yayi wani irin lugud'en bugawa  da 'karfi har sai da ta kai ga dafe dai-dai saitin zuciyarta da taji yana neman tarwtsewa.

A hankali sajida take masa magana wacce ke sake kashe masa jiki "fu'ad ina sonka, bana tunanin zan iya sakacin da nayi a farkon haduwar mu, ka taimaka ka amincewa aurena plz..... tare da d'aura key'n motar a tafin hanunsa tana me shafar tsakiyar hannunsa wanda hakan yasa yayi saurin janye hannunsa "sajida .......fu'ad ya kira sunanta.

"na'am fu'ad dina ..

"zaki iya  fita daga cikin gidan nan da rayuwata gbdy tun kafin zantuttukanki su soma tarwatsa min 'kwa'kwalwa?

tayi shiru tare da tsura masa ido tana kallonsa , take hawaye ya soma ciccikowa a idanunta "kar ka min haka fu'ad wallahi... "dakata plz   just live now ya nuna mata hanyar fita da hannunsa "bazan damu da duk abinda zaka min ba, saboda darajar son da nake maka ,ka sani duk duniya babu wacce tafi can-canta ka aura sama da ni, na ha'kura da kai ne a wancan lokacin saboda lokaci ya 'kure min ,amman yanzu ina tabbatar maka sai inda 'karfina ya 'kare akanka .....

"ni dai na gaya miki ki fita cikin rayuwata, kar ki sake kuskuren furta min kalmar so, saboda ko nakasance mahaukaci  bazan ta'ba  kuskuren aurenki ba, "me na tsinta a aurena da me'ad ballantana nayi tunanin auren ki?

"kar kace haka plz, ka jarraba aurena fu'ad ... akwai bambamci me yawa atsakanina da me..

"shout up there yayi maganar a matu'kar harzu'ke wanda yasa me'ad 'ko'karin fitowa daga cikin part dinta "me ye bam-bamcin ki da me'ad?
"yadda me'ad take haka kike .....

" kar kace haka  fu'ad wallahi akwai bam-banci me tazara a tsakaninmu..tsaki ya ja  a fusace ya matse key'n motarsa  ya shige cikin  ya barta tsaye a gurin tana kallon bayansa babu kowa a parlour'n sai 'karar TV dake manne jikin bango a parlour'n  a hankali dafe da goshinsa ya nufi d'akinsa  ya fad'a saman doguwar kujerar three seater guda d'aya da ke ajiye a gefe d'aya yana lumshe idanunsa .

mee'ad ta shigo d'akin cikin sauri tana binsa da kallo  bayan taje harabar gidan  ba taga matar data kawo mijinta gida ba, muryar ta a fusace ta soma magana "wacece wannan tantiriyar da ta kawo ka gida yanzu ?

"meye ala'karka da  da ita da har take da 'karfin zuciyar tu'ko min miji har ma da shigo min cikin gida?

shigowarta da banzaye tambayoyinta gare shi yasa shi mi'kewa tsaye ya nufin hanyar bayi "honey cant to hear what am saying?

" nace wace 'yar iska ce ta kawo ka yanzu ? ta biyo bayansa tana sake tambayarsa ,yayi mata banza tamkar ba dashi take mgn ba,ya shige bayi tare da bugo 'kofar bayin da 'karfi kad'an ya rage bai bugi fuskarta ba, tayi baya da sauri tana dafe bangon d'akin gaba daya hankalinta da natsuwarta ya soma barin gangar jikinta ,idanu ta tsurawa 'kofar bayin tana mamakin abinda ya faru wanda bai ta'ba faruwa ba, a tun had'uwarsa dashi ,sam bai kasance ma nemin mata ba, ko shiga shirginsu asali ma duk macen da ya ganta bata birgesa itama sa'a taci .

fu'ad na 'karasa shiga bayi ya sakarwa kansa da ya ji yana 'ko'karin rabewa gida biyu ruwa, ya kai tsawon minti talatin yana tsaye ruwa na tsiyaya a jikinsa ba tare da ya cire kayan jikinsa ba, sannan ya cire kayan jikinsa ya soma wanka a tsanake cike da 'bacin rai "me yasa na auri me'ad? ya jefawa
zuciyarsa wannan. tambayar .

"me yasa ban yi ha'kuri da tarin soyayyarta gare ni ba ,na tunzura zuciyata gurin aurenta ,ga shi ina cikin tsaka mai wuya da lamarinta ?

"ta yaya zan auri matar da baxata iya bin umarnina ba tare da sadaukarwa gareni ...?" hakika nayi kuskure a rayuwata , tabbas nayi kuskure babba da na aureta a rayuwata ba tare da nayi tunani ba... "a zahirin gasky hakkin NASREEN sai ya kamani domin ban za6a mata uwa ta gari ba abin alfahari ba.

"why why why na aureta?
ya furta tare dunkule hannunsa ya naushi iska , da wannan tunanin ya 'karasa wankansa ya fito ,tana tsaye tamkar wacce aka dasa ta a gurin ,yazo ya wuceta yana goge jikinsa ya nufi wardrobe dinsa ya ciro jallabiyya black colour ya sanya, ya je ya kunna TV kana ya dawo kan kujera ya zauna ba tare da ya kalli inda take ruku6e ba, ya d'auki remote ya kunna AC .

me'ad ta 'karaso in da yake ta zauna kusa da shi sosai , zuciyarta na wani irin tafarfasa ta tsura masa ido tana kallonsa , da 'kyar ta samu ta tattaro kuzarinta tare da kamo hannunsa d'aya cikinsa sannan ta soma motsa labbanta "Abban NASREEN tambayarka fa nake wacece wannan matar data kawoka plz ?
" i have been talking you since, and i really has to do this before everting could have mess up wit us, kawai just tell me who is she?

hankalina ya saka kwanciya saboda ban ta'ba ganinka tare da wata ba, ballanata har ku kasance acikin motarka tare..

"ka fara neman mata ne ban sani ba ko me?

"plz talk to me now hankalina a matu'kar tashe yake..

fixge hannunsa da ke cikin nata yayi a matu'kar fusace sannan ya juyo a hankali yana fuskantarta sosai " me'ad !!! ya kira sunanta har sau uku da muryarsa a sanyaye sai dai da ji kasan yana cikin damuwa da tashin hankali "you really has carryover in your dity life for this idiot matter .

" me'ad lokacin yana neman 'kure miki amman rashin common sense dinki ya'ki bari ki hankalta, nadamar ki ta kusa zuwa gareki ba tare da kin shiryawa hakan ba , lokacin kukan ki yayi me'ad.....sannan watan da na saninki ya kusan tsayawa matsawar baki canza wannan hali da 'kudirinki naki a kaina ba.....wallahi ina me tabbatar miki sai kin yi kuka da idanunki nan gaba saboda ami.. ...

"dakata dakata malam, wani irin baki ne haka kake min ?
tambayarka kawai fa nayi ba dogon sharhi na nema daga gareka ba, da kake kokarin yi min mugun alkaba'i, idan budurwa kayi ko neman mata ka fad'a ,ai sai kasanar wa mutane bawai kasoma wa mutun mugun baki ba, duk ma abinda zaka yi kaje kayi yayi wannan matsalarka ce ba tawa ba, ni dai yadda gobe zata kasance nafi bukata son sani ba wani surutunka ba.

"who is going stay at home with our daughter tomorrow simple as that?

"i don't know, and if you dare ask me this stupid question again i will deal with you right now,
"shasha kawai kina nan kina haukan banza ana miki zagon kasa a kan wannan banza aikin naki wanda nan gaba zai jawo miki nadama mara amfani ,amman muje zuwa ya 'karasa maganr yana maida idanunsa kan tv..

zabura tayi ta mi'ke a fusace" kaine zaka yi nadama domin kuwa ga tarin nadama nan a 'kwayar idanunka ina hangowa.

"nadamar aurenki ba ya juyo a matu'kar harzu'ke yana dubanta "nadamar aurenki kawai ke cikin 'kwayar idanuna da zuciyata ,wallahi mead i regret married you in my life ,a yanxu na tsani kaina da na zabe ki a matsayin abokiyar rayuwata .

" na d'auka aurenki farin ciki ne gareni ashe tarin damuwa da bakin cinki ne, wallahi ban san yadda zaki kasance min kenan ba da ban amincewa aurenki ba, nayi da nasani yafi sau ba adadi a kan aurenki da nayi ya 'karasa maganar yana me
jan dogon tsaki da zance zuci
" ban san me ya shiga cikin tunaninna ba a kanta?
ban san abinda ya kai ni amincewa zucuyarta a kanta ba?

"a da can baya da mahaifinta ya'ki yarda da aurensu , ya ha'kura da ita amman daga baya ta sake dawo cikin rayuwarsa wanda silar haka komai ya faru da shi ya furzar da iska me dumi ta bakinsa .

ficewa tayi daga cikin d'akin zuwa nata d'akinta, a hankali ta shiga zagaye d'akin hanunwanta sar'kafe cikin juna gaba daya ta kasa tsaye ta kasa zaune, sai zarya take tana yamutsa gashin kanta tare da ri'ke kunguntta tunanin abubuwan da suka faru a baya kafin aurensu take"anya kuwa tayi masa adalci da hallaci a rayuwa.....?

"kasa sukuni tayi  har zuwa sanda aka kira sallahr isha'i, gabadaya abubuwa ne suka shiga dawo mata, tun daga kan haduwar da fu'ad har zuwa  rayuwar aurensu da rashin lafiyar NASREEN kawowa wannan matsalar dake faruwa dasu. tana kiyo sanda fu'ad ya fita tasan masallaci yaje dan haka jikinta a mace ta fito tashiga d'akin NASREEN taba abinci da magani sannan ta dawo daita parlour'n ta kwantar daita tare da yi mata makarin da pillow ,zata   juyo kenan  NASREEN ta riko hannunta "momy..

"yes dear kina son wani abu ne?

yarinyar ta girgiza kai tana dubanta sannan tace" momy meyasa bazaki zauna agida ki kula dani ba kmr yadda doctor yace?

"nafi son ki zauna atare dani..... ..

shiru tayi ta tsura mata ido kawai tana kallonta ,NASREEN ba dai fitar da zance ba, idan tayi mgn xaka  d'auka shekaruntta ya wuce yadda take.
"karki damu baby your dady will be with you zama agida akwai matsala, kinga babu wanda zai taimaka mana, ki duba nawa nake biya school fees dinki da sauran abubuwa idan nace zan ajiye aiki komai zai iya faruwa,kiyi hakuri dad dinki zai kula dake fiye dani kinji an...

k'arar bude kofar ta jiyo ne ya katseta ,dan tasan kowaye, yana gama sanyo kai taga malik abokinsa yashigo, mikewa tayi tana gaidashi cike da farincikinta ,shima ya amsa yana tambayarta me jiki "jiki da sauki gata nan sai rigima.

yayi murmushi yana zama kusa da NASREEN  shima fu'ad guri yasa ya zauna yana shafa kanta,ita kuma me'ad tashege kitchen cikin kankani lokaci ta shake musu Center table da abun motsa baki dan tasan sai tara yake cin abinci, sannan ta nufi d'akinta gabatar da sallah ..

hira suke atsakaninsu wanda duk akan rashin lfyr NASREEN ne, sukaji sautin muryarta "dady momy said you are  going to stay at home with me?

ya juyo ahankali yana duban fuskar kyakkwar diyarsa batare da yace mata komai ba, gbdy yarasa me ma zai ce wa yarinyarsa ,domin yasan idan yace mata bashi zai zauna tare daita ba , zata ji babu dad'i shi kuma bayason damuwarta, dan haka  ya tsinci kanshi da ce mata "yes I m going to stay with you my baby.. fara'ar dayaga ta bayyana a saman kyakyawar fusakarta yayi matukar bashi mamaki .."thank you my dad that's why i love you more..

"i love you dady..... "i love more baby ya fad'a tare da shafa kanta .

malik yace " ni fa baki sona ko babanki kawai kike so?

tayi murmushi wanda ke fidda kamaninta da mahaifinta sannan tace "ina sonka amman sai kabani labaru mamana da babana ....ya kwashe da dry "kaji yarinya da wayo suna zaune me'ad ta sake dawo "honey dining ya kammala "okay kawai yace mata ataikace saboda bayason jan magana " uncle malik kana nan sauraren shirme NASREEN ko?

yayi murmushi "babu wani shirmen datake, hirarku muke daita, kuje kuci aninci larku biye mata dan ita taci .

kukan shagwaba NASREEN ta saki "dady kana jin momy ko?
"karki damu daita itace ke shirme bake ba.. me'ad ta juya ta sake komawa d'aki ,fu'ad ya mike shima "kaje kaci abinci malik. kai fa ?
"bana jin yunwa koma ina banji zan iya sakawa cikin komai.."dan Allah fu'ad ka cire damuwar nan hk..

"bazan iya ba, duk randa kaga na cire damuwar nan na rabu da me'ad ne yakarasa mgnr yana barin gurin jikin malik yayi sanyi sosai kmr zai zubar da hawaye haka ma NASREEN "uncle malik meyasa dady'na zai rabu da momy?
"basuna son junansu sukayi aure ba?
"dan Allah uncle malik kabani labarin.. ina son jin labarin iyayena... ..

runtse idanunsa yayi sosai ya kasa cewa komai kafin daga baya yasoma magana ahankali

mmn sudais ce
[11/3, 8:25 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 36 to 40

ASALIN MAHAIFINKI

fu'ad Muhammed argungu d'an asalin karamar hukumar argungu ne dake jahar kebbi, cirani ne yashigo da kakaninsa garin lagos , wato malam musa da mai d'akinsa halima da yaronsu muhammed , inda sukayi masauki a unguwar g'begulori dake karamar hukumar agege, fu'ad bakabe ne daya fito daga cikin kabawan asalin jahar kebbi ,yayinda danginsa gbdy suka kasance talakawa ne tulis .

tunda malam musa ya dira a garin lagos bai ta'ba zama daidai da rana daya da sunan hutu ba, kullun yana fita neman abinda zai ci da iyalisa ,ba wata sana'a malam musa yake ba illa aikin dako cikin kasuwar matuwaf zuwa ketu ,Allah yasanyawa aikin dakonsa albarka domin basu ta'ba neman abinda zasu ci sun rasa ba ,kuma tun daga kan muhammed Allah bai sake basu haihuwa ba ,dan haka suka d'auki soyayyar duniya suka d'aura akan tilon d'ansu da Allah ya basu ,duk da kasancewarsu talakawa amman hkn bai sa sunyi sakaci da tarbiyar yaronsu ba ,suna iyakacin bakin kok'arinsu akan ganin sun inganta rayuwarsu data d'ansu ,domin sunyi kok'arin sanyashi makaranta gwanati dan samun cigaban rayuwarsa .

"haka rayuwarsu tacigaba cikin talauci da babu har yasamu ya kammala secondary school dinsa a ikeja high school daga nan bai cigaba da karatu ba , sai dai ya Kan fita buga bugarsa duk inda yaga aikin karfi zaiyi fassakare ne wanki da guga zaiyi . Muhammed ya taso tare da mahaifansa har zuwa girmansa , kafin Allah ya had'ashi da ramlat, wace suka kasance diyar makotasu ce ,sukayi aurensu bisa amana da soyaya.

fu'ad shi kad'ai iyayensa suka samu ya tsaya a duniya ,dan haihuwarsu biyar yaran suna mutuwa akansa suka samu ya tsaya wanda sanadiyyar haihuwarsa, mahaifiyarsa ta rasu ,a cewar mutane bama tasan abinda ta haifa ba ta cika, sai rikonsa ya dawo gurin kakaninsa, lokacin daya kai shekara bakwai mahaifinsa ya rasu sakamakon ciwon hawan jinin daya kamu dashi a tun mutuwar matarsa ramlat, ba a d'auki wani lokaci me tsawo ba malam musa shima yace ga garinku. gidan ya saura daga halima sai fu'ad.

fu'ad yayi karatunsa na primary har zuwa jami'a ahmadu bello, bisa tallafi na gwanati da taimakon Allah dana kakarsa inda ya karanci business administration.
,fu'ad ya sha matukar wahala gurin karatunsa saboda rayuwar babu da suke ciki ,da taimakon scholarship dana abokai da tsohuwar kakarsa halimatu yasamu ya kammala karatunsa da kyar ,bayan kamala karatunsa da bautar kasa yashiga wahalar rayuwa sakamakon rashin samun aiki , kafin had'uwar sa da mom dinki ya kwashe shekaru sama da shida yana zaman banza batare da yasamu aiki ba duk da kyawun da takardunsa sukayi.

" sun had'u da me'ad ne
A wata safiyar litinin .

labari ya karad'e koina akan zance batakashin da'akayi a garin lagos duk gidan tv da radio daka kuna a lokacin fuskar ACP Aliyu rano ake nunawa da tawagarsa rike da bindigunsu suna

harbi .

ni da fu'ad ne muka shiga cikin wani d'an madaidacin shago inda muka saba yada zango ,muna shiga na ja na tsaya ina murmushin jin dadi,yayinda fu'ad dake tsaye a bayana yasa hannusa ya buge min keya "banza kawai munafukin Allah ,gulma nacinka ko?

bud'ar bakina sai cewa nayi "abokaina yau fa fu'ad yayi kasuwa da ala'mun shima yau ya fad'a tarko kauna nakarasa mgnr ina kwashewa da dry har da tafa hannu.
"kajika da wani zance iska inji cewar sauran abankanmu, sudais, Abdul da kabeer .

kabeer yacigaba da magana idanunsa na kan kallon tv "yayi kasuwa fa kace kmr wani kayan marmari.

"allah kuwa yau naga qunjinsa domin ya had'u da yarinyar da bazai iya hakura daita ba.
" dan Allah malam karka damemu zauna ka kalli abinda duniya take ciki.. zaro ido nayi sa sauri lokacin da idanununa ya sauka akan TV "kai kai ai naga wannan mutumi da'ake nuno yanzu , wannan batakashin da kuke kallo agabana fa akayisa ,shi dai fu'ad bai ce komai ba yakarasa kan doguwar kujera ya zauna yana duban abinda ake nunowa a TV wanda agabansu komai ya faru.

"kana nufin ka ganshi inji cewar kabeer?

"Kwarai da gaske na ganshi da idanuna, "kai dai wallahi babban makaryaci ne ,yau kuma da karyar daka zo mana kenan?inji cewar abdul ..

"Na girgiza kai tare da kallon fu'ad ,"fu'ad dan girman allah kayi magana zasu fi yarda da maganarka saboda muna tare da kai lokacin da abu ya faru .

fu'ad na jinsa ya sake mikewa akan doguwar kujera yayi kwanciyarsa tare da lumshe idanunsa duka , ya d'aura hannunsa ya dafe goshinsa dayan hannunsa na saman ruwan cikinsa, kasancewarsa marason hayaniyya.

duk surutun danakeyi banza sukayi dani suka cigaba da saurarон labarin da'ake watsowa suna kur'ba ruwan Lietop.

" kunga wallahi da gaske nake kai dai fu'ad wallahi banza ne ,kana ji ana kokarin meidani makaryacin karfi dayaji amman kayi shiru.

"me ka keson nace fu'ad ya fadi hkn atakaice batare daya bud'e idanunsa ba.

"ka gani ba dan Allah kayiwa mutane shiru, shi kansa fu'ad din bashi da tabbas da zance dake fitowa daga cikin bakinka duba da yanayin da yayi magana to yaya kake son mu dake zaune agida mu yarda bayan karyar abincin ruhinka ne daka kashigo fa zance yarinya kake yi ,cikin

minti biyu kacal  kasanyo wani zance daban .

 "eh naji karya abincin ruhina ne, amman wallahi wannan zance ba karya bane ,koda nasaba yi muku karya ,ku matso kuji yadda abun yakasance nakarasa maganar ina me zagayo na zauna akan table ,gabayansu suka zagayeni " muna jin ka fad'i kuma wallahi kana somawa da karya zan gane  ka kuma san karshen abun..inji cewar kabeer.

"ina zaune wancan dan iskan yace na rakashi inji din ciro kudi  ,muna isa aka  fara ruwan sama tare da  walkiyya.. nakarasa mgnr ina zabgawa kabeer duka ajikinsa "kai dan Allah  malam da baki ake bada labari ba da hannu ba "yi hakuri abokina abinda idanuna suke hangomin ne abun birgewa ,tsawon lokaci muna tsaye har ruwan yasoma tsagaitawa mukayi tunanin mu fita saboda hango inuwar mutun tsaye"bude kofarmu ke da wuya sai naga wata kyakkwar yarinya kirar Japanese tsaye  cikin doguwar rigar har kasa hannunta rike da lema ,kyakkwa ce yarinyar sosai  ,ku tamabayi fu'ad dan lokacin na lura har yafini gigicewa akanta, amman sai naga ya waske ita kuma yarinyar idanunta na kansa ta tsura masa ido tana kallonsa, bud'e bakin yarinya keda wuya tace "sannu amman gsky kunjima da yawa sai wani zarar kudi kuke kmr wad'an da zaku cire kudin bank din duka.

nayi saurin cewa "dan Allah kiyi hakuri ai  tuni muka cira , tsayawa mukayi domin fakewa ruwa ,amman bamu aron lemarki sai mun d'an tsaya daga waje ke km  sai shigo idan kin cira sai mu dawo mu tsaya ana .

"a tunanina ni zatabawa lemar tunda ni nayi mata  magana ta fahimta , amman sai naga ta mik'awa wancan dan isakan lema,  ya nuna inda fu'ad ke kwance ,in dai takaice muku  ko damuwa da kulawar data  nuna masa bai yi ba ,sai ma zagayeta da yayi ya wuce yayi gaba ya tsaya tare da tura hannunwasa duka cikin aljihun wandonsa , ina lura da yadda yanayin yarinyar ya sauya, ba dan taso ba ta miko min lemar wanda kad'an yarage hannunmu bai had'e da juna ba, na matsa mata tashiga, ni kuma na fito na tsaya ina karewa halitar jikinta kallon , ina gaya muku kywaun yarinyar ya had'u sosai.cikin mintunan da basu wuce goma ba ta fito idanunta akan fu'ad ,sosai fa  kura masa ido tana takowa zuwa inda yake tsaye.
 cikin hk ruwan saman ya tsaya cak sai kuma harbi takoina a harabar gurin, harbi fa sosai ban san yadda akayi ba sai dai ganin nayi fu'ad ya kamo hannuta sai ga yarinyar manne da kirjinsa nan take suka tsurawa junansu ido suna kallon junansu, wanin harbin yasa tayi saurin shigewa jikinsa gabadaya domin neman mafaka.

cikin minti biyu kacal duk ilahirin gurin ya har gitse, jamar dake wucewa a gurin bubu wanda ya damu da halin da kowa yake ciki, kowa gudun ceton ransa kawai yake saboda gabadaya gurin ya hargitse da k'arar harbi, police na harbi ,y'anta'ada na meida musu .

"ai in gaya muku na rud'e tare da gigicewa amman fu'ad da yarinyar nan ko ajikinsu kallon junansu suke  karasowa garesu nayi ina girgiza fu'ad  domin shi nake da yancin tabawa, nayi sa'ar ya dawo cikin haiyacinsa amman ita yarinyar ruhinta yayi nisa akansa  ,girgizata fu'ad yasoma yi amman ina bata ma san yanayi ba, cikin rud'u ya rike hannunta ya kwasa aguje

yasoma gudu daita, ganin harbin na sake yawa, sannan yana kiran sunana ,ni kuwa daman tuni na boye bayan inji din cire kudi ina kirma..

"kusan awa daya ana batakashin tsakanin 'yanata'ada da police har zuwa sanda acp aliyu rano yayi nasarar harbe wannan mutumin a kirji sannan komai ya lafa gurin gbdy ya turnuke da hayaki daya bayan daya mutane suka soma bayyana fuskarsu cike da matsanancin firgici daga mubuyarsu, ni kuwa sai ware ido nake naga ta inda fu'ad zasu fito, ahankali sai ga fu'ad da yarinyar nan makale da juna sun fito daga mabuyarsu aiko gama bayanarsu ke da wuya sai agaban acp wanda naji yace"a'a me'ad me km kike yi anan ?

hankalinta kwance tace "uncle nazo cire kudi ne ina fatan babu abinda yasameka? ta fadi hkn ne saboda ganinsa rike da hannunsa ga jini na tsiyaya alamun an harbeshi .

" ina jin dai lafiya kalau nike me'ad, waye wannan da kuke tare dashi ?

da sauri ta juyo gefenta fu'ad tagani tsaye agefenta hannunwansu malake cikin juna ,jin Abind acp yace yasa fu'ad yin sauri zare hannunsa cikin nata yana shafa sumar kanshi .
d'an runtse idanunta tayi kana tace "amm bansashi ba ucnle ,yanzu muka had'u dashi ta juya tana kallon fu'ad kmr zata cinyeshi muryata a sanyaye "tace sunana me'ad nagode da taimakona dakayi.

"muryarsa a dake yace ni kuma fu'ad karki damu ya juya ,naga yasoma waige waige ala'mun yana nemana, ita kuma tabishi da kallo yayinda acp aliyu yakira daya daga cikin yaransa "md .

"na'am yallabai .

" taimaka ka'ajiye min wannan yar tawa a gida.

"ok yallabai kasa daga kafafunta tayi agurin, tacigaba da kallon bayan fu'ad .
ina kallonta, jiki a sanyaye tashiga bayan wata hadadiyar mota kiran toyata camry .

Ina kawowa karshen labarin nace ni dai dan Allah ku gaya masa idan bai sonta ni dai ta min, ina sonta kuma aurenta zanyi, aikuwa suka ce me zasuyi ba dariya.... "kai wallahi bazan ne a gbdy labarinka fu'ad take so bakai ba ,koda yace baya sonta kana tunanin zata soka ne?

take na marairaice murya da fuska "ni dai ku taimaka ku tambayar min shi idan bai sonta ya tsaya min na aureta, wallahi dagani yar babban gida ce kunga motar da za'a kaita gida dashi kuwa , kuma dagani akwai halaka me karfi atsakaninta da acp Aliyu rano..
"kai dan Allah malam rabudamu da wannan shirmen banza suka soma kokarin watsewa su barni ,nayi saurin kamo hannun sudais, kai ma tafiya zakayi kabarni?
"Kai rabu dani, idan kana son yarinyar da gaske kawai ka nemi gidansu Dan gsky nasan fu'ad ba saurarantaa zaiyi ba ,dan shi bashi da lokacin mace ,mata nawa suka nuna suna son shi Amman yaki?

********
bangare me'ad kuwa zuciyarta ce ke mugun buguwa a tun sanda tashiga bayan motar tare da hasko mata kyakkwar fuskarsa "tun datake bata ta'ba had'uwa da saurayin daya tsaya mata arai ba kmr shi, sai dai daganin zai yi jin kai da girman kai tattare da isa.

zaune suke su uku sajida misna hailat , sun mugun tsurawa TV plazma ido dake manne da bango suna kallon batakashin da'aka tafka tsakanin 'yanta'ada da ma'aikan sack a dapemu express way dake jahar lagos "barkanmu ,a yau anyi musayar wuta tsakanin 'yansanda ,da 'yanta'ada an samu nasarar harbe wani dan ta'ada me hatsari, acp aliyu rano da jamiansa su sukayi nasarar harbe nabel wanda ya kasance babban dan ta'adar da jamian tsoro suka dade suna nemansa a fadin jahar nan.

"yeeeeee babana yazamo zakaran gwaji..... sajida tasoma murna har da tsallenta "nasan kwanan nan za'ayi wa babana k'arin girma...murna take sosai tare da rungume misna dake kusa daita "gsky na taya dad dinki murna sosai inji cewar misna , hayaniya ce ta kaure atsakaninsu kowanensu na fad'ar albarkacin bakinsu.

me'ad tashigo hadadden parlour'n gidan wanda ya k'awatu tamkar da tayis akayi ginin ,gashi an zagaye shi da manya furanin.
hannuta rike da karamar jaka wace bata wuce a sakalata a tsintsiyar hannuta ba tana juyi sanye cikin doguwar rigar " kawayena yau na had'u da wani saurayi kuma ko wallahi kyakkyawa gaske ne kalar launi danafi so.. takaraso garesu tana murmushin jin dadi "kunji aunty dan allah da wata magana ana labari da d'umi d'uminsa ke kuma kina labarin wani saurayi , "dan Allah malama kiyiwa mutane shiru had'ad'd'e ne fa sosai, Allah ina gaya muku duk fadin garin nan babu me kyawumsa ta karasa fad'ar hk tana sake juya jikinta .

"haka zakice tunda zuciyarki ta yaba dashi ba ,da baki yaba dashi ba duk kyawunsa sai kin nemo makusansa" kmr kinsani kuwa inji cewar misna .

"wai ina miki wasa ne suhailat, ko dake nake maganata? ta fad'i hkn tana tsaki sannan ta fuskanci sajida da misna.

"ku kuma daku fa nake mgn amman kuka min shr , ba ma zaku saurareni ba ,kuna can kallon kwazon da acp yayi "ke dai bari me'ad Allah ina cikin jin dadi yau ,ina ma mama tana raye ta dinganin irin cigaban da baba yake samu, wannan furunci da sajida tayi yasa me'ad kasa cigaba da tsayuwa a gurin ta nufi hanyar d'akinta tana magana "Allah ya jikanta sai dai ki shiyawa jinyar dad dinki bayan kingama tayasa murna k'arin girman da zai samun saboda 'yanta'ada sun harbeshi .

da sauri sajida ta mike jikinta na rawa tabiyo bayanta atare suka shiga dakin "da gaske an harbi dady?

"ke baki lura ba, bakiga ya dafe hannunsa na dama ba?

"ina tunanin anan aka harbe.......
ai sajida bata jira jin karashen zance ba, tayi waje aguje tana kiran layin dad dinta, tayi sa'a ya d'auka "hello dady..

"sajida kina lfy?

" ina lafiya dady kana ina?" yanxu me'ad ke gaya min wata mgn da gaske ne 'yan ta'ada sun harbeka?

"gaky ne sajida ,duk boyewar dana yi ashe ta lura, to dai ki kwantar min da hankalinki, yanzu haka an cire min harsashi ,  mu had'u a gida, kashe wayarta tayi  tare da bud'e murfin motata tashiga ta bar gidansu mead  a guje.

mmn sudais ce[11/3, 8:25 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 42 to 44

......Ahankali malik ya sauke kwayar idanunsa akan NASREEN dake kwance ajikinsa ,wacce bacci yasoma kok'arin d'aukarta amman son jin labarin had'uwar iyayenta ya hanata runtsawa .

shiru malik yayi yana dubanta batare da yacigaba ba, ya d'auki sama da minti goma  a zaune kawao yana kallon NASREEN cike da tausauawa, yarinyar tana bukatar kulawa takowani bangare, amman tarasa shirun  da NASREEN taji yayi yawa ne yasa ta, bud'e idanunta dake runtse taki sunansa "Uncle malik  continue now.... kacigaba ina son jin komai, domin kai kad'ai ne zaka iya 'bata lokacinka ka gaya min.

"NASREEN  ...ya kira sunanta a sanyaye "na'am unlce "kwalkwaluwarki bazata iya d'aukar sauran labarin ba.. "zan iya uncle am getting to 10yrs now babu abinda zaka fad'a da bazan fahimta ba.. ina jin tausayin dad dina dayawa, ina son nasani wani abu akansa takarasa maganar tana meida kanta bisa cinyarsa..

naunayen ajiyar zuciya ya sauke tare da cewa "daga bangaren fu'ad da me'ad babu wanda bansan halin dayake ciki ba, akoda yaushe muna tare da fu'ad, haka me'ad duk inda tasanya kafa ina biye daita sai dai a iya nan zan tsaya ... ya d'auke kanta akan cinyarsa ya meida kan karamin kushin din dake jingine da kujera, sannan ya mike tsaye yana duba agogon bangon parlour'n karfe tara ta wuce da wasu 'yan mintunoni, wayarsa ya ciro daga gaban aljihun gaban rigarsa yana kokarin neman layin fu'ad, sai gashi ya fito "yauwa zo kaji da wannan yar rigimar taka, ta matsa,lallai sai taji haduwarku da me'ad, ni dai nayi kok'arin sanar daita kad'an daga cikin had'uwarku sauran kuwa na barta da bagudo takarasa mata yakarasa fadar hk yana murmushi, murmushi fu'ad yayi shima sannan yakaraso inda take kwance kmr ruwa , ya komata ya zaunar daita tare da yi mata makari da pillow ta bayanta "kinji abinda uncle malik yace ?

"ni ..ni naji amman babu ruwana dashi tunda yaki yacigaba dabani labarin, takarasa mgnr muryarta a shagwabe kmr zatayi kuka,kissing din goshinta yayi "don't cry my bby rabu dashi kinji bby nah ni da kaina ma sai nabaki, ai zaki fi son nawa ko?
ta gyda masa kai kawai batare da tace komai ba fu'ad ya fuskanci malik "yanaga kana kok'arin tafiya batare da kaci komai ba?

"kai rabani da cin abincin nan, yanzu ina ci idan naje gida sai nayi bayani daya bayan daya, an dinga yi min qausetion's kenan ,gara kawai idan na koma gidan naci gbdy, ok muje na taka maka "baby nan ina zuwa just give me w minti .
har waje fu'ad ya rako malik suna sake tautaunawa akan sha'anin rayuwa, da hakuri da rayuwar ita karon kanta ...

koda fu'ad ya koma parlour'n bai iske NASREEN ba ,dan hk kai tsaye ya nufi d'akinta ,inda ya isketa kwance cikin blanket dinta, ya yaye blanket din tare da d'aura hannunsa kanta "my bby kin sha maganinki? "yes dady .
"ok kiyi bacci abinki Allah ya baki lfy me d'aurewa .
"ameen babana, shiyasa nake sonka.....
"i love you more yacigaba da zama yana dubanta tana matukar bashi tausayi yana jin kmr ya ajiye komai ya bata kulawar data dace, ita kad'ai garesa kmr yadda ya kasance, a zahirin gasky baya son yarasata duk da kasancewarta mai karancin lfy yana sonta hk... tsawon lokaci yana zaune yana tunani har sanda bacci ya d'auketa sannan ya yunkura ya tashi ya nufi d'akinsa ya kwanta lamo akan gadon yana tunani ya saka wancan ya kwance wancan, runtse idanunsa yayi sosai yana kiran sunan Allah, ahankali ya bude idanunsa wanda suka kad'a sukayi jawur saboda tuno abinda yake yi masa cikin rayuwarsa, a filli yace "nayi dana sanin aurenki me'ad dana san hk zaki zamomin arayuwata da ban yi kuskuren aureki ba...hawaye ne yaji suna sauka masa akan kuncinsa ,cikin sauri ya sharesu, lokacin ne wayarsa ta d'auki kara, ya kai hannunsa ya d'auka akan bed side ya manna a kunnesa batare daya duba ba.

sautin muryarta yaji ta doki dodon kunneshi ,yayi Shiru tare da janyo pillow ya manna akirjinsa ya rungume tsam sbd d'and'anon dadin muryar "hello hello fu'ad kana jina !! ta sake maimaitawa akaro na biyu.

"uhmm ya'akayi  kira adaidai wannan lokacin ko kin manta ina iyali ne ?
"am sorry for disturbing you , but ina son ka saurareni fu'ad kaji abinda za....

saurin katseta yayi ta hanyar cewa "sauraran me zanyi miki, karki meidani wani shasha mana ,ta yaya kike kokarin manta dangantakarki da me'ad mana ,karki manta har yanzu me'ad matsayin matata take, dan me kike kokarin  sanyo damuwa acikin wace nake ciki....?

" fu'ad ka saurareni mana, haba fu'ad ya dace ace nasamu kar'buwa a wajenka a daidai wannan lokacin, na d'auki sama da shekaru goma ina dakon soyayyarka batare dana fayace maka ba .

" wannan damace tazo mana, kabari mu dama mana dan Allah ... karka ki amsar soyyayata saboda dan adam daraja garesa, idan ka amince zaka aureni zan ajiye komai har aikina domin na baka farinciki dakarasa.

"dakata dakata malama enough is enough don't  talk any rubbish.. "kinsa yadda zaki bani faricikin any not ki fahimtar da me'ad tabi abinda nake so domin a zauna lafiya?

" ni dai ka ajiye mgnr wata me'ad kawai ka amince da au..

"ok baxaki iya bata wannan shawarar ba amman zaki iya shigowa gidanta amatsayin kishiyarta ko...?

"ka fahimceni fu'ad ba ...

"babu wata fahimtarki da zanyi idan ma aure nake da bukata ,bake zan aura ba.... bake ya dace na aura ba, ina da ido nasan inda mata suke okay, dan haka ki shafa min lfy if not zan gayawa me'ad da kaina tasan yadda zatayi dake ya katse kiran yana fitar da numfashi sama sama.

"meyasa kayi haka?
zuciyarsa ta kismamashi hkn, "m e yasa baka amshi tayin soyayyarta ba?
take yabawa zuciyarsa amsa da, bazan k'ara wannan kuskuren ba bazan sake kuskuren auren ya'yan masu arziki ba.......

a ranar fu'ad baiyi ishashen bacci ba, juyi kawai yake ga tunanin ciwon NASREEN ga kewar iyayensa dake addabarsa uwa uba matsalar me'ad da sabuwar matsalar dake shirin kunno kai, har karfe daya ta buga fu'ad bai san yadda zai yi da al'amura dake kokarin kusowa rayuwarsa ba. ahankali tunanin haduwarsa da me'ad ya dinga zuwa masa daki har zuwa lokacin da sajida ta bar gidansu me'ad agigice zuwa gidansu taga lafiyar mahaifinta .
"koda sajida ta koma gida hankalinta yayi matukar tashi saboda ganin raunin harbin da d'anta'ada yayi masa, kuka take sosai tana "furta  sannu dady ..shi kuma yana rarashinta da kyar dai yasamu tayi shiru.

ita kuwa me'ad bayan ta tagama kimtsa kanta tattare da tunanin sabon fuskar data tsaya mata arai ta nufo hanyar parlour tana kwallawa me aikinsu kira " ummi ummi!! har takaraso parlour'n shiru babu kowa hatta misna da suhailat basu gurin, nan ranta ya soma baci tashiga kai kawo ta sake dawowa cikin parlour'n tattare da matsancin damuwa tasamu guri ta zauna tare da d'aura kafar daya kan daya tana girgizawa tare da cizon yatsanta ummi dake d'akin suhailat tana mata guga tayi saurin ajiye Iron ta fito da gudu tana haki, cikin rawar murya tace "aunty gani me'ad ta d'auke kanta cikin isa tace, "ummi ina son tambayarki...

ummi ta d'aga kanta da sauri cikin tsoro jikinta yana rawa tace "kiyi duk irin tambarki da kike so.

me'ad ta sake d'aure fuska kana tace "wai shin nan gidan ubanki, ko kuwa da gadonki acikin wannan gida..?

da sauri ummi ta sake d'ago fuskarta ta kalli me'ad lokaci guda, kuma tayi saurin d'aukewa dan wani irin kallon da me'ad ta watso mata, sannan cikin rawar muryar tace babu ko daya sai dai kawai cin arziki danake yi acikinsa.

"okay a she kinsan cin arziki kike yi amman kike neman kifi ya'yan gida sakewa, ki km fisu iko ko?

ita dai ummi tayi shiru kawai tana kallon kasa dan daman hk halin me'ad din yake duk wanda yake kasanta ,sai yayi hakuri, in kuwa ba hk ba zai rasa aikinsa acikin kankanin lokaci. me'ad ta girgiza kafarta cikin isa da iko "daga yau duk sanda na sake kiranki, kikayi banza dani wallahi kinji na rantse in har baki rasa aikinki ba, zaki had'u fushina jahila kawai dabba mummuna.......

mmn sudais ce
[11/3, 8:25 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 45 to 46

........."Wallahi Ba kiga yadda na tsanaki ba, ji nake kmr na kasheki ta had'e hannunwanta duka

biyu al'amun da gaske zata iya aikatawa abinda ta furta .

da sauri ummi taja baya tare da furta " Dan Allah aunty kiyi hakuri Insha'allahu bazan sake ba,zan kiyaye ....

"Kar ma ki kiyayye kiga yadda zanyi dake .

"Kiyi hakuri ta sake furtawa jikinta a sanyaye "Dan Allah malama banason long talk tashi ki bani guri kazama kawai.

Ummi ta mike jiki a sanyaye babu laka ta fito, idan da sabo tarigada ta saba da wulakancin me'ad.

Me'ad taja dagon tsaki lokaci daya taji gabanta yayi wani irin mahaukacin bugu da karfi , tayi shiru tana tunanin abinda ya sata jin hk, take fuskar fu'ad tasoma yi mata gizo acikin 'kwal'kwaluwarta ,runtse idanunta tayi kawai ta d'auki wayarta tare da mikewa tsaye ta haye sama inda mahaifiyarta take zaune da system agabanta tana tura sakonni, shigowarta d'akin yasa mom dinta d'agowa tare da cewa " yauwa gara da kika shigo, yanzu nake son aikawa akira min ke, me'ad takaraso jiki a sanyaye ta zauna kusa daita "gani sweet momy dina,ina matukar alfahari da kasancewarki mamana "uhmmmmm dan kinga abbanki baya kasar ba,?

"kai momy wai meyasa kike kishi da dad ne?
"nifa gbdyanku ina sonku domin banida abin so fiyye daku a duniya ku ne komai na.

"kinga bason zance karya ina file din da hjy maryam tace ta tura dazu da safe?

tsam tayi da ranta sannan tace" yana cikin jakata "okay je ki zo min dashi yanzu akan aikinsa nake.
cikin mintina kad'an me'ad ta fito daga d'akin mom dinta , ta nufi d'akinta tasoma duba jakarta amman abun mamaki babu diary dinta ballanatana file din dake ciki, gabanta ne ya sake fad'awa , lokacin da 'kwal'kwaluwarta ta hasko mata ko dai ta yarda dashi agurin batakashin da ya rutsa daita gurin cirar kudi.. "tabbas in har bata ganshi ba definitely acan ta yar, ta furta hkn a fili tana cigaba da bincike gefe da gefen jakarta sannan cikin sauri ta fito da niyyar komawa gurin, har zata fita sai taga kmr shigarta batayi ba, basani ba, ko zata sake had'uwa da wannan kyakkyawan fu'ad , Dan haka takoma cikin d'akinta .

ta fito cikin wani koren voyal dinki doguwar riga har kasa ba D'an kwali a kanta ,sai koren mayafin data yane kanta dashi, takalman kafarta suma duk kore ne, ta cigaba da tafiya cikin yanga, ta isa inda aka tanada domin ajiye motocin gidan, ta tsaya tana karewa motocin kallo ,4mart itace wace zuciyarta tabata umarnin shiga .

Tun kafin ta kunna motar me gadi ya zabura ya mike tsaye, yasoma kok'arin bud'e mata get, ahankali tasanyo hancin motarta wajen gidan..a natse take tukin m .

kai tsaye ta d'auki hanyar isa inda suka had'u da fuad ,cikin kankanin lokaci ta iso ,tasamu guri tayi parking din motarta ,tana bin gurin da kallo abubuwan da suka faru a d'azu da safe ne suka shiga dawo mata, tun daga kan sanda ta d'aura idanunta akansa ,har zuwa lokacin data nutse a tsakiyar faffad'an kirjinsa...fuskarsa , ajinsa, jin k'ansa da komai nashi sunyi mata ,ta dad'e bata ga halitar da kai tsaye aganin farko ya mamaye zuciyarta ba .

fitowa tayi daga cikin motar ahankali tana dube dube, duk da zuciyarta na tabbatar mata bazata gansa ba adaidai wannan lokacin ,dan haka tasoma duba inda suka had'u, bata jin ATM dinta domin tasan cikin kankanin lokaci zata mallaki wani ,tafi bukatar diary din dake d'auke da manya sirrinkan rayuwarta tare da file din momy dinta, da shi kanshi fu'ad ,Saboda idanunta na matukar kwad'ayin sake ganinsa .

ta kasa hakuri tsayuwa guri daya, tayi tafiya me nisa dan har ta kusan shiga alimoshi local government, amman bata ga ko mai kama da fu'ad ba da da diary dinta , sannan ta dawo gida cikin wani irin 'bacin rai ,cikin sarsarrafa ta shiga parlour'n, yau kam gabadaya a sama take jin kanta, kuma duk wanda yayi kok'arin shiga track dinta zai had'u da 'bacin rainta.

a daidai tsakiyar parlour'n suka ci karo da mahaifiyarta "ke kuma daga ina haka kika yi wani wujiga wujiga dake?
me'ad ta dan tsosa tsakiyar kanta batare da tace komai ba, "dake fa nake magana kina jina?, kinsa banason wannan fitar ta babu gaira babu dalili ko.
takarasa mgnr tana jan tsaki sannan tace "ina file din danace kin kawo min?

"uhmm ammmmm daman shi naje nema ,daxu da safe ko da direbanta ya kawo na shirya zanje injin ciro kudi sai na kar'ba na saka acikin diary dina ,amman narasa komai nawa ina tunani agurin bata kashin nan ya subuce acikin jakata ,"yanzu hk gurin na koma ko zangani amman .....sai tayi shiru ta kasa k'arasa maganarta sakamakon wani irin kallo da uwar ta jiho mata ....

"abinda kike kok'arin cewa baki gani ba, ko ba abinda zaki ce min kenan ba?

me'ad tayi saurin d'aga kanta "kinsan ko file menene kika yarda shi? "
file ne dake tattare da mahimman bayane akan kudad'en marayun ya'yanta, amman kalli yadda sakacinki yasa aka rasashi , keda zaki ajiye abu a gida amman kika fita dashi, nan fa suhailat tafiki kaifin baseera "am really sorry momy zanyi kokari na nemo.. " a ina zakigani?

" zan sake komawa gurin ko Allah zai sa nagani takarasa mgnr tana narke fuska alamun shagwaba.
"ke bar shi kawai zan sake tuntubarta ko tana da wani copy "thank you my mom .... hjy khadeeja ta shige d'akin mai gidan . Ranta babu dadi ta shiga d'akinta tana shiga ta fad'a saman gadonta ta kwanta flat tare da runtse idanunta

*******

Misalin karfe tara na dare ranar a  kwance da fu'ad yake ya ciro D'an karamin diary dinta brown me d'igon ruwan zinari, daya tsinta bayan rabuwarsu da me'ad ,yana kallonsa dagani kasan me tsada ne ,ahankali ya kai  diary din daidai saitin hancinsa yana shinshina, ni'imtaccen kamshin, Dior addict daya kama jikin diary sosai ,sai kawai yasamu kanshi da lumshe idanunsa tare da bud'esu duka atare cikin wani sabon alamari da ba zai iya kwatantawa ba, a lokacin fu'ad matashi ne Dan kimanin shekaru talati cif da haihuwa ,duk inda ake neman kyau ga d'a nmj fu'ad ya mallakeshi ,fari ne tass me dagon hanci da yawon suma me kyawawan idanu farare kal kuma manya masu cike da nagarta .

Cikin sand'a malik ya iso inda yake kwance ya fixge diary din yana dubawa yaga wasu mahimman file da ATM atsakiyarsa, fu'ad ya d'ago idanunsa ya kalleshi a matukar tsorace.

" uhmmmmm daman nasan ka fad'a tarkon son yarinyar nan ,amman kake wani son waskewa, shiyasa fa nace idan kana sonta ni na hakura nabar maka , kaje  ka nemi soyayyarta, amman ka tsaya wani jin kai ..."kana sonta ko ba hk ba abokina?

"Tsaki fuad yaja a d'an hassale sannan ya juya masa baya "kai dai ayi D'an matsala wallahi, kaje man  kayi introducing kanka agurinta Dan ni bata gabana .....

" shiyasa naga ka tsurawa diary dinta ido ba ,tare shakar kamshin turarenta? inji cewar malik yana me tuntsurewa da wata uwar dry.

Wani tsakin fu'ad yaja "kanka ake ji, ga diary din nan a hannunka  kayi duk abinda zakayi dashi ,sannan kayi kok'arin  ya isa gareta a duk sanda kaje gabatar mata da kanka ,ina maka fatan alkhairi  tare da samun  soyayyarta ...

"Dan Allah abokina, da gaske ,da gaske addu'ar samun nasara kamin? yakarasa mgnr yana me karasowa zuwa inda fu'ad ke kwance ya rike hannuwansa duka cikin nasa "na...gode  abokina amman tare zamuje gidansu tunda ga addresse dinta acikin diary..?

"a'a kaje kai kad'ai ,hallo dai ina maka fatan samun nasara akanta sannan ya meida  idanunsa ya runtse ya cire hannunwasa cikin na malik yana dafe goshinsa da hannunsa daya.

malik yayi saurin boye dryrsa sannan ya mike tamkar wanda akayiwa wanka da ruwan tsanyi ya isa makwancinsa "wannan shine karo na farko daya ganshi cikin damuwa hk, yammata dayawa suna kawo masa farmaki amman babu wace yaga tsan tsan damuwarsa akanta  kmr me'ad, ayau suka soma ganinta amman da dukkanin alamu ta tafi da zuciyar abokinsa, ya kwanta yana dryr muguntа,  domin a zahirin gsky shi ba son me'ad yake ba, amman ganin  fu'ad yana neman waskewa akan sonta, yasa shi son shiga rayuwarsa tunda daman sukanyiwa junansu hk shi dasu  kabeer , daga baya komai ya daidaita, Amman banda fu'ad da duk macen data kawo masa hari baya yarda ya amincewa soyayyarta ,acewarsa ba soyayya ce agabansa ba, yadda zai samu aikin da zai kula da kakarsa yake .

"itama bangaren me'ad kasa runtsawa tayi duk ta inda ta juya fu'ad  take gani acikin kwayar idanunta,wani irin canji take ji a gabadaya ilahirin jikinta, ahankali take jin feeling's na bijirowa gangar jikinta wanda wannan shine lokacin  na farko dataji hk ajikinta, domin duk yadda sajida ke bata labari akan yanayi makamancin hk, bata ta'ba yarda ba, ta d'auki lamarin amatsayin shirme, ashe ba shirme bane da gaske ne?" mutun kanji wannan yanayi ajikinsa idan ya had'u da abinda yake so...

kudundune jikinta guri daya tayi acikin bargonta, tana kok'arin basar da abinda take ji yana tafiya da bugun zuciyarta ,wanda  a zahirin gasky mamaki faruwar hkn ya soma kamata, a kallo daya komai ba neman birkice mata....... da kyar da taimakon bacci barawo tasamu tayi bacci.

Abu fa kmr wasa kullun me'ad sai fita zaga gari ko Allah zai sa ta had'u da fu'ad amman shiru ka keji ,har kusan  sati daya , tana garari agari. yadda take zariyar neman fu'ad, haka malik ke zariyar nemanta domin bata diary dinta dake d'auke dakatin ATM dinta ,da kyar ya samu shigowa cikin estate dinsu ya isa bakin tafkeken get din gidansu da'aka nuna masa, yasamu daya daga cikin masu gadi gidan bayan ya gaishesa ,me gadi ya amsa yana masa wani irin kallo sannan  yace" wa kake nema?

"dan Allah ina  neman me'ad.

Me gadin yayi shiru kawai yana duban malik daga samansa har kasa, ba dan yana da wata makusa ba ajikinsa, sai na talauci da babu daya nuna ajikinsa, me gadi ya sake maimaita tmbyr da malik yayi "kace kana neman me'ad ko me?

malik ya d'aga masa kai ala'mun eh.

"Ita me'ad din tasan da zuwanka ?

"Aa  amman idan kashiga kace  mata wanda suka had'u agurin injin din ci...

"Dakata anan da shirmenka, sannan ka juya ka 'bace daga gurin nan , daganika irin yan yunwan nan ne, jobless  marasa aikin yi," kaga yarinya yar babban gida shine ka lallabo ko? "oya maza ka 'bace tun kafin ita kanta tasan da zuwanka kasha dukan banza.

Batare  da mutsu ba  jiki a sabule malik ya bar unguwar tamkar wanda kwai ya fashewa acikin yana mamakin girman al'amarin, sai dai kullun zai zo amman baya samun ganinta hk zai juya ya koma da diary dinta , inda fu'ad ya d'auki zafi sosai  dashi "kana wahalar da kanka abanza daga karshe ka had'u da wulakaci .
"ka fahimceni fu'ad Allah ba wai .."dakata malam kaje kacigaba da bibiyarta rayuwarka ce, abinda zai min ciwo bai wuce naga ko naji kace an wulak'anta ka ba, yana karasa mgnr ya fice daga d'akin yana huci. Malik ya girgiza kansa ,tabbas ya fahimci irin son da abokinsa kewa me'ad amman ya dakewa zuciyarsa, shi zai yi iya kokarinsa yaga ya had'a ruhinsu  guri daya....

*******

Yau takama litinin wanda kowa yake sauri ya shirya ya samu halatar makaranta da wuri ,ko neman aiki da sauransu , ita kuwa me'ad tana gado tana juyin da tunanin fu'ad dinta ,har kafe tara sannan ta tashi tasa aka had'a mata ruwan,tayi wanka ,nan ma sai da ta'ba lokacin gurin tunaninsa ganin take kmr yana tare daita, duk inda ta juya shi take gani har mafarkinsa take, suna rayuwar aure tare.
ahankali ta fito daga bathoorom gurin shiryawa ma sai data bata tsawon lokaci ta fito ta karya sannan takama hanya dan zuwa bank domin amsar sabon ATM.

tun da ta cusa hancin motarta cikin harabar zenieth bank ta sauya yanayin tukinta tayi parking sai dai tajima acikin motar saboda ganin kmr mutane sun yi yawa kafin daga baya ta fito, tana taku ahankali da rangwad'a tashiga .

kai tsaye gurin costume's care ta nufa , somi itace wace jinisu ya had'u daita sosai, somi na ganin me'ad ta sakar mata murmushi tare da cewa"me'ad you are welcome hade da tmbayarta abinda ke tafe daita, cikin harshen tsadadden turancinta tasoma mata bayanin abinda tazo yi, hannunta ta zura karkashin table ta zaro wani file ta mika mata tare da nuna mata wani madaidaicin office da hannunta "ki shiga can ki cike sai kawo min.

"okay me'ad ta furta sannan ta amshi file din ,cikin mintuna kad'an ta cike ta fito "ta mika mata batare da 'bata lokaci ba akayi mata komai akace taje ATM ta canza pin dinta tare da mika mata envelop ,cike da rausaya ta nufi injin cire kudi bata wani canza pin dinta ba, ainhin pin dinta na da 5996 ta sake sakawa sannan ta kama gabanta wanda dayawa mutanen dake tsaye agurin hankalisu na kanta.

Yau ma kmr kullun tana fita malik yazo gidan sai dai me gadin bai bi ta kansa ba ,saboda kallon wani mahaukaci dayake masa har sanda ta sanyo hancin motarta, ana kok'arin bud'e mata get shi kuma yana kok'arin isa inda motarta take, sauran security suka dakatar dashi, dan wani har ya kai masa mari ya goce da sauri.

Me'ad ta bishi da wani irin kallon sani ,sannan ta kusa hancin motarta cikin gida tayi parking , ta fito tana gyara zaman glass din dake manne da idanunta ,ta kira daya daga cikin masu kula da bakin get "waye wancan mutumin da kuke dambe dashi kan sai ya iso gareni?
sai da obi yayi jim..
sannan yace "wai gurinki yazo yau akalla ya kai sati kenan yana zuwa " what? ta furta arazane sannan tace.

"how dare him yazo gurina akan wani dalili ?

"hk dai yace ranki ya dade.

"Karku  sake ku bashi damar sake shigowa estate din nan ballanata har ya iso bakin get din gidan"yes ma .

ta juya zuwa cikin gida  tana tunanin inda tasan fuska amman sam ta kasa tunawa.
obi ya juya cikin sauri ya isa ga malik yasoma  tura keyarsa "dan Allah ka saura ni abunta nazo kawo mata data yar bawani abu nazo nemana gurinta ba, amman ina sam obi yaki sauraransa har sai da kai ga  fitar dashi gbdy daga estate din.

*******

tafe suke ita da sajida a Shopprit domin  siyaya wa mahafinta dake jinyar hannunsa agida,kuma a yau din nan suke expecting dawowar abbansu me'ad daga kasar America wanda yaje cheek up , ahankali suke takawa kmr basu san taka k'asa me'ad na sake bawa sajida labarin fu'ad sannan suna daukar  duk wani abun amfanin daya kai su bayan sun gama sukaje inda ake biyan kudi me'ad ta bada ATM dinta, suna daf da fitowa suka had'u da Malik cikin saurin yake binsu yana kiran sunanta" me'ad me'ad!! me'ad ta juyo tana ganinsa tayi saurin kawar da fuskarta tacigaba da tafiya "kai kawata wannan mutumin fa ke yake kira.. ki tsaya mana da ala'mun yasanki "baki da hankali aganni na tsaya da wannan ai sai mutane su raina da ajina .

biyota malik yayi" dan Allah ki tsaya abunki zan baki. da sauri taja hannun sajida ,haba me'ad ki tsaya mana wulakanci bashi da amfani balle d'an adam daraja garesa "bawani abun fad'a anan kawata , wancan banza nema yake na kulashi ,ni km ina i can't suka shiga motarsu cikin sauri suka bar gurin kafin malik yakaraso.

"okay mubar zancesa cigaba da gaya min labarin kyawawa nan , ko shima kmr sauran samari gari yake ?
 birki taja sakamakon gitawar da wani me okada yayi ta gabanta.

ta Leko da kanta cikin bacin "kai ina zakaje kake sauri hk?
 " jiki da wata banzar mgn kisawa motarki alamar koya tuki Dan da alamun baki kware ba .

" kai koya min tuki zakayi ko me ?

"Kina bukatar hkn ai.

 "kutumar uban can... "kinga malama duk abinda za'a yi ayi  ammam ban da zagin iyaye yar rainin hankali kawai, ko dan kinganki cikin wannan kememiyar motar kike tunanin zaki zageni na kyaleki?

 sajida ce tayi masa alamun ya wuce kawai tare da cewa "kinga manta da wannan " kibani labarin kyakyawan saurayin nan da kuka had'u last week wallahi ina jin dadin yadda  kike fassalta shi, me'ad tayi shiru ta kasa cewa komai  ,kafin daga baya ta furta sunansa "fu'ad kenan ....

"suna me dadi tunda kike furta min sunasa naji sunan  har cikin raina inji cewar sajida "Allah ko ai sai ma kinganshi kawata hadadden gaye aji farko zance fu'ad suke har suka shigo harabar gidansu sajida inda suka iske motar gidansu me'ad"kai kinga da ala'mun dady Dina   ya sauka? Cikin sauri suka fito hannunwasu rike da farar laylon.

Da dariya suka shigo parlour ,n inda suka iske mahaifin sajida da nata zaune suna tautaunawa akan abinda ya faru " ai ina gaya maka Aliyu tabbas zakasamu  k'arin girma nan ba da jimawa ba akan wannan kokarin naka,mead takarasa kusa da mahaifinta ta rungumeshi "dady  sannu da zuwa.

"yauwa yar baba fatan kina Ify?

"ina Ify amman ba lau ba takarasa mgnr tana nufar mahaifin sajida "gashi uncle "ka gwada wannan kaji yana da dadi sosai .

" yar baba aliyu ya gaya min cewa tsalake rijiya kikeyi a wajen harbe harben da'akayi? batare data juyo ba tace "eh baba amman babu abinda yasameni ,uncle ka fa zama jarumi a gari "kalli can kagani ta nuna masa tv da yatsan hannuta, kowani gidan talbijan  kai suke nunawa tun daga last Week har yau din nan    sajida ta zauna kusa da mahaifinta tana gyara masa zaman bandage dake d'aure da hannunsa.

Mahaifin me'ad ya gyara zamansa tare da cewa " yar baba kawo min coffee mara madara "okay dad.

"uhm yar baba nima ki kawo min, me'ad ta nufi hanyar kitchen tana karasa shiga ta ja ta tsaya tana kiran "sajida ........

"na'am.

"a ina kika ajiye sugar?
takarasa mgnr tana kallon wasu jerin robobi dake ajiye a kitchen cabinet ,acp ya bata amsa daga zaune dayake " ai in dai wannan yar zaki tambaya ,to kuwa kin saba lamba.

sajida ta kaiwa babanta naushi a dayan hannunsa mara ciwo tana dry "kai baba  "kai baba ko gsky na fada? " ko sau daya bata ta'ba shiga kitchen din nan da sunan d'aura wani abu ba, bari nazo na d'auko miki yakarasa mgnr yana me mikewa tsaye "me'ad..... sajida takirata tana murmushi nima kizo min da coffee da k'arin sugar kinji kawata.

" hmmm yarinyar idan zaki koyi had'a shayi Da kanki ,   ki tsaya ki koya ko Dan aure da zakiyi watan gobe "ni imran din ma nake tausayi inji cewar acp "in tambayeki yar baba, waye wancen yaron dana samun labarin yana xuwa gurinki kullun bayan ga maganar safwan da'aka ajiye "uhmmmm wannan Shashan , ai kwana hudu data wuce na fara ganinsa ban san inda yasan ni ba amman har sunana ya sani abun tsoro .

"uhmmm?

" uhmmm uncle nifa abun ya fara damuna yau ma sai da muka had'u dashi a shopping, acp ya juya zai bar kitchen din fuskarsa da ala'mun rashin yarda "uncle kar ka fahimceni ba daidai ba "ai shikenan yar baba na fahimceki ....

********
tsaye suke su duka acikin had'ad'd'en boutique dake depomu wanda yakasance mallakin mahaifin kabeer ne .wasu yammata ne su biyu suka shigo cikin harabar gurin, kowace sanye da riga iya cinyarta wanda ke nuni da yare ne, makale da yar karamar jaka suna tautaunawa, kabeer dake tsaye kusa da malik yana dan kurban fiver alive "yace kumeless tare da binsu da wani shu'umin kallo malik yayi saurin juyawa shima ya bisu da kallo ,sannan ya juyo ya kalli fu'ad yana dage masa gira kana ya sake juyowa ga kabeer "idan kabiyi wad'an yammanta kai ka zasuyi su baro ,duk bugi ne wallahi ina gaya maka. "kai dan Allah banason shirme ka juya ka kalleshi da kyau gsky sun hadu inji cewar kabeer.

Malik ya sake juyowa ahankali yana kare musu kallon tsab sannan yace "uhmmmmm wad'an yammanta lagos din suna da tsabagen wayo tsiya ,su sha kwaliya su dinga maganganu irin na birgewa, amman duk fanko suke,ya dan sake kallon inda fu'ad yake sannan yacigaba "daya nagani acikinsu me nagarta da kamalar madarar kyau ...... sudais yayi saurin cewa "da gaske ?

"yace uhm.

"kallesu da kyau kagani duk kwaliya ce kawai "yanzu kayi kok'arin kallonsu batare da kwaliya ba kagani .

"kamar yaya kenan? inji cewar kabeer .

"ka aiyana da tunaninka mana ..
"kai dan Allah banason shashanci da ala'mun fa kwal'kwaluwarka tasoma samun matsala inji cewer kabee .
"kai ne dai mahaukaci amman ni nasan abinda nake duk da cewar akwai yammata dayawa amman me'ad dina ta zarce kowa yakarasa maganar yana ware hannunwansa duka..
"kaji mahaukaci suka kwashe da dry "matar da jiya jiyan nan tagama shuka maka rashin mutunci, wai har da wani cewa me'ad dinsa suka sake kwashe da dry suna nunashi .
fu'ad dake tsaye rungume da hannuwansa duka a kirji bai kulasu ba illa fuskantar kofar shigowar dayayi tare da takaicin malik, aiko tamkar a mafarki yaga shigowarta sanyi cikin doguwar rigar abaya har kasa ta nad'e kanta da mayafin abayar hannunta rike da karamar jaka saurin runtse idanunsa yayi yana cigaba da kallonta ahankali ya mutsutsuka idanunsa" itace ko kuwa wata ce me kama daita ,tabbatar da itace yasashi saurin waskewa alokacin da suka had'a ido daita itama kallonsa ta tsaya yi cike da matsanancin mamaki ta mutsumutsuke idanunta tagani ko shaukin sonshi ne yasata ganin hk oho.

muryarta a sanyaye tace "sajida ga fu'ad dina tare da nuna mashi, tsura masa ido sajida tayi, lokaci daya numfashinta ya nemi d'aukewa ganin halitar da bata ta'ba ganin irinta ba, tana ganin kyawun imran wanda zata aura amman na fu'ad ya zarta nashi,kad'an kad'an taoma jin tsigar jikinta na tashi abinda ta kasa fassalta ma'anarsa, wani irin sanyi soyayyarsa ne ya tsarga mata ya fara bin ilahirin jikinta, take ta lumshe idanunta zuciyarta na wani irin harbawa da sauri sauri, gbdy ta kasa d'auke idanunta akanshi har sanda ya juya musu baya.

shi kuwa malik na ganinta yasoma murmushin tamkar wanda akayiwa bushara da gidan aljanna sannan yace "kai kabeer sudais itace fa gata can yarinyar nan wallahi itace ..me'ad najin hk tayi saurin riko hannun sajida "kinga wanda na nuna miki?
"uhmm sajida ta iya cewa still idanunta na kan fu'ad "wance dake sanye da kaya shine fu'ad dina amman zo mubar nan yanzu yanzu saboda banason wancan mahaukacin ya dagula min lisafi ,sai yanzu na tina shi, ranar da muka hadu da fu'ad suna tare sai dai bansani ba taren suke ko kuwa anan suka had'u, wanda nake so daban shi kuma yana kokarin hanani rawar gaban hantsi .

"haba me'ad dan Allah ki tsaya naga fu'ad din da kyau shine dai sanye da riga pinky?
"eh shine amman mu wuce kawai...

da sauri malik ya biyo bayansu yana kiran sunanta "me'ad...jimana me'ad!! dan Allah ki tsaya ya kwaso aguje su kabeer suka biyosa" kai majinun ina zaka bayan gasu can, cangurin fa sukayi, ba itace me kaya ruwan d'aurawa ba?
"eh itace "mead dan Allah ki tsaya ita kuwa tafiya kawai take tana jan hannun sajida, "gsky fu'ad kyakkywa ne ajin farko amman me zai hana ki tsaya ki saurari wancan wata killa abokinsa ne fa.
"kinga da ala'mun magana yake son yi dake.

me'ad tayi mata banza sai janta take har suka shiga lift "ki daina turani mana, shi Wanda kike so ma bai san kina yi ba, ba gara ki tsayawa me binki ba, watakilla ma abokinsa ne ya taimaka ya janyo miki hankalinsa ,aguje malik ya biyosu yana ihun" jimana dan Allah ki tsaya minti daya abunki zan baki ta cikin lift sajida ta d'agowa fu'ad hannu wanda ya sake juyowa "sannu tana dariyar da za'a iya kiranta na farinciki "kibari mana sajida kina magana zai ta binki ne ya d'auka muma irinsa ne.ta fadi hkn ne a tunanita ko Malik sajida ta dagawa hannu, sajida tayi murmushi tana sake daga masa hannu.
" haba sajida meye hk ne? Karki manta fa watan gobe ne za'a yi bikinki.

"kinga bangane mgnrki ba nifa fu'ad nake d'agawa hannu ba wancan me bin namu ba "stop it sajida.. .." ki daina kallonsa dayawa da fa sadakin wani akanki "ki kyaleni nayita kallonsa tun yanzu kafin aurena bayan nayi auren shikenan... me'ad tayi shiru kawai takasa cewa komai har sanda lift ya tsaya suka fito da sauri me'ad janye da hannun sajida .
malik kuwa sai kokarin saukowa yake daga step domin ya iske su akasa .
yayinda fu'ad ke tsaye a inda suka barshe yana kallonsu batare da yayi yunkurin motsawa ba....

mmn sudais ce
[11/3, 8:26 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page 47 to 48

.....yana nan tsaye a gurin da suka barshi har sanda suka dawo suka samesa, malik ya dafa kafad'arsa yana fidda numfashi sama sama sannan yace "abokina kaga me'ad dina ko?" gsky yarinyar ta had'u iya had'uwa ,dan Allah abokin ka taimakeni ka tayani yakin shawo  kanta,dan zan iya rasa raina akanta yakarasa mgnr yana kwashewa da dry....

on expecting malik yaji sautin muryarsa " Allah yasa ka mutu yanzu in har sai na tayaka yakin neman amincewarta sannan ya juya yasoma takawa ahankali ya bar malik tsaye, sake da baki yana kallon bayansa sai dai fuskarsa kunshe da dry ..kana ya juyo yana fuskartata kabeer "kungani ko zargina fa yana neman tabbata fu'ad son yarinyar nan amman miskilancinsa ya hanashi fahimta, amman ni nan zansashi ya fahimci ya fad'a tarko dan bazan bari yarinyar ta subuce masa ba.." tabbas zanceka hk yake,yana sonta, itama yarinyar da ala'mun ta kamu da matsanancin sonshi inji cewar sudais.

kabeer ya numfasa kana yace "kar dai ku manta da halin fu'ad, tunda bai ce yana sonta ba ku yanzu meye naku a ciki ?balle kai malik da kabi ka hakikance akan yariyar , ka dai bi ahankali kar ka je ka jefa kan cikin wahala shi dai fu'ad bai aikeka ba har gara ma kayiwa kanka yaki neman au...shigowar wasu costumer's ne yasa kabeer katse zance yaso garesu tare da kiran daya daga cikin yan dake kula gurin..

bangarensu me'ad da sajida kuwa tunda suka shiga mota babu wanda yayi kokarin yin magana kowace da abinda zuciyarta take kismamata akan fu'ad, har suka karasa gida jiki a sanyaye suka shiga parlour'n inda suka iske hjy Khadija zaune tana kallon labarai "momy sannu da gida.

"sannunku yammatana har kun dawo ?
"ina siyayyar da kuka fita yi?

sajida ta zauna jagwab akan kujera tana fuskantar momy "me'ad ta hana mu yi taba amsa da hkn tana runtse idanunta.

"bangane hausar ta hana ba?

" nan sajida ta gaya komai amman banda sunan fu'ad. momy taja numfashi da ajiyar zuciya atare sannan ta dubi inda me'ad take tsaye tana cizan lip's dinta "karki soma janyowa kanki tashin hankali kinsa dai an gama maganar aurenki da safwan jiran dawowarsa kawai ake... tun da momy tasoma mgn tayi yunkurin barin gurin dan zuciyarta baxa iya saurararn maganganunta akan safwan ba, wanda a halin datake ciki yanxu ta manta dashi balle wani magana da'aka tsayar a tsakaninsu.

dare yayi sosai yanayin garin yayi sanyi baka jin sautin komai da sautin komai sai na iskar garin dake kad'awa ahankali yana bin jikin bil'adam ciki kuwa har dasu sajida da me'ad da idanunsu ke bud'e ,babu wani ala'mun bacci acikinsu juyi kawai suke akan gado suna tunani rai daya wato fu'ad, sosai sajida ke zurfafa tunaninta akansa sam bata tsamaci kyawunsa da nagartasa ta Kai yadda tagansa ba,a zahirin gasky bacin me'ad tasoma furta tana son fu'ad ba, da tsab zata rusa zance aurenta da emran ,tayi yakin neman soyayyarsa tare da  aurensa, amman kashi ....me'ad tayi mata tawayar da baxata iya kai kanta garesa ba ...... sam ranar sajida bata samu runtsawa ba, har gara ma me'ad ta runtsa da taimakon mafarkinsa daya kawo mata ziyara.
  abu fa kmr wasa kullun mee'ad ta kwanta sai tayi mafarki  fu'ad yana romacing dinta wani lokacin har saduwa daita, saboda zurfafa tunaninsa datake.

parlour'n gidan momy ta fito sanye cikin doguwar rigar har k'asa da madaidaicin hijab ,tana gyara zaman takardun dake rike a hannunta tare da kiran sunanta "mead..me'ad!!
ummi tayi saurin cewa "tana d'akinta bata fito ba tukun.
kai tsaye hanyar d'akin momy ta nufa tana cewa karfe takwas fa har tayi me'ad amman har yanzu kina kwance, koda tashiga d'akin kwance ta isketa akan gadonta kmr yadda tazata ,ta lullu'be jikinta da blanket me taushi , momy tak'araso har inda take kwance tare da zame bargon data lullu'ba dashi "me'ad  kitashi mana  karfe takwas fa tayi "uhmmmm momy bacci nake ji tayi mgnr tana mika ...ki d'aure ki tashi ....
 tashi zaune me'ad tayi idanunta a runtse "maza tashi mana  wannan fa shine  karo na biyu fa dana dana shigo tashinki bazan sake dawowa ba kin san dai kina da interview yau ko?
nima na shirya zuwa aiki momy ta juya abunta  idan kingama ga abincinki  can har ta kai bakin kofar taja ta tsaya tace "me'ad ...."na'am momy ya sunan yaron ?
da sauri ta bud'e idanunta sosai sannan tace sunan wa kenan momy ?
"sunan yaron  dakika jarabar so har kika kwana kina marfakinsa.

 runtse idanunta tayi ta sauko daga kan gadon zuwa kan doguwar ta kishingid'a ,sannan tace fu....... ad "uhmmmm idan na dawo mayi magana akanshi ,sai na dawo dan gsky na kusan makara ki hanzarta tashi.

goshinta ta dafe tana tunanin, "yanzu son fu'ad hk zai mata ?

ta dad'e zaune kafin daga baya ta mike tashiga wanka shap shap ta fito sanye cikin riga da siket na atamfar super exclusive me zanen fuluwa ja da baki a had'e wanda ya d'an kamata ajiki kad'an, kanta babu d'an kwali kasancewar bata fiyye son d'aurawa ba sai karamin bakin mayafi data yane kanta dashi ta fita cikin takunta na yanga da nuna ita yar wani ce ta shiga motarta oil and gas dake cikin apapa.

koda ta isa ta iske dubbanin mutane suna jira amman da zuwanta kiran waya kawai tayi sai gashi an bada umarnin tashigo kai tsaye batare da bata lokaci ba ta fito wanda fitowarta sai days bugar da zukatan tarin mazan dake zaune agurin ciki kuwa har da fu'ad dake tsaye rike da takardun neman aiki, zuciyarta taji tayi wani irin bugawa da karfi ahankali ta d'ago idanunta kmr ance ta waiga gefen hannunta na dama taganshi tsaye shi da wani da batasan kowaye ba, kallo daya tayi masa taji zuciyarta ta sake bugawa kmr yau ta fara ganinsa ,duk da bawai yau ta fara daura idanunta akanshi ba, sai dai kusancin na yau ya sha bambam da sauran lukuta wani irin kyakkyawan kallo take masa, yau gashi a gabanta ba daga nesa nesa ba, shima gabansa ne ya fad'i sakamakon ganinta dayayi a aininhin shigarta ta hausa fulani.

ahankali take daga kafafunta har zuwa office din alhj Ibrahim wanda yake shugaba ga maikatan kuma aminin mahaifinta, bayan sun gaisa ya tambayeta lafiyar mutanen gidansu, tace "duk lfy atakaice sannan akabata aiki wanda zata dinga daukar albashi me tsoka batare da wani interview ..kusan minti biyar tana zaune alhj ibrahim ya d'ago yana dubanta sannan yace "ko akwai wani abu ne, shiru tayi na minti biyu kana tace akwai "ina sauraronki ya fad'a tare da meida idanunsa kan tarin takardu dake gabansa "akwai wani danake son ka taimakawa kabashi aiki a ma'aikatar nan.

"yana ina?
" shine kika tsaya jan maganar abinda zaki fad'a da confidence ai ba mutun daya ba diyata ko mutun goma kike son a d'auka za'a d'auka masengen sa ta aika yaje ya shigo da fu'ad, wanda shigowarsa yayi daidai da tashin da alhj ibrahim yayi, yakaraso shigowa sanye da suit da bakin glass frada a idanunsa take office din ya gauraya da kamshin turarensa kafafunsa rufe cikin cover shoe baki ,taja masa kujera tana nuna masa gurin zama amman yaki zama "ka zauna zaka samu aiki karkashin jagorancina matukar shi kazo neman ,idan kuma kaki zaka karad'e garin nan batare da kasamu aiki ba saboda mu 'yan alfarma gama maganarta keda wuya ya juya kawai batare yace mata ko uffan ba, ta mike da sauri tabi bayansa tana kiran sunansa "fu'ad ka tsaya zan saka abaka aiki me mahimmaci .
amman ina ko juyowa baiyi ba har ya isa inda sudais ke tsaye yana jiransa ya rike hannunsa "zo mu wuce kawai ya iya furtawa "ka tsaya mana bakaji tana kiranka bane ?
kana ji fa taimakonmu zatayi "banason duk wani taimako daga gareta kazo muje kawai idan km baxaka ba na wuce.... ya fixge hannunsa cikin nasa "to bazani ba shekara nawa ina neman aikin bansamu ba yau zamu samu amman kake girman kan banza ...

fu'ad ba tsaya ba ballanatana ya juyo gareta yacigaba da tafiyarsa shi kuma sudais yakarasa

gareta "ranki ya dad'e kiyi hakuri hk halinsa yake, shegen girman kan tsiya shi ba... "dakata karka soma furta kalmar 'batanci garesa, daya tsaya har kAi zaka iya cin albarkansa tana karasa fad'ar hk ta juya fuuuuuu zuwa inda tayi parking din motarta ta figa aguje, mutane kuwa sai zagin fu'ad suke akan wasa da damarsa da yayi.

tana barin oil and gas  kai coffter coffe ta zarce inda suka saba had'uwa da sajida ,dukkaninsu shiru sukayi suna kallon junansu bayan labarin da me'ad tabata akan abinda ya faru atsakaninta da fu'ad. "me zai hana ki hakura dashi, tunda yaki saurararki.

"i can't sajida ina son shi  bansan ina son shi ba sai yau dana yi masa kallon gani ga shi, ni dai ki tayani adduar samun shi kawai dan matsawar ban auresa ba sai dai na mutu babu aure ..
"all the same inji cewar sajida "what?
"no babu komai suka cigaba da zance fu'ad batare da sun kai coffen da'aka kawo musu bakinsu ba tsawon lokaci suna zantawa sannan suka mike atare daga nan gidansu sajida suka nufa ,trafic ya kamasu suka tsaya inda malik shima yana d'ayan gefen hagu bai lura dasu ba sai danja tabasu damar wucewa sannan ya gansu, nan fa yashiga binsu akan lefan dinsa .

kmr ance sajida ta kalli mudubin gefenta ta hangosa yana daga musu hannu, leko da kanta tayi domim tabbatar dashi din ne "me ad duba madubin gefenki kiga wannan d'an jagaliyar fa mu yake bi  inji cewar sajida "kai dan Allah tayi mgnr tana dubawa ,"tabbas mu yake bi amman nasan yadda zanyi maganinsa k'ararsa zan kai gurin uncle ya jefa min shi cikin magark'ama ayi masa dukan tsiya haba dai ke kuwa kamar shi yace kar fu'ad yasoki takarasa mgnr tana dry a daidai lokacin da suka iso kofar gidansu sajida shims yaja ya tsaya tare da parking din mashin dinsa  suna fitowa daga cikin motar ya iso garesu yana cewa  jimana me'ad. nasan kinsani amman kike pretending kamar bakisani ba ...dau dau ta d'auke shi da mari "how dare you calling my name? yayi saurin dafe kuncinsa yana kallonta.

"me ma yasa kake bina? "kasan ko ni wacece?
"dan jagaliya irinka kake bibiyata "waye ubanka a duk fad'in garin nan ?

jiki a sanyaye yace" daman bawani abu bane amman idan baki tunani ba, ni ne malik wanda muka had'u agurin ciro kudi  ..

"and so what?
"jibeka  kawai wani wawa dashi ,ko iya fitar da maganar bai iya ba,da muka had'u sai akayi yaya?

"daman kin yar da diary dinki ne shine fa na amsa gurin abokina fu'ad dan nasan shi ba bazai ta'ba biyoki domin yabaki ba ,shi nake ta ajiyarsa  kullun ina son nabaki amman bakya saurarata..

"inna ilaihi wa inna ilaihi rajiun ta furta acikin zuciyarta  ...........idanunta a kansa

mmn sudais ce
[11/3, 8:26 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

page  49 to 50

....kallon kallo suka shiga yi atsakaninsu duka uku sajida me'ad malik, shiru me'ad tayi tana kallonsa batare da ta sake yunkurin cewa dashi komai ba ,sai dai gabadaya nadama tattare da kunyar abinda tayi masa a yanzu ya kamata tare da raunata wani shashi na gangar jikinta," ta wulakanta mafi kusanci ga zuciyarta bisa ga mummunar d'abi'arta...."me yasa tayi saurin marinsa?

"why why why!!! me'ad?

"why did you slap him..?

tana nan tsaye jikinta na rawa har malik yakaraso zuwa inda take tsaye jikinta nacigaba da kyarma ya miko mata diary dinta ......nadama ce fal dankare da zuciyarta "hakika ta cuci kanta ta cuci rayuwarta ba zata ta'ba yafewa kanta abinda ta aikata masa ba matsawar yayi silar rasa fu'ad dinta....."ki amsa ko nabawa kawarki ne?
jin sautin mgnrsa yasa tayi saurin dawowa cikin haiyacinta domin natsuwar tasoma barin gangar jikinta, kallo daya zaka mata kagane kalar damuwar datake ciki.
sai daya sake mgn sannan jiki a  sanyaye tasanya hannuta ta amshi diary dinta, shi kuma ya juya tamkar wanda kwai ya fashewa aciki yasoma tafiya , har ya kai gurin mashin dinsa yana shirin hawa yaji sautin muryarta ahankali "tsaya dan Allah sannan tasoma kok'arin takowa zuwa inda yake,  jikinta a matukar sanyaye .

muryarta na rawa tace "dan...dan girman Allah kayi hakuri ta furta hkn tana mai  runtse idanunta kasancewar wannan shine Karo na farko data bai wa wani  mutun hakuri ,bayan iyayenta da suka kawota duniya "kayi hakuri ta sake maimaita kalmar muryata a raunane tare da bud'e idanunta fess akansa tana kallon yanayinsa da gbdy ya sauya, a yanzu dayake gabanta ganin take tamkar fu'ad dinta ne tsaye a gabanta cikin matsanancin damuwa , "hakika nayi abinda bai dace ba ,da rashin kamata gareka,

tun ranar farko dana soma ganinka a gidanmu nayi tunanin kmr nasan fuskarka amman alokacin na kasa tuna inda nasanka, sannan lokacin dana ganka tare da fu'ad a boutiq shima ban tantance alakarku dashi ba amman dai kayi hkr dan Allah.

" babu komai ,komai ya wuce Allah ya kiyaye na gaba, hk daman rayuwar take ,da nabi shawarar fu'ad da ban jawo wa kaina wulakanci ba, domin babu abinda ya kai wulakanci kmr a tsinkaka ta hanyar mari..... ...amman babu komai "me'ad yakira sunanta ,nasan kina mutuwar son abokina fu'ad duba ga yanayin nadamarki bayan kinsa alakata dashi, amman shi mutun ne me matukar kamewa ,kai tsaye hk bazai ta'ba fuskantarki ba ....

"nasani ....nasan da haka amman ko zaka iya taimaka min plz takarasa mgnr muryarta na craking ?
domin zan iya yin komai akansa ,"da fari dai ka taimaka min da number wayarsa tare da sake bashi hakuri.
"sajida plz ki matso kusa mana ki bashi hakuri kema bawai ki wani ja kin tsaya kina kallonmu ba.

"me zance masa me'ad?

"me kike son nace masa after kingama aikata son ranki ?
"i think kin bashi hakurin kuma yace ya hakura.

"eh amman ni dai kice masa wani abu dan Allah har yanzu akwai damuwa a tattare da shi.
"dole kuwa kiga damuwa atare dashi me'ad , bashi ba koni kika karewa kallo zakiga ala'mun hk atare dani "ta yaya daga ambatar sunanki zaki maresa?
" tun ranar farko daya kira sunanki na gaya miki definitely wannan mutumin yasanki wani guri amman kika nuna min sam ba hk bane yanzu wa gari ya waya?

" komai sai kin saka zafin rai aciki, sosai sajida tayi mata fad'a ta inda take shiga bata nan take fita ba har sai da malik ya nuna abar zance ya isa hk "kuma har ga Allah komai ya wuce daga karshe ya karanto mata number fu'ad bayan tayi tsore, tace yabata nashi yabata sannan ya wuce .

" a she dai mutumin kirki ne nake masa wani irin kallo ta furta hkn tana kallon bayansa .. .......
juyawa sukayi zuwa cikin gidan suna shiga d'akin sajida tasoma neman layinsa amman kiran duniya tayi bai d'auka ba haka takarar da wunin ranar akan kiran layinsa bai d'auka ba.

shi kuwa malik a sanyaye ya karaso gida, duk da har cikin zuciyarsa yana jin abinda me'ad tayi masa ya wuce, amman gangar jikinsa takasa hakurin hk, ganin yanayinsa yasa sudais dake bawa kabeer labarin abinda ya faru a oil and gas a safiyar yau din nan ya karaso gurinsa yana tmbyrsa, shima kabeer yazo ya tsaya dayan gefensa "lafiyarka malik?
" me yasameka duk ka dawo wani iri hk? yayi masa tmbyr ajere. naunayen ajiyar zuciya ya sauke tare da gaya musu abinda ya faru har zuwa Number wayar fu'ad daya bata, dan basa

boyewa junansu komai, daga karshe yace "karsu sanarwa fu'ad saboda ya sha ja masa kunne da gargadin abinda zai je yazo .
abinda malik bai sani ba gbdy mgnrsa acikin kunnesa yayita,wanda take ran fu'ad ya 'baci zuciyarsa tazo har wuya tana tafarfasa sai dai ya kudirici aniyar zai ganar daita kurenta ta hanyar tarkonsa data fad'a .

sai gurin tara na dare me'ad ta sake gwada kiransa da dayan layinta, bugu biyu ya d'auka cikin dakakkiyar muryarsa duk da bai san ko number waye ba, "hello..... ji tayi tamkar an mata bushara da gidan aljanna ne dan dadi, lokacin dataji sautin muryarsa ta ratsa cikin dodon kunneta, tayi sallama cikin sanyayyiyar muryarta amadadin "hello din daya ce mata, ," daga can bangarensa yayi shiru kawai yana sauraran yaji ko waye duk da zuciyarsa ta soma gano masa ko wace saboda sautin muryar mace dayaji, ita km hucin Numashinsa dake fita ta cikin wayar ne yayi nasarar kashe mata ilahirin jikinta har yasa ta kasa mgn, jin shirun yayi yawa ne yasa shi cewa "waye  yake kok'arin shiga cikin lokacin hutuna?

murmushin fariciki tayi gefe daya kuma hawaye ya cika kwarnin idanunta sakamakon sake jin sautinsa a hassale , sai da ta sake kwantar da muryarta sosai sannan tace "me'ad ce.

"wace hk?

jin abinda yace ya sata mikewa zaune daga kwance datake "uhmm ammm dan Allah karka ce baka ganeni ba, gurin abokinka malik na amshi numberka ?

"kit taji ya katse kiran ta sake kiransa back bai d'auka ba daga karshe taji ya kashe wayar gbdy ranar dai kwanan zaune me'ad tayi ,duk inda ta juya fuskarsa take gani da komai nashi bata ta'ba tunanin zata fad'a tarkon d'a nmj irin hk ba. washegari bata tashi da wuri ba saboda rashin baccin dabata samu yi daren jiya ba. sai gurin 12 ta tashi tashiga wanka.
ta sake neman layinsa da wata number daban yana d'auka tace "barka dai me'ad ce take magana  ...kit taji ya katse kiran wani irin sarere tayi agurin ahankali tayi kasa ta zauna akan gadonta sai ga hawaye yasoma ciccikowa a idanunta ta tsurawa wayar ido tana kallo gani take kmr shine acikin wayar.

wani tunani tayi ,zuciyarta ke umartata data kira number malik, take batayi sanya a gwiwa ba tashiga neman layinsa, bayan ya ta sake bashi hakuri akan abinda ya faru sannan ta d'aura da damuwarta "hakuri yabata Inshaallahu zan masa mgn. "ok nagode sosai sai kaji kirana ta katse kiran shi km ya sauke idanunsa akan fu'ad dake tsaye yana shirin zuwa gurin inna kakarsa "fu'ad yakira sunansa.. ya d'ago kansa tare sauke kyawawan idanunsa akansa batare da yace komai ba "dan Allah saurari yarinyar nan  ,ka duba kaga yadda ta ajiye jin kanta, gadara takama da komai nata akanka  ...

"an so what?

"na aiketa ko nasata?

"kai nifa banida lokacinta yakarasa shirinsa tare da barin d'akin ..misalin karfe 11 :00 na dare kiranta yashigo cikin wayar malik ya d'auka dan lokacin idonsa biyu yana kallon ball tare da su kabeer fu'ad ne dai ke kwance har yasoma bacci ,gaisawa sukayi sama sama "dan Allah malik ka had'ani da fu'ad "ok ya mike tsaye yayinda su kabeer suka bishi da wani irin kallo har yakarasa inda fu'ad ke kwance ya manna wayar a tsaitin kunnenshi ,sautin muryarta yasashi bude idanunsa ahankali yana duban malik dayayi saurin had'e hannuwansa guri daya yana rokonsa daya saurarera. lumshe ido kawai yayi batare da yace komai ba yaji ta sake mgn "fu'ad... dan Allah kayi hakuri da kiran danayi adaidai lokacin nan dole ce tasa hk gbdy na kasa runtsawa.. lip's dinsa ya ciza da k'arfi kmr zai huda, sannan ya kamkame jikinsa guri daya sakamakon jin muryarta, kai bazai iya cigaba da sauraronta ba, saboda zai iya shiga wani yanayi a dalilin jin muryarta da kuma ya birkita masa lisafi idanunsa ya rufe gam yana kawar da tunaninta tare da tunanin hanyar da zai bi ya musguna kmr yadda ta wulakanta malik..... "ina son mu had'u da kai gobe a coster coffee domin akwai bayanai masu matukar mahimmanci danake son mu tautauna da kai "gud dama tasamu ya furta acikin zuciyarsa, wanda a zahirance cewa yayi "okay.
"nagode sai mun hadu gobe karfe biyar na yamma ya katse kiran batare daya tanka ba.

bai je kmr yadda ta bukata sai dai shi yana tabbacin taje tagama tsamanin ganinsa ta wuce sai bayan kwana biyu  malik ya matsa akan zance,sannan  suka had'u a coster coffee dake awolowo waya gabadaya ta rame fuskarta tayi fayat kallo daya zaka mata kasan bata cikin natsuwarta da hankalinta  tsawon minti talatin tana tsaye kmr ance ta juya taganshi sanye cikin riga green me adon pinky a gabanta, gashin kansa a gyare sai sheki yake" kallo kallo sukewa juna kafin daga bisani ya runtse idanunsa tare da zube hannuwansa duka cikin aljihun wandonsa muryata na rawa tace "ammmmm uhmmm sannu da zuwa gsky ka ..kayi kyau ..wannan ce  maganarki mafi tsada ?ya fad'a tare da meida idanunsa ya runtse .

"eh but  ta mika masa karamar flower ga wannan kai na kawowa ,dan girman allah ka amsa koda kuwa bazaka amshi tayin abinda nazo maka dashi ba.

a banzace ya kawar da flowers yasamu guri ya zauna yana juya mata baya zagayowa tayi ta zauna ta gabansa tana fuskantarsa "me zaka sha ice cream coffe ko shayi da madara?

"da kyar ya fizgo numfashi kmr zaiyi mgn sai kuma ya fasa .

Zuciyartace tayi tunanin watakilla zai bukaci coffee
Dan hk take tabawa masu kula da gurin umarnin akawo masa coffee  ta meida idanunta a kanshi tana satar kallonsa juyar da kanshi gefe yayi kmr baisan me takeyi ba tare da datse lip's dinsa    ....
 Ganin ta kasa d'auke idanu akansa yasashi yi mata wani irin kallon wanda yasa kirjinta bugawa da karfi, sannan ya d'auke kansa dan shi duniya babu wanda yake jin yana matukar so kmr ita,amman ji da kanta gadara takama da kudin mahaifinta tare da wulakacin abinda tayi malik yasa yake jin kaunarta  na neman riked'ewa ,a lokacin ji yake kmr ya tashi  ya bar gurin sai dai kafin yayi hk sai ya wulakantata, sun jima tare da yin shiru kowanensu zuciyarsa na saka  da

warwara, fuad yaji shirun yayi yawa har sanda maikacin gurin ya ajiye tire me d'auke da cups guda biyu ya juya siririn tsaki yaja batare daya kalleta ba " yana da kyau kiyi abinda ya kawoki domin duk lokutana atsare suke babu wata dakika da take a wajena dazata zo face tana cikin tsari don haka kiyi gaggawa sannan ki takaita wajen maganarki dan banason mutun mai surutu ko dogon magana dan hk ina sauraranki .

Me'ad tayi mugun tsaresa da idanunta tare da gyara zamanta tana saukar da numfashi" hakika so wani shu'umin abu ne wanda yake sarrafa duk wanda ya shigesa ,fu'ad da fari dai sunana me'ad kmr yadda na sanar maka a ranar farko da muka had'u muna zaune agarin nan tare da mahaifana ,ba sai na tsaya gaya maka waye mahaifina ba, kana ganinmu kasan muna da milloyoyin Kudi da bazasu lisafu ba sannan...."dakata dan Allah malama kafin ki cigaba da wad'an banzayen kalaman naki "jikeke ke wata jaruma ce ko me dakike zubo dogon bayanai hakan kmr agidan radio ?

kanta ta girgiza tare da cewa "aa.

"ok Kamata yayi ki yi magana me ma'ana da takaitawa kmr yadda na fad'a miki tun farko,
"Ko kin d'auka da hkn da kika soma zaki birgeni ne ?
"dan kin wani zo kina zancen dukiya, kin d'auka soyayya ce a ganin farko bari kiji ba wata soyayya irin haka kin siyo furi kin kawowa saurayi abu ko tsari babu sannan saurayin dasani minti kwanaki kalilan kika yi masa, ki kashe kudinki a wasu abu na kirki wata killa zaki iya samun lada..

Me'ad batayi musu ba tabishi da shu'umin kallo wanda ke bugar masa da zuciya sannan tayi wani irin murmushi duk abinda take bukatar nmj dashi, fu'ad ya tattara, aji kyau kamewa tare da sanin Ciwon kai shima ya juya ya kalleta wani irin shaukin sonta na dibarsa.
" a zahirin gsky maganar dakayi tasa ilahirin jikina yayi sanyi ...

" go straight to your point dan Allah malam.. tsura masa ido tayi gbdy ya d'aureta duk ta inda tayi tunaninsa ya zarta hkn cikin sanyi murya tace ".tun ranar farko dana d'aura idanuna akanka naji kamin, na dad'e ina tunani kmr bamu dace ba amman zaune da nake agabanka na tabbatar da babu nmj daya dace dani kmrka ,ka cancanta kazamo uban ya'yana shiyasa zanyi kok'arin domin naga na fayyace maka na kamo da matsanancin sonka, duk da nasan kaima hk ne dan na cika budurwar da dole nmj ya kalleni ya soni ,ba dan komai kodan kyawuna kudina da kuma tarin ilimi na, da iya kalamai duk da nasan a yanzu hk ka gama amincewa, amman zanso ka furta kanasona kmr yadda na furta maka, sannan ga sakon zuciyata danazo maka dashi takarasa mgnr cikin murya me sanyi ta mika masa wata karamar akwati , amman sam yaki amsa illa idanunsa daya tsura mata"ka amsa dan Allah ni fa sonka nake tsakani da Allah kuma a shirye nake dana aureka.. zan iya sadaukar da komai nawa akanka ciki kuwa har da rayuwata.

Fu'ad yaji gbdy dry ta kufce
Masa yayita dry abinda bai taba yi ba kenan dryr data bayyana hakorarnsa "ni kike so...?

" yes ofcourse dole nasan zakayi mamakin kamata na furta ina sonka, amman kayi la'akari da so ba karya bane ,kuma kagaggen abu ne tunda kan Annabi adamu (a.s) kaga kuwa babu mamaki dan nace ina sonka.

"Tabbas kin burgeni dan naga ala'mun kema jaruma ce da har kika iya kallon wad'an idanuwana kikace wai kina sona duk da kinsa ko acikin mafarki baxakiyi tunanin ni fu'ad zan amince da uzirinki ba,  yayi shiru tare mikewa  a fusace yasoma kok'arin barin gurin batare da ya amshi abinda ta miko masa ba da sauri tabiyo bayansa tana share gumin daya jikata mata fuska "ka tsaya dan Allah ko coffee din fa baka sha ba , tafiya yake tana biye dashi  tare da kokarin son magana  " yayi saurin daga mata hannu "karki dameni  da banzayen kalamanki, I thought tun farko nace banso mgn dayawa ko?  "Ummmm amman Dan girman allah ka tsaya ka saurareni bakasan yadda nake jin zuciyata .
" yi min shiru tare da d'auketa da wasu maruka har guda uku ajere sannan yace "wawiya kawai kinyi zaton a banza zaki samu soyayyarta ko? Har  da zuwa da shukun fure da akwatin zoben masoya, kina zaton zan amince da soyayarki ne saboda kina da kudi, iyayenki ma hk kisani wannan talakan daban yake da sauran talakoki koda nake talaka ina tabbar miki wutsiyar rakumi tayi nesa da kasa dan kije ki samu daidai dake mai kudi da duk abinda kike takama dashi .

"fu'ad ka mareni a bayyanar jama'a dan nace ina sonka?

"yes na mareki ko zaki rama ne?

girgiza masa kai tayi kawsi ala'mun a'a, "ok na d'auka tak'amarki zai sai ki rama dakikiya kawai yana gama karasa wannan mgnr ya juya kai tsaye bakin titi yaje yana tsaida me  adaidaita "kai zaka capitol road?

ta biyosa da sauri "kabari na rage maka hanya nima hanyar zanbi "kai me adaidai wuce abunka tare muke dashi batare da bata lokaci ba me adaidaita ya wuce ya sake saida wani nan ma ta hana tare da fito da id card din acp aliyu ta nuna masa kana kuskuren d'aukarsa sai dai ka iske kanka amagark'ama nan take ya wuce yana cewa "kan wani dalili aiko bazam jawowa kaina ba.
 tafiya  fu'ad yke tana binshi a baya tana rokonsa yazo ta rage masa hanya amman yaki saurarata har sukayi nisa da inda tayi parking din motarta

tsaida me okada yayi kawai kafin tasoma dogon bayaninta tuni me okada ya wuce hk jiki a sanyaye ta koma tashiga motarta cikin tsananin damuwa da bakin cikin abinda fuad yayi mata ta figa motar aguje ta nufi estate dinsu kai tsaye  tana wani irin mahaukacin gudu Wanda zai kayi mamaki matuka in idan akace macece take tuka wannan motar ta miliyoyin kudi ,wani irin sautin kidan soyaya ne ke tashi acikin motar tamkar zai tarwatsa motar.

Yayinda samarin dake zaune a layi masu ji da kansu kuma yayan masu kudi irinta sai binta suke da wani irin kallo cikin bakinciki domin duk isarka duk iyawarka da iya wankanka baka isa tayi ma koda kallon arziki bane ballanatana  kasanyawa ranka zata saurareka, hk ta ratsa har ta iso

makeken gate din daya lullube ilahirin gidan hon daya ,tayi duka mutun ukun dake kula da get din suka taso suna kokarin bud'e mata get tare da jero mata sannu da zuwa amman babu wanda ya isheta kallo balle har ta amsa gabadaya idanunta a rufe suke .

bayan tayi parking a inda aka tanada domin ajiye motocin ta fito jikinta a sabule still zuciyarta na mamaki tareda alajabin abinda fu'ad yayi mata wanda ko a mafarki bata taba expecting wani bil adama zaiyi mata ba da wannan tunani ta taka zuwa parlour mahaifiyarta, inda ta cusa kai tare da yin sallama aciki .

Momy ta d'ago tana dubanta kallo daya tayi mata tasan tana cikin damuwa amman sai ta ajiye hkn akan aikin data fara ne, yasanya yanayinta ya sauya cikin sakin fuska momy tace " duk gajiyar hk?

Naunayen ajiyar zuciya ta sauke batare datace komai ba illa kwanciya datayi akan kujera tace ".ganin nan dai momy kwata kwata bansa abinda ke damuna ba "allah ya kyauta momy tace kawai tare yin shiru kana ta sauke ajiyar zuciya momy tayi "ni kuwa me'ad ina son nayi wata tambaya . " kai momy zaki fara ko, kwana biyu kin barni nayi kiba amman yanzu zaki soma yi min zance safwan abinda kika san banason jin a halin yanzu....

Momy ta maso kusa daita tare da dafata "haba me'ad yanzu arayuwa babu wanda baya son cigaba ,idan kika aure safwan zaki samu cigaba arayuwarki da wata daraja ta Musamman..

"Kai momy meyasa zaki dinga yin irin wanna bayanan , ada kinsa duk duniya babu mutumin Dana fi muradin kasance dashi kmr sa, amman yanzu an wayi gari bana bukatar hk, momy kudi fa da kike ganinsu a yanzu nasan basa siyan kima daraja mutunci kwarjini soyayya ,dan hk momy ki daina irin wanna tunanin kiyi fatan na auri wanda zai bani farinciki ina son fuad ..... Duk da nasan takala ne tulis......kuma zan auresa duk da talau...

Subuhallahi karki sake ki karasa wannan kalmar domin fiyayen halita ma yanemi tsari da ita dole ina son kiyi aure wanda duniya take damawa dashi wanda shi da mahaifinsa, suka maza masu abin hannunsu kuma bazan so ki auri Wanda bai kai ubanki kudi ba, sai wanda yafi shi dan haka a kullun adduar da nake miki kenan, ki janye batun yaron nan tun mahaifinki bai ji ba, idan dad dinki zai amince da aurenki dashi ni meye nawa aciki ?duk yadda nake son kiji dadi a gidan safwan hk zan hakura amman da zaki yarda ki amince kwarya tabi kwarya atsakaninku dana ji dadi sannan ki shiry tarban safwan yana kan hanyar dawowa .

Me'ad ta ta'be baki aranta tana jin zata iya yaki da kowa akan fu'ad , ahankali ta mike ta nufi bangarenta inda ta iske ummi tana faman goge goge tayis din dake barandar .

Ummi tana ganinta ta mike da sauri tana cewa "aunty sannu da zuwa, tsaki me'ad taja a maimakon ta amsa mata tayi shigewarta ummi tacigaba da abinda take yi aranta tana mamaki yanda me'ad ta d'auki duniya da zafi hk, duk da tun kafin tazo duniya anyi wad'an da suka fita wulakanta mutane amman babu wanda aka taba nunawa aka ce yayi nasara, balle itama

tasanya ran wata rana zatayi nasara wannan girman kan nata ta sake ajiye numfashi tacigaba da aikinta.

mmn sudais ce
[11/3, 8:26 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

Page 51 to 52

.......kwance take akan makeken gadonta kiran italy tana kallon saman d'akinta ,sosai tayi zurfi cikin tunanin lamarinta da fu'ad tare da neman mafutar yadda zatayi, ahankali ta mike zaune ta koma gefen gadonta ta zauna tare da lullu'be kanta da hannuwanta duka sakamakon bugawar da zuciyarta keyi akansa ,tamabayoyi tashiga jerewa kanta d'aya byn d'aya "me yasa fu'ad yaki amincewa da tarin soyayyata garesa?"me yasa ya mareni akan nace ina sonshi? "Kodai Malik ya gaya masa abinda ya faru ne da hkn yazamo silar d'aukar fansa gareni ta hanyar disgani cikin bayanar nasi..."ga shan mari har uku ga rashin amincewa da soyayyata da bai yi ba... "yanzu ya zanyi da rayuwata ? Ta sake jehowa kanta tmby.
" ina bukatar fu'ad arayuwata kuma zanyi komai akansa domin naga na mallakesa. wani abu ne data samu yazo wa zuciyata shine sake jin fu'ad datayi ajikinta yana yawo cikin jinin jikinta, tayi saurin goge hawayen da suka cicciko a kwarnin idanunta ya kawowa kuncinta ziyara, tasa hannunta ta dango d'igan hawayen tana kallo "yau itace ke kuka akan nmj?"nmj ma d'an talakawa wanda ba kowa bane...mikewa tayi ta isa gaban dress mirror dinta ta tsaya tana karewa kanta kallo daga samanta har k'asa "meye tarasa ajikinta kyau ne ko me da har fu'ad yake mata kallon ita bakowa bace?
Ahankali take karewa cikar halitar da Allah yayi mata, tayi imani ko ita ta isa tasa fu'ad ya fuskanci lamarinta yasota fiyye da yadda take masa, sai alokacin ta lura da irin yadda gashin kanta data d'aure duk ya wargaje a saman kafad'unta adalilin tunaninsa ,hannuta ta kai kan wayarta tasoma neman layinsa, Amman yaki d'auka, kasa hakuri tayi tacigaba da kiransa har sai data yi masa kira yafi sau goma bai d'auka ba sannan ta nemi layin malik kira daya biyu malik ya d'auka, bayan sun gaisa tace "malik kuna tare da fu'ad ne ka had'ani dashi?
" a,a ina gurin kallon ball, na dai barshi tare dasu kabeer a gida.

"Okay idan bazaka damu ba zanyi maka wasu 'yan tambayoyi, amman ina bukatar jin gsky

daga bakinka ."uhmmm ina sauraranki?

"Ka ta'ba  gayawa fu'ad abubuwa da suka dinga faruwa atsakaninmu da kai har zuwa kan marin danayi maka?
sai daya ja naunayen ajiyar zuciya ya sauke da kyar sannan yace"alahakikanin gsky wasu Abubuwan yasani sai dai batu na mari bai sani ba, dan ban gaya masa ba, wani abu ne ya faru da har kikayi tmby?

"Nothing  ,Amman yanzu wani  irin taimako zaka min malik akan abokinka?"na maseefar kwadaituwa da aurensa, ina son shi  sosai kuma zan iya yin komai akansa matsawar zan sameshi, ka taimakawa rayuwata malik nasamu fu'ad, nayi maka alk'awarin zan maka komai ciki kuwa har da samammaka aiki a karkashin ikona tunda shi yaki amsa daga gareni ..?

Numfashi da ajiyar zuciya ya sauke atare kana yace "zaki iya mallakar zuciyar fu'ad cikin sauki dashi kansa gbdy, bisa dalilin abu daya da sauri ta katse Shi ta hanyar cewa"meye shi malik ka fad'a  meye shi zan iya yin komai akansa "meye zanyi fu'ad yasoni?

"Bawani abu bane daya wuce kyautatawa, fu'ad na matukar son kyautatawa ,da km kyautatawa wanda ya cancanta most especial mara shi,ina tabbatar miki matukar kika kasance daya daga cikin masu kula da kyautatawa zaki mallaki zuciyar fu'ad cikin sauki batare wata matsala ba, ni kaina ina miki sha,awar aurensa domin idan kika sameshi amatsayin miji ina me tabbatar miki zaki yi alfahari samun miji kmrsa "shikenan malik nagode sosai da shawararka, km InshaAllahu zanyi kok'arin naga na kasance cikin masu kyatatawa mutane, gobe karka  manta kasameni a oil and gas.

" InshaAllahu bazan  manta ba Na gode sosai Allah ya mallaka miki zuciyar fu'ad "ameen nima nagode da wannan adduar taka sai mun had'u goben ta katse kiran ta   koma gadonta ta zauna inda zuciyarta take bata umarnin me zai hana ta tura masa ko da sakon text message ne tunda yaki d'aukar wayarta hannuwanta duka tasa ta rike wayar tasoma rubutu sako  kmr hk.

_Assalamu alaikum ina fatan kana cikin koshin lfy, daman na turo maka wannan sakon ne domin na k'ara baka hakuri bisa ga kalamaina na d'azu danayi amfani dashi ,wanda sukayi silar 'bacin ranka har ka mari kyakyawar fuskar matarka, azahirin gsky naji babu dadin abinda kayi min ,sai dai tarin soyayyar danake maka ta hana rashin jin dadin nawa  tasiri  ,ina sonka fu'ad har bansan yadda zan misalta maka ba, ka daure ko ba yawa nima kasoni kwatankwacin yadda nake sonka I really sorry for what I did ..sai da safe daga mai sonka Me'ad Ediris  Takai_

Tana tura masa ta koma kan ganta, ta kwanta lamo tare da runtse idanunta bawai dan tana jin bacci ba, sai Dan shaukinsa dake dibarta ,gudundune jikinta tayi, lokacin da tunaninsa ya yawaita ajikinta dan har ta fara hango sunyi aure dashi da yadda yake sarrafata akan bed gurin aika mata da zafafan romancing dinsa masu birkita 'kwal'kwaluwa.

A kwancen dayake a d'akinsu sanye cikin  jallabiya fara sol hannunsa rike da wayarsa yana

brownsin sakonta yashigo ,amman bai bi ta kai ba yacigaba  da abinda yake, km ko bayan daya gama bai duba ba yayi kwanciyarsa, ranar dai me'ad bata samu ta runtsa ba duk inda ta juya fu'ad take ganin da hannunsa dake yawo a ilahirin jikinta .

Washegari tun 7:00 malik ya tashi yayi shirinsa ya iso oil and gas, sai dai bai  iske me'ad ba dan bata karaso ba tukun, yasamu guri ya zauna zaman jiranta, sai gurin takwas tashigo cikin hadaddiyar motarta kiran toyota Camry ta gabansa ta wuce amman bai ganta ba saboda ba'a cikin irin motocin daya saba ganinta ciki bane, bayan ta isa office dinta da kmr minti 2 tasa ayi kiransa,cikin wasu 'yan mintuna malik ya bayyana a office dinta cike da girmama ya gaisheta, ta amsa da kulawa sannan ta nuna masa gurin zama da hannunta kana ta bukaci takardunsa ,batare da 'bata lokaci ba ya mika mata, bayan ta duba ta mike tsaye "kabani minti 20 "ok badamuwa ranki ya dade. Kai tsaye office manager ta nufa domin neman alfarma.

Acikin awa daya kacal  malik yasamu aiki a ibadan karkashin kulawar me'ad amtsayin wanda zai dinga kula da ficen da shigen kud'ad'en  kasancewar accounting ya karanta

 Lokacin da wannan labarin yasameshi a zaunen dayake a office dinta, yayi matukar murna da farinciki, godiya ya dinga yi mata kmr zai mata sujada, aikin daya d'auki sama da shekaru biyar yana nema sai gashi yasamu acikin awa daya nigeria kenan kayi karatun kagama sai kana da hanyar zaka samu aikiyi..

"Kabar min godiya hk nan ,ka godewa Allah daya nufeka dasamu, sai dai shawarar da zan baka ,ba wuce  ka rike aikinka da mahimmanci ba ,domin mutane dayawa irinka na can suna nema kasa danaka basu samu ba , sai abu nagaba ka taimaka min nasamu fu'ad.....

"Angama ranki ya dad'e InshaAllahu zanyi iyakacin kok'arina akan lamari, "ok ranar Monday zaka soma aikinka yanzu zakayi dropping account number dinka, akwai wasu kudin daza'a tura maka domin siyan sutura.
 "Nagode nagode!!!   ranki dad'e wallahi har bansan irin godiyar da zan miki ba ,hk suka rabu malik na farinciki samun aiki ita km tana murnar zata samu fu'ad cikin sauki tasan idan yaji itace tasammansa aiki zaiyi farinciki wata killa adalilin hk burinta ya cika.

Koda malik ya jewa fu'ad da labarin samun aikinsa ta hanyar me'ad, yace "tayi kokari sosai, sai dai kajira ranar zuwan wulakanci daga gareta, domin wannan aikin daka amsa daga hannunta daidai yake da ka amsarwa kanka wulakanci ne da damuwa, ni dai babu ruwa duk abinda yaje ya dawo sai dai ya kare akanka.

"Wace irin magana ce hk fu'ad?
" gskyar lamarin nagaya maka sai kayi taka tsantsan "Naji ni dai ka min addu'a shi nafi bukata daga gareka bawani dogon  sharhi ba ,sai agame  da zance me'ad , yarinyar nan ta damu da lamarinka dayawa , ka duba kagani kyau ilimi nasaba duk tana da, uwa uba gata da zuciyar taimako "ai ta taimaka maka dole ka fad'I  hk mana , ni dai  ina umartarka ka takaita maganarta anan  dan kadameni da zance ina da abubuwan yi.

Malik  yayi dry sannan yace "ni da zakabi shawarata da ka amince ka aureta komai cikin sauki zaka samu aikin ma dake bulayin nema ba sai kaje ba, kana daga kwance za'a yi maka komai."to baza'a d'auki shawarar taka ba ,idan ka damu da lamarinta har hk ka aureta mana ,ai daman kana sonta.
"Ina sonta bata sona kai take so, da kace ni ta nuna tana  sona wallahi ina tabbatar maka babu abinda zai hanani aurenta,"yanzu ma zaka iya gwada sa'arka yana karasa fad'ar hk ya wuce ya bar malik tsaye yana kallon bayansa.

*********
Duk abinda me'ad zatayi domin shawo kan fu'ad tayi, tabi abokansa da duk wani wanda tasan suna muamula, duk inda tasan zata ganshi kafafunta na gurin amman ko kallo arziki bata isheshi ba ,asalima yana ganinta zai bar gurin yakama gabansa, acikin tsakankanin wannan lokacin ne labarin rashin Ifyrsa ta risketa, bata tsaya sanya a gwiwa ba ta nemi malik da yayi mata rakiya, shine yayi mata jagora har gidansu inda ta tsaya kallon ruba'b'ben gidan dake shirin zubowa "kace na ne gidansu malik?
"Kwarai kuwa nan ne gidansu  "kina mamaki ne?
Shiru tayi batare datace masa  komai ba illa tsurawa gidan idanu datayi "yanzu anan fu'ad dinta ke rayuwa tun tasowarsa? A she fili tayi  zance batasani ba ,
"Ki daina mamaki ranki ya dad'e nan  ne gidansu kuma inda yayi rayuwa acikinsa idan kin mutsu ne mushiga Kigani d'aki na d'aya na biyu nan ne d'akin kakarsa.

Tana gama sauraransa ta juya ahankali Jikinta matukar a sanyaye tashiga cikin parlour gidan me cike da duhun tsiya ,hannunta rike da karamar jakarta da kyar take ganin inda take sanya kafafunta duk rana ce ba dare ba ,yayinda malik ke biye daita da manya manya fararen lododi guda biyu ,taja ta tsaya abakin kofar shi km malik yayi sallama tare da kutsa kanshi cikin d'akin sannan itama tayi sallama tashiga "a'a Malik kai ne hk da rana tsaka  ?"to marhabun  lale  ku karaso ciki mana inna  ta fad'i hk  tana mai mikewa ta shimfid'awa me'ad dadduma  ,Dan  shi Malik  tuni ya ajiye lododin hannunsa  yakarasa inda fu'ad yake.
Duk wanda yasan d'aki marasa shi hk d'akin yake bawani shararrun kaya ne acikinsa ba illa wani D'an madaidaicin gadon, sai kayan miyar dake ajiye gefe guda mai nuna alamun na siyarwa ne, gefe daya km wata katuwar akwati ce ajiye kallo daya tayi wa d'akin tasan d'akin marasa shi ne kmr yadda gidan yake sai da ga dukkanin Alamu yana samun kulawa ta hanyar gyara da tsaftaceceshi .
 cikin ladabi tamkar ba ita ba, ta durkusa har kasa kanta  a sunkuye cikin sanyi murya"inna barkanmu da warhk  ya gida da me jiki.. inna ta amsa cikin sakin fuska da kulawa batare datayi tunanin inda tasanta ba saboda ganinta tare da Malik .
 ahankali me'ad ta juya inda fu'ad ke zaune Wanda  ke aikawa malik da uwar harara  sanye cikin gajeren wando da T shirt fara sol gashin jikinsa kwance luf Luf tmkr na jarirai ,ta gaida uban gayyan da ko kallon inda take bai yi ba " ina yini ya jikin ? abunda me'ad ta fad'a Kenan taja bakinta tayi shiru.
ya d'an d'ago kad'an yace Ify atakaice shima dan inna tayi masa ala'mun da kafarta ne ,me'ad ta sake yin wani kayataccen murmushi sannan tayi shr.

Malik yayi gyaran murya sannan yace "inna ga surakarki budurwar fu'ad tazo duba lfyrsa ..inna tayi dry "kace kishiya ce shine har da bata gurin zama ,shi kuma jairin sai wani cika yake yana batsewa kmr ba yanzu nagama fama dashi gurin shan magani. Me'ad ta sunkuyar da kanta alamun kunya .malik yace " har yanzu fu'ad bai bar gudun magani? " ina fa har tsoron rashin lafiyarsa nake saboda  hkn.

Mead ta dago  da niyyar ta saci kallonsa ,karaf suka had'a idanu atake kirjinsu ya buga, tayi saurin d'auke idanunta Dan bazata iya cigaba da kallon surar jikinsa inna na gurin, sai dai muryarta a sanyaye tace "inna me yasa aka barshi a gida ba'a kai shi hospital ?
"Wannan za'a kai hospital inna ta nuna fu'ad daya yatsina fuska alamun damuwa inna tacigaba "mutumin dake gudun magani balle allura idan kika ganshi kuzarin jiki kawai garesa amman laulauyi garesa sai ki kishirya, murmushin jin dadi  mead tayi ganin tasamu karbuwa agurin inna .
sun jima shr sannan inna    ta mike tayi waje ,shima malik yace "bari nabawa masoya guri, tsaki fu'ad yayi batare daya tanka masa ba .
Yana fita fu'ad ya gyara zamansa cikin rashin jin dadi fitar da inna da Malik sukayi dan ba'a son ransa ba, dan babu  yadda zaiyi ne.
 me'ad ta matso zuwa inda yake ta tsuguna tare da cewa  "fu'ad...
Sam bai kalli inda take ba hasalima cigaba da danna wayarsa dake rike a hannunsa yayi, tayi kusan minti uku sannan tayi kokari kai hannunta da zumar Kwace wayar hannunsa ya kallota a fusace tana dakatar daita  da manya idanunsa  domin bayason kusancinsu a yadda yake Dan shi kadai yasan abinda tafiya acikin jikinsa tsawon minti 2 yana tsare daita da manya idanunsa kafin daga baya yasoma mgn kasa kasa "karki wahalar da kanki da   wata banzar kalmarki ko gaya min uzirin abinda ya kawoki,domin   ina tabbatar miki sam banyi murna ganinki kusa da innata ba  ,ni a bangarena bai zama lallai dole sai na soki ba ko yin wata muamula dake ba, dan haka ki daina wani rawar kafa dan sam ba birgeni zakiyi ba, dani bakowace mace ce zata iya yaudareni ba ..

me'ad datayi masa kuri da idanunta tana kallonsa ta saukar da numfashi tace" na jinka fu'ad sai dai abinda nake son kasani tunda nice naganka kuma na aminta da kai, zan iya d'aukar komai tare da shanye duk wasu kalamanka gareni sannan zanyi komai dan ganin na mallakeka amatsayin uban ya'yana koda dukiyata zatakare da numfashina..

wani irin kallon banza  fu'ad yayi mata irin na sama da kasan din nan sannan yace "iska na wahalar da mai kayan kara .

"Ina tabbatar maka wannan iskar bazata wahalar da mai kayan kara ba ,domin zamu kasance cikin inuwa daya koma nace bargo daya . tana gama wannan mgn ta juya cikin fushi tayi ficewarta shi kuwa fuad daya bita da kallo ya saukar da numfashi cikin sanyin jiki ya mike daga inda yake zuciyarsa cike da tunaninta  tabbas tana  matukar burgeshi muttaka, har yana jin idan bai sameta ba komai zai iya faruwa dashi .
bayan tafiyarta tashi yayi ya sake yin wanka yasanya kananan kaya  marasa nauyi ya tsaya fesa turare inna tashigo hannunta rike da bakar leda mai dauke da ruwan roba da Malta Amman

taga wayam babu yarinyar dazu babu alamunta cikin sauri tace " kai fu'ad ina yarinyar da malik? Kafadunsa ya daga mata alamun bai sani ba sannan yasanya kai yayi waje inda machin dinsa ke parke.

tuki take cikin 'bacin rai tana ciza yatsan hannuta gbdy ta kagara taje gida domin ta samawar kanta mafuta akan lamarinta da fuad wani irin taka birki tayi dan karfi gudun kada ta buge abinda tagani a gabanta.

a matukar fusace ta fito daga cikin motarta tayo waje inda tsohuwar take tattakawa ahankali saboda tsufa datayi Dan har ta d'an rankwafa "haba matar nan wannan, wani irin mugunta ce hk wato ke kin gama cin kuruciyarki A cikin tsiya shine zaki ja min masifa wato idan na bugeki kika mutu a kamani ko? to in har hk kike nufi ki sani idan na bugeki na kad'e banza dan dake da kuda daya ne agurina dan hk ki matsa kafin nabi ta kanki da mota..

tsohuwar ta d'ago da kyar ta kyalleta tace yarinya kiyi ahankali ahankali domin an yi wasu kafin ke kuma basu ta'ba cin riba ba kinga kema baxaki ciki riba.

me'ad taji wani irin 'bacin rai ya turnukota sai dai lokaci daya shawarar da malik yabata ya fad'o mata "fu'ad na matukar son kyautatawa da kyautatawa marashi kenan irin wannan kyautatawa yake nufi?
"bugu da kari mgnr tsohuwar ta kashe mata jiki murus,Dan HK tasoma nadamar abinda ta aikata da farko ta matso sosai kusa tsohuwar tare da rage sautin murya kasa sosai"inna dan girman Allah kiyi hkr nayi nadamar abinda na aika miki, ni kaina bansa abinda yasa wani lokacin nake reacting hk ba, amman kiyi hkr idan magana ta 'bata miki ,muje na tsalakar dake ta kai hannu zata ta'ba tsohuwar tace "dama kin bar shi yar nan zan iya tsallakawa, sai dai naji dadi da kikayi saurin gane kuskuren abinda kikayi ,ita duniyar ma guda nawa take?" ku dunga d'auka da mai kudi da talaka duk abu daya, saboda Allah da yayi mai kudi shi yayi talaka ba kuma dan baya son shi ba.

"Haka ne inna na gode sosai amman kiyi hkr kibarni na taimaka miki tayi saurin komawa cikin motarta ta kirgo kudi wanda zasu kai kimanin dubu goma ta dawo inda tsohuwar take ta riko hannuta tasanya mata kudin "inna ki amshi wannan dan Allah karki aa"kai yar nan har da wata hidima to nagode kwarai da gaske Allah yayi albarka, Allah yayi miki abinda kike so Inshaallahu zaki gama da duniya lafiya. "Ameen inna na gode.

fu'ad da fitowarsa kensn abun ya faru akan idanunsa duk da bai ji tautaunawarsu ba ,Amman ya ji dadin taimakon datayiwa matar har sanda ta tsallakar daita dayan bangaren tsohuwar na dariya tare da d'aga mata hannu ta koma tashiga cikin motar ta figa a guje yana kallon sannan ya taka mashin dinsa yacigaba da binta abaya batare da tasani ba ,har inda ta sake tsayawa saboda hango wata makauniya rike da yar jagoranta wace bazata wuce kamin shekara takwas ba ta mika musu sadakar dubu daya bayan ta tsaya sun tsallaka abu kmr wasa hk ta dinga taimako mutane wanda abin yacikasa da mamski "daman tana da zuciya irin hk me kyau ?"gsky idan har tana da irin wannan halin na taimakawa marasa karfi ta cancanta tazamo abokiyar

rayuwarsa, adaidai jection din bankole suka rabu shi yayi titi dopemu road ita kuma kai tsaye gida ta nufa inda ta iske sunyi bakin da suka dade suna expecting zuwansa, wato safwan almustapha maitama daga kasar hollond, mahaifin safwan baban mutun ne a kashen duniya gbdy ,sannan me gidan mahaifin me'ad ne a can baya kafin yayi rites . Safwan ya dawo daga kasar Holland ne da niyyar abubuwa guda biyu, na farko cima burin auren mead daya kwalafawa ransa tun shekarun baya, sai abu na biyu cigaba aikinsa amatsayin shugaban shashi na kasuwancin Nigeria.

jin ana jera mata sannu ne yasa mom dinta yin saurin fitowa dan tayiwa yar tata gargadi kada ta kawo musu wargi .
me'ad ta kalli uwar cike da mamaki "ni wai momy meyasa kike min hk ne?" narigada na gaya miki na canza mind dina akansa yaje gaba ya auri matarsa ni matar fu' ... momy tayi saurin rufe mata baki "karki sake me'ad kiyi ganganci, karkiyi wasa da damarki,domin damar mutun sau daya take zuwa masa arayuwa, ina shawartaki karki bari taki ta subuce miki.
me'ad tayi wani irin murmushin sannan tace, karki damu momy da subucewar wannan damar ni dai fu'ad nake so simple as that tana gama fad'ar hk tashiga cikin parlour'n mahaifinta wanda sai bakinsa masu mahimmanci yake tara acikinsa ,ta samu gefe daya ta zauna "dad sannu da zuwa ya hanya ?

mahaifin safwan ya amsa da kulawa sannan ta waiga inda safwan wanda tun shigowarta idanunsa ke kanta yana kallonta saboda wani irin azababben kyau dayaga takarayi masa sai dai ta rame kad'an Wanda bai San dalilin faruwar hkn ba ,sautin muryarta ce ta dawo dashi "yaya ina yini?

ya lumshe idanunsa na second biyu sannan ya bud'esu fess akanta kanwata kin yini Ify?
tayi masa wani irin kallo mai bugar da zuciya sannan tace Ify atakaice.

sun jima a parlour'n dad dinta ya dubeta yace ki kai yayan naki lambu ya huta mana , babu mutsu me'ad ta mike shima yabi bayanta cikin matsananci farinciki yayinda ita kuma ba'a son ranta ba Dan dai babu yadda zatayi ne.

wani parlour'n ta kai shi al wanda duk gidansu babu irinsa an maserfar zuba abun duniya agurin ,an zuva komai wanda me rai yake burin mallaka.

bayan ya zauna tasa aka gabatar masa da abubuwa sha kmr yadda tasaba sannan ta sake tashigowa batare da wani abu ba ta zauna shiru batace masa komai ba gbdy sai yaji baya bukatar cin komai dake gabansa illa matsowa da yaayi ya saita bakinsa daidai kunneta "ina sonki mead dayawa amman banji dadin yanayin dana ganki ba at least kinsa ina bukatar kulawa daga gareki. .tace har da gaske kana sona har yanzu ka mayar da akalar soyayyata ga wata in har kana son farincikina .
A matukar firgice ya tsura mata ido yana kallonta Kafin daga baya yace "no no hkn ba zai yuwuba "saboda me ?"saboda bana sonka yanzu sannan karka kazamanto me yawan wahalar da kanka wajen sake tadda zance aurenmu domin ahalin yanzu zuciyata bata gareka , ta

kamu da soyayyar waninka ,da sauri safwan ya kalleta cike da matsanancin mamaki abinda take fad'a masa yayi shiru ya kasa cewa komai illa jikinsa dake rawa..

"kaji abinda nace amman har yanzu ka kasa Cewa komai, ko magnata ta kurmanta da kai ne?
. "ko daya kawai mamaki kikabani shin kin manta matsayina a gidan nan dama duniya gbdy?

"sam maganganunki a yau babu girmamawa balle nuna tarbiya, "dan Allah ki gyara maganarki sam banji dadin yadda kika min ba saboda har yanzu ina sonki me'ad kuma banga abinda zai hanani aurenki ba matukar ina raye.
da sauri me'ad ta kalleshi cikin mamaki tayi wata dry na rainin hnkl " amman baka kyautawa xuciyarka ba sannan bakayi tunani me kyau ba, karkayi takamar dan mahaifinka me gidan mahaifina ne bazai sa nagaya maka abinda ke cikin zuciyata ba, idan kuma kayi kuskuren aurena girmamawa zai yi wahala ka samu romon da maxa dayawa in sunyi aure suke samu ba sai nagaya maka ba dan nasan kaima agidanku akwai irina safwan kake ko wa kake ;? ina son nagaya maka wallahi ban ta'bawa yiwa kowani mahaluki karya ba ko shi waye to kaima bazan ma karya ba, safwan har ka aureni bazan maka biyyaya aure ba sannan bazakayi min kulle ba, duk abinda nake so shi zanyi agidanka,kuma ba lallai ne na dinga maka girki ba idan taka ma har Wanda nake so sai na kawoshi gidanka kuma nayi duk abinda nake so dashi ,idan har kaga zaka iya to kana iya turo a karasa mgnr aurenmu da kai ,idan km ka janye niyyar aurenka akaina sai mucigaba da muntuncinmu , tayi shiru tare da mikewa tayi hanyar kofa, har ta zira kafarta daya a kofar parlou'n sannan ta tsaya batare data jiyo ba tace zaka iya fitowa ka tafi tunda na sallameka ..

tana gama fadar hk ta juya shi kum safwan da bita da kallo sannan ya saukar da numfashi ckin sanyi jiki ya tashi ya nufin parlour'n zuciyarsa cike da tunaninta tabbas yasan yana son me'ad so kuwa me tsanani har yana ji aransa matukar bai aureta ba tabbas akwai Matsala dan wannan abun datayi masa mugun burgeshi tayi shifa bai ga dalilin da zai bar wani me'ad dinsa ba alhalin yana raye bai mutu ba ,babu wannan nmj a duniya kuma kowaye sai ya nemoshi da karfinsa da dukiyarsa .

ita kuwa me'ad byn tafiyarsu ta shige part dinta ta sake wanka tasanya kaya marsa nauyi sannan ta fito paloun mom dake zaune ita kadai tana kallon labarai a CNN jin takun me'ad tana saukowa daga step " momy kallon kike ke kad'ai a parlour'n ina suhailat ?

momy tayi dry ai daman yanzu zan kiraki dan ina son naji yadda kuka yi da safwan.

me'ad tayi saurin kallon momy tace "waye km hk an?
da sauri momy tayi saurin kallo me'ad cikin mamaki da tsoro, cike da in ina momy tace " me'ad me ye nufinki?

batare da ta kalli momy ba tace "nufina bawai wuce ya nemi wata ya aura ba danni har abada ta fu'..

"yi min shr me'ad kada ki meidamu kanana mutane tare da meida hannun agogo baya dan wallahi tallahi baki isa ba  a wannan karon mune muka haifeki dole muyi duk yadda muke so dake wallahi baki isa kiyi mana mugunta ba dan hk ki meida hankalinki cikin jikinki tun kafin mahaifinki yaji .

"momy kingama ?

me'ad ta fad'a batare data kalleta ba, bata jira abinda momy  zata ce tacigaba "mom ni babu ruwana da  dady yasani  dan nafi son hk, kowa fa takasan yake yi yanzu dan hk baxaku matsamin ba, dan kawai kun kawoni duniya,  ku dai yi hkr  zanyi shawara da zuciyata idan na rarrashita akan fu'ad taji zata iya rabuwa dashi fine then zan iya auren safwan ,amman idan taki hakura sai dai kuyi hakuri, duk yadda nayi da zuciyata zan gaya muku tana gama fadar hk ta mike zata fita momy itama ta mike cikin bacin  rai da fushi ta riko hannunta har sai datayi kara.

"momy cire min hannuna zakiyi dan kawai banason safwan ?

momy dataga ala'mun fa yarinyarta tayi zurfi sai ta kwantar da murya "kiyi hkr me'ad ki zauna muyi mgn nasan zaki fahimci mamanki.

me'ad ta kurawa momy ido tana saukar da numfashi momy "kema kiyi hkr ki barni da zabin raina  sannan mgnr da zamuyi  ,mayi idan na tashi daga bacci tana karasa fadar hk ta mke ta koma samanta momy tabita da kallo cikin takaicin domin ita kad'ai tasan bala'in daza'a yi idan mahaifinta yasan tana soyayya da talaka abunda shi ya tsana kenan had'a hanya da talaka arayuwarsa .

me'ad kuwa gadonta ta haye tayi kwancinyarta tare da rufe idanunta fu'ad fess take gani acikin idanunta har ga Allah wani irin so take masa me tsuma zuciya da wuyar bari  ..hk tayita tunaninsa har bacci ya dauketa bayan ta tashi momy tashigo d'akin tayita rarrashita  amman furrr taki yarda da zabin iyayenta "momy tun farko banason safwan ke dady kuka matsa min ,ta yaya yanzu nasamu wanda nake ku nemi hanani aurensa.

"Ba hanaki aurensa mukayi ba ki tuna alkwarin dake tsakani Dan allah yarinyata ki duba lamarin nan "momy kema uwa ce nasan kinsa abinda ake kira da soyayya tunda nasan ba hadaku akayi da dady ba, ku kuka ga junanku ,ina rokonkanki momy ku barni da fu'ad wallahi akansa zaku iya rasa takarasa mgnr tana kuka . ..tsakanin uwa da 'ya tuni itama ta sauko taji zabin diyarta yayi mata, zata bata damar ta auri zabin zuciyarta..

Ranar da kyar safwan ya runtsa kwana yayi yana zubawa cikinsa giya da tunanin abun yi, "tabbas yakamata ya d'auki mataki nemo kowaye ke kokari kawo rayuwarsa nakaso ,tun da sanyi safiyya ya baza yaransa domin bincike akan wanda mead take so .
Tashin farko bincike ya zo masa  akan yadda bai so ji ba ,domin duk wani abinda ya danganta da fuad  da rayuwarsa sai daya zo masa daki daki ya sha mamakin" wai Dan talakawa me'ad take kokarin  neman gujewa aurensa ,aransa yace" idan kinsa wata ai baki San wata ba ,nasan

dai babu ta yadda za'a  mahaifinki ya yarda ki aureshi, balle shi karan kanshi yaron bai sonki ,gbdy safwan yazaba yaransa a gari domin cigaba da kawo masa rahoton komai akan fu'ad.

******

ranar monday  da misalin karfe 1:00 na Rana kabir  yazo gidansu  fu'ad domin   zuwa office din Alhaji Abubakar aminin mahaifinsa  Wanda zai  samarwa fu'ad aikin  da kaninsa ,a shiryensa yake zaune a kofar gida yana zaman jiran karasowar kabir yana hangosa yashiga cikin gidan inda yakewa inna sallama "inna mu za fita akan zance neman  aikin kiyi  min adduar samun nasara kansa ta dafa "InshaAllahu zaayi nasara zaka samu wannan aikin ina jin hk ajikina sai dai Wani tsananin rabo"allah yasa  ni na wuce, "a dawo  lfy  Allah  ya tsare, "ameen  ya fice daga  dakin .

kai tsaye company da alhj Abubakar ke tafiyar  da aiki suka nufa akan lefan din fu'ad suna isa suka iske jama'a wanda dayawansu neman abunyi ya kawosu, batare da bata lokaci ba suka nufi office Alhaji Abubakar inda suka iske shi yana sallah sai mataimakinsa sukagani suka gaisa ya nuna musu gurin zama "ku zauna  ga guri nan ,suka zauna har zuwa sanda ya idar yakaraso garesu inda kabir yayi saurin cewa dady barka da Warhk "a'a kabir har kun iso?ya fad'i hk tare nufar hanyar office dinsa dake cikin wanda suke zaune da sauri kabir  da fu'ad suka  mike sukabi bayansa atare  suka shiga kabir yasamu guri ya zauna akan daya daga cikin kujerun gurin tare da jawa fu'ad shima ya zauna "ai kuna da sa'a duka takardun mutun biyu din da ka kawo sun samu aiki,Amman  D'an bani minti 2 ya fadi hk  sakamakon wayarsa dayaji ta d'auki kara ya zagayo ya zauna mazauninsa tare da d'aukar wayar ya manna kunnesa abinda yaji ne ya kusan bugar masa da zuciya "safwan almustapha maitama ne ke mgn da kai  daga nan office din jakandancin na  kasuwancin Nigeria, naji ance wani mai suna fu'ad yazo neman aiki gurinka ko ba hk ba ?
"Haka ne ranka ya dade.
"To kasani bashi aikin da zakayi yana daidai darasa kujerarka da matsayinka gbdy. .." a,a ranka ya dade ba zayi hkn ba InshaAllahu yadda kake so hk zaa yi,"idan kabi umarnina ka tsira da aikinka kit safwan  ya kashe wayar .

shi kuma alhj Abubakar yashiga goge gumin dake keto masa, bayan yagama goge gumi  ne  ya fuskanci kabir "yauwa kabir batun aikin abokinka a gsky babu shi a halin yanzu ,Dan bazai samu aiki akarkashinmu ba sakamakon wasu dalilai da ba sai na bayyana maka su ba .
"Kmr yaya dady?"da fari kace zasu samu  ,yanzu km ka..fu'ad ya dafa kafad'arshi yana mai mikewa tsaye "karka damu abokina da rashin samunka aikina ka d'auka komai mukaddari ne bani da rabon samun aiki anan ne... yana karasa fad'ar hk ya juya.
"Amma fu'ad...."nace karka damu kayi facing din na  abdulrashid

alhj Abubakar da zuciyarsa ke cike  da matsanancin tausayin fu'ad yacigaba da mgn sai zance aikin kaninka shi yasamu aiki, maiduguri zashi ,zuwa wata mai zuwa   ,wannan aikin mutane dayawa na nema Amman acikin sa'a yasamu kad'an jira takardar tabbatar da samun aikin domin zata iya zuwa a kowani lokacin .

fu'ad yataso daga inda yake zaune yana tunanin dayasa zancen samun aikinsa ke neman shan ruwa, ya kwankwasa glass din office inda kabir ya d'ago yana dubansa cike da tausayawa, alama yayi masa da zaije kasa ya jirasa, shi ma da kai ya amsa da badamuwa .

Fu'ad ya sauka kasan maikatan ya isa inda yayi parking din maching dinsa yana waige waige a gurin hannunwasa duka zube cikin aljihun wandosa ,karaf idanunsa ya sauka Akanta tana tuki cikin karewa, itama tun daga nesa ta hangosa tayi saurin ware idanunta bakinta na furta" fu'ad Dina ...... sai dai tun kafin takaraso inda yake taga ya haye maching dinsa tare kunnawa yayi gaba aiko itama tabishi abaya..........

Mmn sudais ce
[11/3, 8:26 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

Page 53 to 54

.... gudu yake sosai akan titi tana binsa abaya ,yasamu ya karya wata kwana wacce zata fitar da mutun kai tsaye oshodi Express , anan machine dinsa ya tsaya cak yaki tafiya, sai ma hayakin dayasoma fita daga cikin salansar , dan hk ya sauko daga kan machine din ahankali tare da tsaida shi yana dudubawa, har sanda ta iso garesa tayi parking had'e da fitowa daga cikin motarta zuwa inda yake " abun yayi min kyau ba kad'an "gashin nan cikin minti uku kacal nazo na sameka ,"me km yasamu machine dinka ta tmbyta tana dukursowa ta karkashinsa tana kallon fuskarsa cike da matsanancin kaunarsa ,ya mike tsaye tare da rike kugunsa da hannunsa d'aya yana waige waigen ta inda zai samu makaniki kusa ganin babu alamun hk yasa da dungule hannunsa daya ya naushi iska yana furzar da huci mai zafi daga bakinsa ,ita kuma ta matso kusa dashi tana fuskantashi tace"wato fu'ad lokaci yayi da zan baka gudumuwa ,ta hanyar ajiye wannan machine din naka, mai kama Dana masu ACA'ban abbatuwa .

Yana jinta sai dai yayi mata banza batare da ya ko kalli inda take ba har sanda ta maida idanunta akan machine din "uhmmmmm Allah sarki machine dinmu kenan "ko tun yaushe kake dawainiya damu? Kana
Ta matso kusa dashi har suna iya shakar numfashin junansu "kana ji ko fu'ad,Kafin yanzu yaci ace ka kalli duniyar wata ,duba yanayin morar machine dinka dakayi, tazarar dake tsakanin

duniya da wata Mil dubu biyu ne da talatin da biyu da d'ari takwas da sha uku ,ta sake matso shi sosai tamkr zata shige jikinsa wanda hakan yahaddasawa zuciyarsa bugawa da karfi yaja baya kad'an "meye hk kike kuqarin yi ?
Sharesa tayi kmr bata manufarsa ba tace "bari na tmbyeka wani abu ra'ayinka ne hawa machin ko me ?

"kinsan acikin duniyar rayuwata ba son takura balle shishigi, Dan hk ki kama gabanki kawai ya wuce yasoma tafiya dan yasan machin dinsa ya rigada ya tashi daga aiki ,da sauri ta biyo bayansa "wai abun yayi maka rashin dadi ne ko me daka wuce kabarni tsaye?

Sake banza yayi daita yacigaba da d'aga kafafunsa batare daya kalli inda take ba "kana jina ko zan sai maka lafiyayyiyar mota kiran zamani saboda kafi karfin ka dinga hawar wannan kwarababben machen din , shi km wannan machine sai ka kyautar dashi amman kafin nan zan saka kanikawa suzo su d'auka domin gyara .
yayi saurin juyowa yana fuskantarta har hucin numfashinsa ya bugi hancinta ,tayi saurin lumshe idanunta kirjinta na mahaukacin bugawa kusan minti biyu suna tsaye suna kallon kwayar idanun juna sannan a kasalance muryarsa ta fito "anan garin aka haifeni na tashi na girma, nasan kowani lugu da sako dake nan unguwar, akwai makanikai idan ina bukata zan nemesu da kaina, "batu na mota km kibar abunki saboda fu'ad bai bukata komai daga gareki .

"no karkace hk mana bayan da dukkanin alamun rayuwarka na bukatar ha.....a matukar tsawace ya katseta ta hanyar cewa "Kimin shiru anan kafin na d'aukeki da maruka ...

"Mari fa kace?"kina mamakin faruwan hknne ? Yayi mata tmbyr yana tsare gira ," Tayi saurin girgiza kanta alamun a,a "ok na d'auka kina mamaki ne kiga aiki da cikawa wawiya kawai sannan ya juya yacigaba da tafiya tayi saurin shan gabansa tana sauke naunayen ajiyar zuciya tareda rike kuguntа da duka hannuwanta "ok muje na saukeka a gida tunda baka bukatar taimakona "nagode kije abunki kawai....
"Haba fu'ad me yasa kake min hk, Allah fa shi yasan abinda yake nufi daya had'amu ,kayi hakuri kabari na saukeka..a fusace yace "banaso ko dole ne?

Ta. runtse idanunta ahankali tana jin d'aci da rad'ad'in ,wulakanshi gareta, kusan second biyu tana tsaye agurin tana experience din abinda rayuwa kan zowa mutun batare daya shirya ba ,ko a mafarki bata ta'ba expecting zata tsinci kanta cikin soyayya da irinsa ba ,ta d'an Jima tsaye domin ita kad'ai tasan halin tashin hankalin data tsinci kanta sannan tasoma kok'arin bud'e idanunta taga wayam babu shi babu alamunsa agurin ta kara gaba da sauri ta fito titi still bata ganshi ba ,sai ma cin karo datayi da wasu yara kusan su 6 tsaye abakin titi mutun uku makafai yayinda 3 suka kasance masu ido, da alamun titi suke son tsallakawa , tsawon minti uku tana tsaye tana dubansu yayinda mota ko d'aya batayi kok'arin tsayawa domin basu damar tsallakawa ,sbd idan ba lura kayi da kwayar idanunsu da sukayi sama ba, ba bazaka ta'ba cewa marasa idanu bane ,cike da matsanancin tashin hankali ta karasa zuwa inda suke tsaye tare da d'agawa mota ta karshe dake shirin kunno kai hannuta take motar ta tsaya cak, sannan tasoma tsallakar dasu d'aya byn d'aya, wanda hkn ya faru ne a idanun fu'ad ,ahankali shima ya fito

daga inda yake zaune yana jiran ta wuce ya kama gabansa, yak'araso inda sauran yaran ke tsaye, sai waigawa tayi tagansa rungume da yaro daya, d'ayan km rike a hannunsa
bayan sun gama tsallakar da yaran, tasoma kok'arin iskeshi inda yaja ya tsaya rungume da hannunwasa duka a kirji yana kallonta tmkr ranar yasoma ganinta ,tana k'arasowa ta tsura masa idanunta tana kallonsa kmr yadda yake kallonta gabadaya kowanensu zuciyarsa cike take taf da shaukin juna "me yasa kake kallona hk ?
"Na canza maka ne ko kuwa har yanzu kana jin haushina aranka ?tayi masa tmbyr ajare tana sake kallon kwayar idanunsa da suka soma canza launi "a halin yanzu bana jin kiyayyarki cikin raina sakamakon kyawawan halaiyenki ki cigaba abu ne mai kyau taimako da kyatatawa kmr hk.....
yana gama fadar hk ya juya zai wuce tayi saurin riko lauluasar tafin hannunsa cikin nata tana murzawa,ahankali"ina zaka fu'ad kabarni ?
"Dan Allah kagaya min kana sona ko akasin hk saboda ina son na karshen komai a tsakaninmu takarasa mgnr tana cigaba da Murza laulausan tafin hannunsa ."a zahirin GSKY bazan sani ba, ko zuciyata na sonki ko akasin hk amman zaki iya tmbyr ita zuciyarta duk amsar databaki zaki iya d'aukarta amatsayin kaddararki.
Ta narke masa fuska tmkr zatayi kuka alamun shagwaba "ni dai kace kana sona plx tafiya zanyi gobe zuwa Abuja takarasa fad'ar hk tana kai hannuta daidai saitin zuciyarsa dake wani irin harbawa "plz now say something to me "kace kana sona Dan Allah.

"Baza'a ce ba , yasanya d'ayan hannunsa ya zare hannunsa dake rike cikin nata, yakara gaba ya barta tsaye agurin , ita km tsurawa bayansa idanunta tana kallonsa har sanda ta daina ganinsa sannan ta juya ahankali zuwa inda tayi parking din motarta.

tana isa tun daga nesa ta hango safwan zaune akan motarta yana dubanta tare da yi mata kallon kasa da sama sannan yace "sweetie daga ina kike haka? Tayi masa banza ta isa jikin kofar tana kok'arin bud'ewa ya duro daga saman motar tare da riko hannunta ,a matukar fusace ta d'ago kyawawan idanunta ta. Zuba masa tana yi masa kallon kaskanci "cool down sweetie abinda nake son sanar dake akwai kuskure acikin abinda kika aikata a mintunonin da suka gabata, barin mota a irin wuraren nan Sam bai kamata akwai hatsari aciki,gashi kin bar motar dake tattare da sirrikan rayuwarki abud'e "saurin me kikeyi da har kika bar kofar motarki a bude?

Tayi kokari fixge hannunta cikin nasa Amman ta kasa saboda irin rikon da yayi mata bazata iya kwatar hannunta ba ,"karki wahalar min da kanki dan bazaki iya ba ,shiga mota kawai muje gida akwai mahiman bayanan, ko nace magana ta karshe dazamuyi dake ..

Qakarasa maganar yayi tare da bud'e mata kofar motar tashiga ya mayar ya rufe mata, shima ya zagaya ya shiga suka bar gurin, ascot da direbobinsa suka biyosu abaya .

Kai tsaye babban parlour'n gidan suka shiga, tayi tsaye nesa kad'an dashi ta rike kuguntа tana cika tana batsewa, ta matsu bai fara maganarsa domin kawowa karshen zancesu ,saboda ita Sam bazata iya aurensa ba , sannan duk duniya a halin yanzu babu wanda zai takurata akan

zancen aurenta dashi "kayi sauri kayi maganar sannan idan zakayita ka takaita saboda ina da abun yi ta qarasa mgnr tana furzar da iska ta bakinta "ki duba yanayina ,da yanayin shekaruna Wanda yaci ace zuwa wannan lokacin nasamu natsuwar ajiye iyali atare dani ,mead ina sonki son mai yawa, son da bansa lokacin daya shigeni ba ,amman dai yanzu ajiye wannan a gefe, a ina maganarmu ta kwana dake?

"ta kwana ne, a in da nace maka bana sonka,bazan iya aurenka ba ,ka nemi wata matar ka aura period ta fadi HK tare da runtse idanunta..
Shima runtse idanunsa yayi tare da cewa "Amman ke kad'ai ce a zuciyata ,shekara biyar kenan ina dakon sonki me'ad kuma har yau bansamu wata wacce naji ina sonta kwatankwacin naki ba, sai ke mead.
duk maganar dayake mata ahankali take fita kamar yana mata rad'a ita kuwa har lokacin , kasa bud'e idanunta tayi balle ta sake furta komai ko ta kalli kwayar idanun safwan wanda ke fitar da wani irin abu acikinsa mai kama da kibiyar so ......
jin ya qara yin kusa daita tare da riko laulausar tafin hannuwanta ahankali, shi yasa tayi saurin ja da baya daga tsayen datake.

"safwan idan saboda kyawuna ne I thought kaima kana da naka kyawun daidai gwargwado, sannan akwai yammata masu kyau wad'an da suka fini suke da duk abinda kake gani ajikina dakaji kake sona ka zabi daya daga cikinsu ka aura mana zakaji dadin rayuwarka dasu , zaka samu tattali fiyye da yadda kake tunanin samu a wajena, safwan ina son fu'ad fiyye da son kowa a duniya idan har ka fitar da iyayena "har ni me'ad kin fi son shi akaina yayi mgnr muryarsa na kmr zaiyi kuka?
"daman kai ni ban ta'ba kawowa zuciyata kai a matsayin mi....
yayi saurin janyota jikinsa ta fad'a cikin fad'ad'd'en k'irjinsa inda bai tsaya wata wata ba ya rungume tsam sbd yarigada ya fara rud'ewa daita, "karya kike me'ad bakya son shi ni kike so, shekara biyar din da muka d'auka tare, ban ta'ba jin kin ambaci sunan wani d'a nmj ba ,asalima sunana ne acikin bakinki meyasa kike son ki gujeni yanzu alhalin ina mutuwar sonki ......... ?"ki aureni zan mallaka miki komai nawa dana mallaka ke ko rayuwata kike so zan baki amman karki barni...

Tayi saurin janye jikinta tare da sake ja baya sosai tana fitar da numfashi sama sama sai alokacin ta lura babu mayafi ajikinta balle abinda takama gashinta dashi, ta bata fuska sosai tmkr zatayi kuka "me yasa ka cire min mayafi?ko kayi zaton nima kmr irin mutanenka ce ,to bari kaji na gaya maka nifa ba yar is...
"Me ya kawo wannan batu mead?su waye km mutanen nawa? Yayi tsoki yana dafe gefen kansa daya ji yana sara masa kad'an kad'an sannan yace "ki samu guri ki zauna muyi mgn, naji na janye zance aurenmu hk yayi miki?"kije ki gayawa shi wanda kike son din ya turo iyayensa kawai musha biki .

"da gaske!!! kake safwan ka janye batun aurena ?"sosai kuwa ai nafi bukatar farincikinki akan nawa.."sai me ?" Sai ga me'ad ta dawo kusa dashi ta zauna rike da hannuwansa "nagode nagode safwan Allah yabaka wace tafini "ai kibar wannan adduar me'ad saboda bazan ta'ba

samun kmrki ba ,dubi surar jikinki fa meye baki dashi me'ad?

Take ta had'e rai "Ka d'auke idanunka ajikina ,ni dai na.......gode sosai, sannnan ina neman alfarma agurinka "uhmmmmm ina jinki ki roki komai kike so?
"ina son ka gayawa dady ka janye batun aurenmu sannan kayi masa zance fu'ad dan Allah idan kamin hk ka gamamin komai a duniya, kuma zan tabbatarwa kaina lallai kai mai sona ne da son farincikina.
"karki damu swe ...am kanwata an gama, ba sai hira ta barke tsakaninsu ba har inda take gaya masa zatayi tafiya zuwa abuja gobe, amman kwana biyu zatayi ta dawo Dan Allah tana son kafin ta dawo yayi mata kok'ari, har kusan la'asar suna tare makale da juna kmr tun farkon shakuwarsu, kafin shakuwar ta juye zuwa soyayyar da iyayensu suka karfafata, har farfajiyar gidan ta rakashi suna cigaba da tautaunawa da kanta ta isa ta bud'e masa mota yashiga ya zauna yana d'aga mata hannu tana daga masa har motacinsa suka fita daga harabar gidan , safwan ya bar gidan zuciyarsa na wani irin tsalle da zafi tmkr ana zuba masa ruwan dalma acikinta.

**********

ta bangaren sajida kuwa, tana cikin tashin hankali mara misaltuwa ,ganin yadda kullun kwanakin aurenta ke sake. matsowa ,gbdy ta rame tayi baki ta fita haiyacinta ,bata samun ishashen bacci akan mutumin da bai san da zamanta ba ,lamarin aikinta ma tattara shi ta ajiye agefe ,sai zaman d'aki da kuka, har ta kai ga kiran emran dake k'asar London yana aiki da BBC, tana kuka take gaya masa ita tafasa aurensa ba ,shima kukan ya fashe mata dashi yana tmbyrta dalili had'e da rarrashita tare da bata hakuri " idan narasaki sajida Zan iya rasa raina nima ,byn sun gama waya daita,ya kira acp yake gaya masa abinda ake ciki, acp yace" ya kwantar da hankalinsa tare da bashi tabbacin mutuwa ce kawai zata hana yiwuwar aurensu , tunda gashi ma lokaci ya kusa ,a daren acp bai runtsa ba sai daya dangana da d'akinta in da ya sketa kwance tana kuka "yayi mata kaca kaca sannan ya k'ara"matsawar kika butulcewa auren emran bani babu ke ,sai dai ki nemi wani uban Amman bani ba... wannan tashin hankali ke hanata sukuni da walwala tasha gwada kiran fu'ad, amman ko ya d'auka bata mgn ,sai dai ta saurari sautin muryarsa ta kashe, a ranta take aiyana ko ta auri emran zata kashe auren domin cikar burinta.

**********

Dare yayi nisa amman fu'ad ya kasa runtsawa ,shi yasan ya dad'e da tsintar kansa cikin shaukin soyayyarta, sai dai yasan rijiya ba gurin wasan yara bane, dan haka yasoma yaki da zuciyarsa, ta hanyar yakar sabbin kibiyoyin dake hud'a kowanne sako na cikinta. Sai dai duk iya kokarinsa a wannan daren baccin dayake bukatar samu ya gaza samunsa ,surar me'ad kawai yake gani cikin kyakkwan murmushinta ,Dan hk da yayi sallar asubahi ma ya dad'e zaune yana rokon Allah saukin al'amarin amman ina mead ediress takai ta kankane koina na zuciya da kwalkwaluwarsa ta karasa gangar jikinsa bata barshi da ko saqo daya da zai sanya tunanin kansa..

*********

Kmr yadda fuad bai samu runtsawa ba hk rayuka uku nan ,basu runtsa ba mead sajida safwan, safwan na kokarin ganin ya cire me'ad da lamarinta acikin rayuwarsa, ita km sajida tashin hankalinta yadda kullun me'ad take nacin son mallakarsa wannan takaicin ke hanata runtsawa . Yayinda me'ad abubuwa guda biyu ne suka hanata runtsawa da fari farincikin janyewar safwan da kuma tunanin yadda fu'ad zai fuskanci lamarinta, wanda kusan nashi tunanin ne ya hanata runtsawa, abinda tabasayi, shi mike domin yi wato sallar dare, allah yayita da dabi'u mabanbata Amman sai ya tsaida ita,da yawon son ibada acikin zuciyarta, duk iskancinta bata bari alokacin sallah ya wuceta ,wannan kuma Allah shi ya barwa kansa sani akan manufarsa gareta , alwala tayi domin gabatar da nafilfilinta data saba, tana nan zaune har sanda aka kira sallah sannan ta tashi ta gabatar, bata yi yunkuri komawa bacci ba tasoma shirinta, Dan hk washegari byn tayi sallama da iyayenta itace mutun ta farko data yiwa inna sallama a bakin kofarta , tazo ta bud'e ita kuma ta umarci direbanta daya kwaso kayan dake bayan boot din yashigo dashi sannan tasanya kanta cikin d'akin bakinta d'auke da sallama, Zuwansa gidan inna kenan yana kalaci. Fu'ad ya d'ago kyawawan idanunsa yana kallonta kirjinsa na wani irin mahaukacin buga domin sam baiyi tunanin zai ganta adaidai wannan lokacin ba ,itama kallonsa cikin kwayar idanunsa take wad'anda atake ta gane kankancewar da sukayi gashi sunyi ja alamun rashin wadataccen bacci kmr nata, kada tayi haufi inji zuciyarta shima ya kwana cikin kwatankwacin irin situation din data kwana.

Inna ta shimfid'a mata sallaya, tace "bismillah ki zauna ki kasance tare damu tasoma kok'arin zama idanunta na cikin mayatattun sexy eyes dinsa "tace anya kuwa inna ayi hk?"akan hanyar aiport nake .

"Duk da hk dai yar nan wannan sammakon da kikayi bai isa ace kin sanyawa cikinki abinci ba sai dai idan kalar namu abinci ne bai miki ba...
Tace"wallahi ba hk bane inna ,babu yadda mom dina batayi ba ,Dan na tsaya naci amman idan wannan jikan naki yayi min izini sai in ci ko acikin nasa ne.

Fu'ad ya ajiye kofin shayinsa dayake kur'ba ahankali ahankali ,idanunsa acikin nata yace "idan ni ne sai dai ince kada Allah yasa kici, me'ad da inna suka tsurawa bakinsa ido "kina kallona inna wace bataji mgnr mahaifiyarta ba, Dan me zataji tawa?

Tayi ajiyar zuciya tana mai nunasa da d'anyatsa hannunta" kai ko sannan tayi kasa da murya wanda shi kad'ai zai iya fahimtar abinda zatace "hidimomin tunaninka ne fa ya hana tsayawa na karya .
ya murmusa gently abinda bata ta'ba gani ba kenan a fuskarsa, shiru tayi tacigaba da kallonsa.

inna tace "manta dashi ki zauna kuci tare bari na qaro muku "a,a inna kibarshi kawai Dan banajin yunwa , ga sako can an shigo dashi karki ce bazaki amsa ba dan Allah inna ni dai fatana kin sanya min albarka "fu'ad ya runtse idanunsa Dan dadi yaji dadin abinda tayi amman bazai bari wannan kyautar shiga tsakaninsu ba ,ahankali ya bud'e idanunsa yasanya cikin kwayar idanunta sannan yakira sunanta"me'ad ..
wannan shine karo na farko da hkn yafaru taji sautin sunanta abakinsa wani irin abu taji yana

yawo acikin jikinta. Dama kwalkwaluwarta gbdy ta amsa da "na'am fu'ad "ki koma da abinda kikazo dashi mun gode kwarai da kulawa....
tayi kicin kicin da ranta sannan tace "ina ruwanka da abinda na kawo?"inna na kawowa ba kai ba balle kace hk ta waiga gurin inna "inna ni zanyi tafiya zuwa abuja ki min addua sannan ki sanya min albarka, kai kuma sai kaji wayata ta mike tsaye inna na kwararo mata addua sukayi sallama.

Can dare har ya kwanta wayarsa ta d'auki kara yasan babu wanda zai kirashi a daidai wannan lokacin sai ita, ya mika hannu ya d'auka zuciyarsa na beating ya manna a kunnensa a kasalance yace baki kwanta ba ?

Tace "na kasa bacci ne ,na sauka lfy Amman tunani na neman mayar dani mara lafiyar karfi dayaji.
Ya rage muryarsa saboda kada ya tashi su kabeer yace " ke kuwa tunanin me kike hk me'ad?

"Kai tsaye tace "tunaninka?

Yayi ajiyar zuciya mai sanyi cikin ransa yace "nima hk tunaninki ya hanani walwala da runtsawa ,bai san cewa a fili ya fad'a ba ita kuwa kunnuwanta sun rigada sun zuko mata sautinsa, tayi murmushin jin dadi wanda ya fidda sauti, cikin ranta km godiya tayiwa Allah daya takaita mata wahala da rashin tabbas din datake hangowa alamarinsa.

Daga nan sai me? Sai hira ta 'barke tsakaninsu kmr ba fu'ad ba shi kansa har mamakin kansa ya shigayi ta yadda cikin kankanin lokacin me'ad ta tankwasa zuciyarsa ta sauya mata akidar tunaninsa, na bazai saurari kowace mace ba har sai byn ya samu aiki, tare da daidaita a rayuwarsa sannan zai bud'e shafin soyayya.
Amman gashi a wannan daren ya kulla soyayya mai karfi mai ban mamaki da me'ad takai wanda bai ta'ba tsintar kansa ciki ba.

Tun daga ranar kullun sai sun raba dare suna wayar soyayya, har tabaro abuja, yanzu ne me'ad tasan tana cikin shaukin soyayya, ba soyayyar kuruciya ba da'ake son tursasa zuciyarta ciki . wasu emotion ke tangaliliya da rayuwarta da zuciyarta akan fu'ad dake aiki cikin zuciya da kwalkwaluwarta. bata 'bata lokaci ba gurin sanarwa da aminiyarta sajida ba ,wanda wannan sakon yayi gigita ya haukatata har yayi nasarar kwantar daita a gadon asibitin ..

Mmn sudais ce
[11/3, 8:27 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

Page 55 to 56

.......bata san inda hankalinta yake ba, sai farkawa tayi ta ganta a gadon asibiti ,ta fahimci hakan ne ta hanyar ganin wata nurse a tsaye akanta, dan tana bud'e ido daita tasoma cin karo tana kokarin sanya mata k'arin ruwa.

tayi saurin mikewa zaune tana raba idanu tare da tuna abinda me'ad takirata a waya ta sanar mata wanda shine abinda ya haddasa mata zuwa asibiti , me'ad wace dawowarta kenan daga tafiyar datayi zaune take abayanta tana mata sannu , jikinta a matukar sanyaye, sai dai kallo daya sajida tayi mata abinda ta gaya mata ya sake dawowa cikin 'kwa'kwalwarta da gangar jikinta, idanunta gbdy sun rikid'e sun dawo kamar gauta al'amar taci kuka tagaji dan har lokacin hawaye ke bin kuncinta,tana jin tmkr ranta ake zara gbdy takaicin me'ad take ,a halin yanzu bata jin akwai halitar data tsana sama da emran daya nacewa aurenta sai km me'ad datayi wa rayuwarta karan tsaye ,tana matukar son fu'ad kmr tayi hauka aganinta ita tafi cancanta yaso ba me'ad,saboda tafi tsananin son shi da buk'atarsa .

"Me yasa so yayi mata yanka kauna irin hk?"me yasa idanunta suka had'u dashi? "Ina ma batayi mata rakiya ba a wannan ranar, ranar datayi silar dagulewar duk wani lisafin rayuwarta.....takarasa zance zuci tana sake fasa wani irin gigitaccen kuka tare da fizge hannunta daga rikon da nurse tayi mata,sannan ta bar jikin me'ad ta kakkame misna tana wani irin kuka "shikenan narasa shi ko misna ?

Ta furta hkn a bayyane ta sake tafiya luuuuuuu sai gashi ta kifa k'asa daga misna da me'ad har nurse din sun gigice har aka rasa wanda zai yi wani abu akai.

me'ad ta durkushe bisa gwiwowinta tana jijigata cike da matsanancin tashin hankalin ,da kiran sunanta cikin k'araji, yayinda kukan datake ta rikewa tun d'azu ya kwace mata, ita kuwa nurse da gudu ta fice daga d'akin dan kiran likita atare suka dawo wannan karon har da dady da acp da hjy Khadija mahaifiyar me'ad suka biyo bayansa.

likita ya d'agata da taimakon su dady suka maidata kan gadon yayyafa mata ruwa sukayi, sai kuwa ta bud'e idanunta tare da sakin wata ajiyar zuciya da karfi ,idanuta ya d'auro akan mahaifinta da iyayen me'ad "Allah sarki uwa mai dadi,ina ma tata uwar na raye da wata killa tazamo sanyi idaniyya mai share mata hawaye, acikin wannan halin datake ciki.

kallon mahaifinta take tana kuka sosai a zuciyarta ta sake furta "shikenan narasa shi ko?

gbdy suka k'araso gareta cikin tashin hankali saboda jin furucinta a she a filli tayi mgnr batasani ba "waye shi din wanda kika rashi?

me'ad da momy suka rungumeta suna gunji kuka cikin kuka momy tace "sajida waye shi ki gaya mana ko waye shi da kike ikirarin kin rasashi, "a tunaninmu emran kike so kuma yana raye bai mutu ba, asalima yanzu muka gama waya dashi.

Girgiza kai tasoma yi tana fidda numfashi sama sama "bashi ba..bashi nake nufi ba ni kad'ai nasan kowaye ,wanda nake nufi yana raye sai dai narasashi.....

".ki gaya mana kowaye shi zamu san abin yi "a'a khadeeja koma waye shi sai dai ta hakura ,sbd ni bata ta'ba sanar dani tana son wani ba byn emran,wanda itace da kanta ta kawo min amatsayin  mijin aurenta, kuma zuciyata ta aminta dashi," kan wani dalili take son maidamu kananun mutane.?

likita ya dafashi alamun rarrashi yana cewa "ka kwantar da  hankalinka ranka ya dad'e,ka natsu ka binciketa da kyau idan har batason shi wanda ta kawo din yanxu ,sai a hakura mana ,  "itace dai zata hakura da koma wani d'an iska ne . "Alamarin na soyayya mafi yawa masu kwalkwaluwa irin tasu su kan d'auketa da tsananin sai daga baya komai ya daidaita, kamata yayi kasamu lokaci kayi zaman sirri daita domin sanin kowayeshi yaron, "wallahi kaji na rantse sajida bata da miji daya wuce emran koda mutuwa ce sai dai ta dauke ad'akinsa Amman...

wata irin zabura tayi hjy Khadija ta rikota da sauri,wanda hkn yayi nasara katse acp ya tsura mata ido, shi kansa dady sai dayayi dayasani furuncinsa,saboda yadda yaga gbdy ta sake firgicewa, likita yayi kok'arin 'ban'bareta da kyar daga jikin momy yana fad'a tana sakin momy ta sake Sumewa alamarin daya d'aga musu hankali kenan kuka kawai suke har da acp ,momy tace wannan wani irin maseefa ne ? A zuciyarta.

" Ga zance me'ad  dake soyayya da d'an talaka ,wanda har yanzu mahaifinta bai sani ba ga lamarin sajida.

likita yana bata taimakon gaugawa yace "ban so ka dinga fad'ar irin wand'an maganganun ba,yallabai,  irin wannan lamarin rarrashi da nasiha yake bukata da kwantar da hankali yakarasa mgnr yana mata allurar bacci sannan yacigaba "koda zata farka Insha Allahu  zata dawo Normal"Allah yasa suka amsa gbdy,lamarin na sake d'aure musu kai.

Cikin ikon Allah kmr yadda likita ya fad'a koda ta farka tasamu natsuwar zuciya , bugun zuciyarta datake jin ya tsananta ,yayi k'asa sosai yasoma dawowa daidai, sai dai kallo daya zaka mata kasan tana cikin matsanancin damuwa. Lokacin da me'ad ta gama taimaka mata tayi wanka da sauransu ta matsa da tambaya.

"waye shi wanda kikarasa sajida ,da har yayi silar kwanciyarki hospital?tayi mata shiru taki cewa komai "to mai ma zata ce mata,tace akan fu'ad tashiga wannan hali ko mai? Ai ma abun

kunya ne ita da aminyarta sun kama da soyayyar mutun daya kmr wani almara.
Tsawon lokaci me'ad na tare daita tare da son jin damuwarta amman sam sajida taki gaya mata komai"wato ni ban san ciwon kaina ba kenan danake gaya miki sirrukana da abinda ya shafi rayuwata ba ko ?

"shikenan sai kicigaba da rike damuwarki ke kad'ai mu km zamu cigaba da tayaki da addua, Dan ni tuni zuciyata  ta soma zargin kin fad'a soyayya da wani mafi kusanci damu.

"ba karya kika fada...."ina ma  zaki bar min shi da har karshen rayuwa bazan manta dake ba?tayi mgnr cikin ranta tana mai runtsa idanu.

Kwananta biyar a hospital likita ya sallamota duba da ganin samu saukin jikinta,domin tayi kokarin tsaida zuciyarta gurin soma cire fu'ad cikin ranta, ta sake maye gurbin gurin da emran kai tsaye gidansu me'ad aka wuce daita bisa umarnin mahaifinta daya bayar.
Kowa a gidan attention dinsa na kan sajida da bata duk wata kulawa tare da sanyata cikin nishadi, hkn nayi mata dadi sosai sai dai har lokacin tunaninsa yaki barinta.

*******
Yau me'ad da kanta tashiga kitchen sa'baninta lokutan baya,ta  had'a dinner mai rai da motsi da taimakon ummi sannan tashiga wanka har ta fito ta tsaya gaban mirrow hankalin sajida na kanta tarasa dalilin da hk kawai take jin babu aranta, a game da wanka data shiga, ahankali me'ad tayi shafinta ta  shirya  cikin wasu had'ad'd'iyar  doguwar riga swiss less ruwan zuma tana fesa turare a kowani lugu na jikinta kararrawar shigowa gidan tayi k'ara sannan wayarta ta hau ruri tabbacin fu'ad dinta ya iso kmr yadda sukayi dashi, daman tun a safiyar yau kai tsaye takira masu gadi ta gaya musu tana da baKo su barshi yashigo, tayi taku d'aya biyu taji sautin muryar sajida cikin rauni dayasa ta tsaya batare data juyo ba "fu....fu'ad ne yazo . ?"uhmmm ta bata amsa dashi tana gyara mayafin jikinta "ok ki gaida min shi "zaiji ta sanya kai fice daga d'akin ,mead na fita ta mike tashige bayi saboda kukan daya tunkuro mata mai had'e tari ,tana shiga ta fashe da wani tsumammen kuka.

Me'ad  na k'arasawa farfajiyar  gidan,ta d'aura kyawawan idanunta akansa sai ta nemi daburcewa , kasancewar wani azababben kyawun dataga ya kara mata, suka dubi juna da wani irin kallo mai kwantar da zuciya, kafin kowannensu ya saki murmushin mai d'auke da boyayyar ajiyar zuciya.

Gaba tayi ya biyota abaya yana kallon kugunta dake juyawa ahankali wanda yasoma tayar masa da boyayyen tsumin shaawarsa da bai san yana daita ba ,da sauri ya d'auke idanunsa zuwa yanayin tsarin gidan , adaidai wani karamin parlour'n baki ta tsaya tare da kaucewa tabashi hanya  yashigo parlour'n cikin kodaddiyar shadda mai hasken sararin samaniya gilashin idanunsa fari ne dan siriri, wanda ya fiddo da zahirin cikar kamalarsa na cikakken d'a nmj wanda rayuwa ke yayi ,matsalarsa dai rashin aiki da kudi, ita kanta tana da tabbacin da zai kasance mai aiki a hannunsa, matan da zasuyi rubibinsa suna dayawa da wata killa ma bata had'u dashi ba me'ad tayi nisa sosai a kallonsa, yayi murmushi yasoma busa mata iskar

bakinsa a idanunta tayi firgigib ta dawo haiyacinta .

"kallon ya isa hk me'ad ,sosai taji kunya abinda yace, ta wuce ciki suka zauna cikin kananan leather da suka yiwa qaramin parlour'n nasu qawanya.

Tace "sannu da zuwa honey ya hanya?  Yayi murmushi tare da lumshe idanunsa kmr bazai amsa ba sannan yace "lfy  . tayi D'an jim tana kallonsa sannan suka gaisa  gbdy suka kasa boye soyayyar dake zuciyoyinsu sun jima suna bayyanawa juna sakonni zuciyoyinsu daga karshe ta gabatar masa da abinci da abun sha amman Sam yaki ci komai "iya ganinki kad'ai me'ad ya isheni ....taji Dadin wannan furuncin nasa sosai har kasa boye farincikinta.

Sajida takira mahaifinta dayazo ya d'auke da kansa, Dan bazata iya tuki ba, ta gwammaci zaman kadaitan gidansu akan tacigaba da zama tare da mead, wacce  bata iya boye son fu'ad ako gaban waye,nunawa take, da yammanci ranar tana kwance tasoma jiyo jinia, ta tabbatar da mahaifinta yazo, har cikin gidan yashigo sun dade da dadyn su mead suna tautaunawa akan yadda bikinta zai kasance ,sannan daga baya yasa akayi kiranta nasiha da rarrashi sosai dady yayi, har gaban motar dazata shiga ya kai ya bude mata da kansa yana sake rarrashita ,dady na tsaye har sai daya ga wucewarsu sannan ya koma cikin gida yana girgiza kai.

********

Soyayya fa mai karfi tashiga tsakanin me'ad da fu'ad, cikin salo mai ban mamaki basu iya sati basu sanya junansu a ido ba ,kullun yana  kan hanyar zuwa gidansu  idan kuma bai zo ba, suna makale a waya, duk wannan wainar da'ake toyawa babu wanda ya sanarwa dady har safwan dan koda ta tmbyesa ko ya sanar masa "cewa yayi bai samu had'uwa da dady ba,gashi tafiyar gaugawa tasameshi American sai ya dawo tukun.

Bata damu ba, tacigaba da bawa fu'ad kulawa, fu'ad shi din yasan me Nene  so? yasan darajar abinda yake son,ya km iya tafiyar dashi ta hanyoyi daban daban,  ta yadda duk wanda zata so shi,zata so shine da dukkanin zuciya, ruhi da gangar jiki koda taki Allah shi ba dan bariki bane, amman ga matar dayake so, mugun dan soyayya ne kmr ba indiye dan irin kalaman dayake furta mata azahiri da cikin waya idan ka ganshi a zahiri rantsewa zakayi kace bashi yake fad'arsu ba ,sbd tsare gida da rashin son raini ,Dan hk ne bai sha wahalar sake yiwa zuciyar me'ad kamun kazar kuku ba, bata da wani tunani sai na fu'ad ,bata da wani ra'ayi sai nashi bata da wani buri sai na mallakarsa matsayin abokin rayuwarta har karshen rayuwa.

Gbdy ta mance da wani safwan dake can wata kasa tattare da dakon soyayyarta ,a wani zuwa ne da fu'ad yayi  tana zaune gabansa cikin less mai taushi fari sol da zanen silver ,dinki bakaramin kama jikinta yayi Dan har saman dukiyarta yana iya hangowa, shr yayi zuwa wani lokaci sannan yakira sunanta muryarsa a kasalance  "mead, na zauna nayi tunani mai yawa akan lamarinmu dake, ni talaka ne sannan d'an talakawa gaba da baya, wanda yake karkashin kulawar kakarsa ,da bata da komai ,bata aje ba sannan bata bawa kowa ajiya ba,gani zaune babu aikin yi ina sonki sai dai bansa yadda zanyi ba idan batun aurenmu ya tashi .

Maganganunsa sun mata ciwo matukar da hk muryarta a d'an zafafe tace "duk nasan da hk fu'ad nace ina sonka.

Ya langwabar kansa tare da tsura mata idanu kmr zai cinyeta sannan ya bude bakinsa da kyar yace "zaki iya zama dani cikin halin babu, sannan bazan iya rayuwa babu innata a kusa dani ba saboda nayi aure, Dan tayi min komai arayuwa, byn kasancewarta kaka gareni uwa ce mai tattare da matsayin uba, ta taka matsayin komai gareni zaki iya tallafawa rayuwata data innata?

Ta lumshe ido cikin wata sabuwar kaunarsa dake mamayarta ta km lullu'be zuciyarta "kada ka damu baka da matsala dani fu'ad soyayyarmu had'in Allah ce ba dan wasu kyale kyalen duniya ba, kacigaba da tafiyar da rayuwarka hk ina sonka hk , ina girmamaka sbd dattakonka,ni fuad din kawai nake so bawani abu nasa ba ,ina matukar sonka ta yadda har bazan iya waiwaya ba, in hango hierarchy dinsa ,yake gani wanda shi so baya la'akari dasu.....sai byn data furta hkn kunya ta lullu'beta Dan ganin irin yadda jikinsa yajike yake tsuma km ya zubawa dan karamin bakinta idanu dake motsi yana fitar da kalamai masu sanyi garesa, tacigaba "ni dai fatana da burina ka rikeni amana ka yardani nima in yarda da kai, Allah yardadamu yabamu ikon mallakar juna idan kayi min wannan, ni km nayi maka alkwarin zama da kai muddin rai cikin kowani irin hali ,akwai ko babu dadi ko akasin sa....da sauri ya mika mata hannunsa tun kafin takarasa.

"shake my hands my love..nagode da soyayyarki gareni, ina rokon Allah ya fiddani kunyar soyayyarki..yabani ikon fita hakkokinta yabani ikon sanin mahimmantata fiye da duk wani alamarin da dan adam ke burin samu suka had'e hannuwa guri daya kmr masu kulla alkwari. Ta lumshe ido jikinta na tsuma saboda had'uwar tafukan hannuwansu ,domin ji wani abu na fita daga cikinsu zuwa nata naunayen ajiyar zuciya ta sauke tana sake damke hannunsa cikin nata sannan tace "sai batu na neman aiki fu'ad kabani CV's dinka a samomaka aiki, ina bukatar ganin cikin office honey, ka yarda ka amince min....

Murmushi yayi "kibar wannan issue din, nima ina kan nema da kaina wanda ya amshi takarduna ina sa ransa samu, ki min addua yakarasa mgnr yana saka yatsun hannuta cikin bakinsa, bai tsaya bata lokaci ya fara tsotsarsu domin kwantar mata da hankali, aiko take abinda yake bukata daga gareta ya kau Dan jikinta ya d'auki kyarma dan ji tayi kmr yana zarar ranta da kyar tasamu ta kwaci hannunta fa fad'a jikinsa .

************

An yi bikin sajida na ban mamaki sannan aka kai amarya gidan mijinta dake cikin ajawo estate, 'yan kai amarya mutun Hudu basu tsaya ba ,suna kaita suka juyo bayan kowa ya fita ne ta d'auki jakarta tashige d'aki ta kulle kanta har gari ya waye sannan ta shirya ta fito ta zauna cike da jin haushi emran ita fa fu'ad take so, zuciyarta ta kasa hakura dashi gbdy ango yarasa gane kan amaryarsa, duk yadda yayi daita taki haushinsa take ji, da ganin bai iya komai ba ,komai yayi bai iya ba fu'ad ne ya iya kwata kwata baya burgeta tana zaune emran yashigo yana fara'a wai shi me amarya ya samu gefen kujerar da take zaune ya zauna tare da zura mata ido baya

ko kiftawa.

ita kuwa ko kallo bai isheta ba ta juya masa baya dama tagaji da kallon dayake mata kawai sai ta mike tashige dakinta .
yasha mamakin abinda ya faru shi daman tun kafin bukinsu yaga ta canza tmbyr duniya yayi mata taki amsa masa .

Satinta daya a gidan
da yamma emran yashigo yace taxo yana son ganinta, bata kulashi ba dan bai isa ba shi km ya dawo parlour'n ya zauna yana jiranta ya jima yana zaune a parlour'n amman bata fito ba hkn yayi maseefsr 'bata masa rai ya tashi ya koma cikin d'akin yasameta a kwance a inda ya barta batare da niyyar tashi ba ,ya daka mata tsawa da cewar sajida wai me ke damunki ne da har zan dinga miki mgn kina jina byn ba dole nayi miki ba ?

"wai ma me kike nufi ne tun sanda aka kawoki gidan nan kin kasa zuwa ki gaida iyayena, dan baki d'aukesu abakin komai ba,
sannan ko ruwan zafi baki tab'a dafa min kin kawo min nasha ba balle kiyi min girki irin na mata da miji ki kawo naci to kisani bazsn dauka ba..

sajida dake kwance jin yayi shiru yasa ta tashi zaune tana yiwa emran wani kallon tsana tace "amman emran kabani dry dan ina jin kana da matsalar kwalkwaluwa, banda hk ka dubeni da kyau kace wai ni zan maka girki ashe zaka mutu da yunwa bakaci ba,dan ni ba yar aikinka bace kuma ba tun yau ba kasani ko ruwan zafi ban iya daurawa ba, idan kuma ka manta na tuna maka saunawa me'ad na sanar dakai sajida bata iya komai ba?

Dan hk ko ruwan zafi dazaayi wanka dashi ban iya dafawa ba ,kai ko gas ban iya kunnawa ba balle km yin girki dan hk ka nemi wace zata dafa maka abinci sannan zance inje ingaida iyayenka ai basu na aura ba su dan girman kai tinda nazo gidan basu zo ganni ba balle su girmamani amatsayina na matar d'ansu, kaga nima bazanje in gaidasu ba don neman gindin zama bazanje koina ba kaji ko?

idan km sai naje ne sai dai ka sakeni nakara gaba..

"au haka kikace ko?

Emran ya fad'a cikin 'bacin rai "Kwarai na fad'a itama ta mayar masa tana cewa dama kasakeni naje nayi yakin neman auren fu'ad shi kawai zuciyata ke muradi ba kai ba ta fada aranta.

bai kuma cewa komai ba yasanya kai ya fita yana mamakim abinda ya canza masa sajidarsa ,shi ba zance rashin girkinta ne yafi damunsa kmr yadda take nuna kiri kiri bata sonshi yanzu.. idan rashin girki ne ya Dade dasanin hkn, km har yayi tunanin nema musu me aiki amman kwata kwata yarasa meyasa ta tsiro masa da wannan halin to ko dan taga yana maseefsr sonta ne?

amman yasan yadda zai yi mata momysa zai gayawa watakilla yasamu kanta .

yana fita sajida taja wani dogon tsaki ta koma ta kwanta lamo tana tunanin fu'ad.

Mmn sudais ce[11/3, 8:26 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

Page 57 to 58

.........Emran na fita kai tsaye bangaren ummansa ya nufa bakinciki duk ya cika masa zuciya,umma ta sarawa d'an nata lokacin daya gaya mata irin abinda sajida take masa .

Umma da kanta taje bangaren sajida domin yi Mata fad'a saboda tana mutuwar sonta kmr yadda emran dinta ke sonta, Amman abinda  sajida tace ya kusan sumar umma dake zaune cewa tayi " hjy ai ba nice kawai mace ba a duniya , idan yaji haushi kuma bazai iya da halina ba ya sake aure tunda yana da kudin da zai iya auren ko mata nawa ne,Dan  ni ba ruwana ,abinda nake son ya gane kuma ya fahimta  banzo gidansa Dan in yi masa biyayya ba,ko wani bauta, shima yasan da wannan, in karya ne ki tmbayeshi gashi nan zaune agabanki .

Umma ta girgiza kai cike da bakinciki sannan tace "shikenan babu komai tunda da kanki kikace yayi miki kishiya zakuwa ayi da yardar Allah, Dan kuwa  zan tabbatar da d'ana emrana ya auro santaleliyar budurwa yar gidan mutunci.

"To ni hjy manene zai dameni ,byn nima har yanzu amatsayin budurwa nake babu nmj daya ta'ba takani , ni da zaki taimakamin ma  da kinsa wannan d'an naki ya sallemi na huta...
emran ya yunkura ya mike jikinsa na rawa zai d'auketa da wani gigitaccen mari, hjy tayi saurin taresa "kul karka soma ...  akwai abinda yafi duka ko mari zafi arayuwar d'an adam, shi yafi cancanta kayi mata ba mari ba Dan ko ka mareta bazaka huce ba.

Gabadaya jikinsa kyarma yake "yanzu har sunzo gurin shi sajida,?wulakantashi da iyayensa zagaye dakin yasomayi zuciyarsa na masa daci da tafarfasa, ita dai umma bata sake cewa komai ba ta tashi ta fita tana jin zafin abinda sajida tayi mata, sai dai tayi kanta alkwarin duk

runtse sai ta aurawa emran mata har biyu sai dai idan shine baya so.

Kwana hudu tsakani abinda daya faru da daddare suna bacci kaddara ta fad'o gidan, domin barayi ne sukayiwa gidan diran makiya, saboda jin labarin emran yashigo da wasu makudan kudi masu yawa xshiyasa sukazo dan su amshi rabonsu, gabadaya mutanen gidan suka tara a falo daya, duk sukace kowannensu ya kwanta flat a kasa ,kowa ya kwanta amman banda sajida saboda jin itace diyar acp , taki kwanciya babu yadda emran bai yi daita ba amman taki, babbansu yace" da kyau yar kanwata kinfa burgeni sosai, dan kina da zuciya mai dakiya ke matar 'barawo yakamata kizama bana na maikacin BBC ba , amman duk da hk za'a shafa miki bakin fanti da iya rayuwarki idan kika tuna zaki ji zafi, ke ba iya ke ba har ya'yanki sai bakin fenti ya shafesu, yakarasa mgnr ya kalli wani baki mummuna daga cikin yaransa yace "kai shigar min daita turakar mai gidanta, in sha jinita sannan nayi maganin abinda ke damun kwalkwaluwarta. Take yaron ya isa inda sajida take ya kama hannunta da karfi ya fixgota xuwa jikinsa, tayi waya siririyar kara tare da kiran sunan emran da mahaifinta cikin tsananin tsoro da razana.

Emran yayi saurin d'agowa ya dubi ogan zuciyarsa na beating yace "Dan Allah oga kayi hakuri wallahi duk abinda kake so zan baku in dai zaku kyalemin mata amarya ce ka duba girman aure.

Ogan yayi dryr mugunta yace "kada ka damu abokina zan koyar daita komai sannan zai koya mata hankali da ilimin rayuwar duniya ba cutar daita zaiyi ba, idan kuma ka sake mgn abakin ranka ya afka d'akin daaka shigar daita,shi kuwa emran bai sake cewa komai ba yana jiyo ihun sajida tana kwalla ihu da gudu ya tashi ya nufi hanyar d'akin yana kiran sunanta Amman Kan ya karasa wani ya daki kansa da tsinin bunduga anan ya zube kasa a sume bai sake jin komai ba, sai farkawa yayi ya gansa kwance a d'akin ummansa su km kannensa sun zagayeshi ya dubi umma yaga fuskarta tana cikin damuwa ya sauke ganinsa Kan wasila kanwarsa yace "wasila sun kashe min sajidata ko?
Sun kashe min yar amana," amanarta mahaifinta yabani, sun kashe min ita ko?

Wasila ta girgiza kai tace "kayi hkr yaya basu kashe kowa ba sai dai sunyiwa sajida fyade , wata irin zabura yayi ya mike tsaye cikin takaici, tabbas sajida ta cucesa wata daya da yin aure Amman bata ta'ba zuwa dakinsa ba kullun akwai wulakanci datake masa daban daban akan hakinsa tace"bai isa ya kusanceta, yau gashi wani katon banza wanda bashi da imani yazo har gida kuma har cikin dakin aurenta ya keta mata alfarmar aure, tabbas hakkinsane ya kamata tun baaje koina ba.

Ya dawo da kallonsa wajen ummansa yace "umman yanzu tana ina?

Umma ta d'auke kanta daga kallonsa tace"ina zata? "Tana dakinta mana ,wannan mugun halin nata da kunya bazai barta ta zauna cikin mutane ba .

Emran bai ce komai ba ya mike cikin sanyin jiki tana can kuryar gado ta had'a kai da gwiwa tana

kukan nadama da cutar kanta datayi bisa rashin kunya wanda ba halinta bane a da.

Ya tsaya abakin gadon ya tura hannuwansa duka biyu cikin aljihun wandosa "ina ganin bamu ya kamata ki zauna kinawa kuka ba, kamata yayi ki bisu kiyi musu kuka ina tunani hk ne zaifi ,tunda su suka miki laifi ba mu ba, in km baxaki gane inda suke ba  ya zame miki tilas kiyi hakuri Dan ba zai yiwu ki cika mana kunne ba.

Sajida tayi saurin kallo emran cikin mamaki ,cikin sanyayyiyar murya daya santa dashi tun farko haduwarsu tace "amman emran ai ya kamata..
"Yi min shiru muguwa in mugunta ce ai kanki kikayiwa bamu ba, Dan hk tun kan dare yayi miki ki nemi wanda yayi miki fyade kiyi masa wannan banzar kukan naki bani ba ,yakarasa mgnr yana saukar da numfashi zai yi mgn sai km ya fasa ya juya ya fita cikin bakincikinta.

Sajida ta km fashewa da wani kuka yanzu ya zatayi kenan  ? Tarasa fu'ad tarasa emran tarasa budurcinta tyi biyu babu.....

**********
Kwana goma kenan sajida bata saka emran acikin idanunta ba ,kai ita kan tana cikin taskon rayuwa duk batagane abinda yake nufi da hkn da yayi mata ba ,ta mike jiki a sanyaye ta nufo hanyar parlour'n inda tasame shi zaune yayi tagumi itama ta nemi kujera kusa dashi ta zauna tana kallonsa kafin daga baya tayi ajiyar zuciya da numfashi atare sannan tace" emran ina son kasakeni....gabansa yayi wani irin bugawa saboda har ga Allah yana sonta ransa a matukar bace yake daita shiyasa ya shareta, amman ji mgnr banzar datake gaya masa,wani kallon wulakanci yayi mata sannan a matukar hassale yace"ai kin san yadda ake yin sake, ki dauko takarda da biyo kiga yadda bazan sakeba, aikin banza kawai yakarasa mgnr yana furzar da iska ta bakinsa.

 tsam ta mike ta shiga dakinta ta fito hannunta rike da fallen takarda da biro tazo ta mika masa gashi" ka sauwake min  yanzu na bar maka gidanka  dan konace zan cigaba da zama da kai ba daraja zanyi ba ,batare da bata lokaci ba ya amsa yasoma rubuta mata yana cewa "idan akwai gaba da gidana kije me ya dameni..

Cikin minti biyu yace "gashi ya miko mata  takardarta "na sakeke saki biyu yana gama fadar hk ya mike ya bar parlour'n yana goge zafafan hawayen da suka zowa  kuncinsa ,wannan shine karo na uku daya zubar da hawaye akanta Dan tunda yake baitaba jin bacin rai kmr na yau ba yadda ta nuna  kiri Kiri bata son zama dashi ,alhalin shiya kamata ya gujeta gashi har yanxu zuciyarsa na tsananin sonta yana fita harabar gidan yakira mahaifinta ya sheida masa daga ya kashe wayarsa da zumar barin kasar a gobe goben nan.

"dady yasoma tsarguwa aKan rashin zuwa safwan  gidansa, alhalin yana kasar , amman kiran Gaugauwan da mahaifin sajida yayi masa ya hanashi nemansa a  wannan lokacin, yana  fitowa mead na fitowa agigice saboda labarin mutuwar  auren sajida yasameta atare sukaje, koda ya isa tarin bakinciki ya iske,domin yana xuwa acp ya mika masa farar takarda da sajida ta bashi,

yana masa karin bayani "bansan abinda yarinyar take nufi dani ba?
"ta kashe aurenta batare da wani mahimmin dalili ba ," yanzu emran din ya kirani yake gaya min abinda ya faru sam banga laifinsa ba sai na wannan yar iskar yarinyar, ya dubi gefen inda take rukube yace "ba dai zaman gidan kike bukata ba gaki ga gidan ina tabbatar miki har ki kare rayuwaeki bazaki taba samun miji irin emran ba, tunda dady ya rike takadar yake zabga kalmar inna lillahi wa inna ilaihi rajiun "amman sajida baki kyautawa rayuwarki ba ke yanzu a tunaninki zaki samu kmr emran? ita dai kuka kawai take har da shesheka "dady ka rokon mun babana ya yafe min dan Allah nasan fushinsa atare dani babbar matsala ce "kinsa da hk kika ki zama a gidanki byn duk abubuwan da suka faru dake ,a wannan zamani wani nmj zai iya hkn?

fad'a sosai dady yayi mata sannan ya bawa acp hakuri da nasiha "akan hk Allah ya kaddaro babu yadda zasuyi sai adduar, sannan yace tazo ta roki mahaifinta yafiya.

akan hanyar komawarsu gida "yar baba dady yakirata "na'am babana "kwana biyu sai nake ganin wasu canje canje agame dake sannan safwan baya zuwa gurinki ,fatan  dai lfy? Dan bana son asamu matsala irin na sajida dake.

tayi shiru tana souronsa batare  datace komai ba har ya dasa ayar  mgnrsa, a zahirin gasky taso gaya masa gdkyr lamari amman ganin zuciyarsa a hannu take akan lamarin Sajida ,tayi tunanin tabari har su isa Gida.
suna isa gida direba yayi parking atare suka fito tare da dady.

"barka da cikar k'arin shrkara ....me'ad ,saitin data jiyo kenan ,wanda yasa ta waigo daidai inda tafi zaton daga nan sautin ya fito safwan tagani tsaye  ajikin motarsa yana mata murmushin mai cike da farincikinki  ganinta, da wasu kayayyakin kyauta gareta ,har da cak ,yakarso gurinsu yana murmushi ya mika mata wannan naki mead yayi mgn yana gaisar da dady cike da girmama"aiko dai  na gode sosai tare da fadada murmushin fuskarta. dady yace "dan albarka mgnrka nake acikin raina ,suka karasa cikin gidan inda sukayi masauki a babban parlour'n gidan dady ya dubeshi "ya baban naka yake yana dai lfy ko? "yana lfy ,tare da kai cup din coffe bakinsa ita km me'ad tana daga gefen hannun kujerar dady"yana Dai kula da sukari ko? "narasa dalilin dayasa ya kasa barin shan sukari gashi yana tattare da ciwo , ga itama wannan hk take kmr sha xumamu  take .

"kai dady yaushe kake barina nasha ,duk wasu abu da suka danganci sukari in dai ba wai baka kasar nan ba mutun yasamu yasha gidanmu ya dawo tmkr sanssani sojoji takarasa mgnr tana me mikowa safwan tiren hannunta "a'a ki ci kawai na gode yayi mgnr idanunsa na kanta  "dady bari na baku guri ina zuwa ta mike tashige ciki  ,inda hira ta barke atsakaninsu har inda safwan ya zayyanewa dady komai dake faruwa fada dady ya rufe shi dashi "dan me zaka min hk?" idan ka daina sonta sai akace kabata damar cigabada soyaya dan talaka dan matsiyata "dady safwan yakirasa "karka damu wallahi ina son me'ad har yanzu, na dai barta ne saboda akwai taku dana shiryawa lamarin kasan yaran yanzu sai da rarashi da dabaru ta hkn ne kadai zamu samu abinda muke so, yanxu ma hk nazo ne mu fita domin tayata murna karin shekarrata, numfasawa dady yayi duk da yaji dadin rashin janyewarsa amman hankalinsa a matukar tashe

yake banda gumi babu abinda ke fitowa daga cikin jikinsa.
Safwan ya mike dady sai kajini zamu fita daita yanzu, km Dan Allah karkayi mata zance "dady bai yunkurin cewa komai ba ya fice yacigaba da zaman tunani da mamakin abinda ya faru agurin ina ai baya jin zai iya hakura da wannan tashin hankali yana zaune yaji tashin motarsu sannan yasamu ya yunkura da kyar gefen kansa na wani irin sara kmr zai rabe gida Biyu..

Washegari

Da misalin Karfe tara na dare ranar ta yiwa fu'ad rakiya ya tafi tana dawowa ta cimma dady, zaune a parlour'n ya zabga uban tagumi yana huci takarasa ta sauke masa tagumi tace "dady'nmu lafiya ka zuba wannan uban tagumin hk? "Har nashigo bakasan nashigo ba.

Ya dubeta sosai da idanunsa da babu sauki a cikinsu yace "mead.

Bata amsa ba illa zuba masa idanu datayi saboda yadda yakira sunan nata cikin kakkausar murya.

"Waye wancan yaron da kika raka yanzu?

Ta sauke naunayen ajiyar zuciya sannan ta sunkuyar da kanta kasa batayi mgn ba saboda batasan abinda mgnr nata zai haifar ba, har da dady ya buga mata tsawa yace "Dan ubanki ba mgn nake miki ba?
cikin sarkewar murya tace "dady kayi hakuri da...daman dady ina son sanar maka ko waye shi, sunansa fu'ad kuma muna son juna dashi dan har mun yanke shawarar yin au....ji kake dau..daun..dady ya dauketa da wani gigitaccen marin har guda uku dayasa ta hantsila tayi bayan kujera tare da ganin wasu taurari sun gilma ta cikin idanunta, take ta nemi ji da ganinta tarasa, dady yana huci yacigaba "yanzu abinda zaki mana kenan? "Tozarcin dazaki mana kenan?
"Karamar yarinyar dake kinsa kan mugunta, kina kokarin yiwa iyayenki bakinciki saboda yanzu kina daukar salary mai tsoka "kina nufin bazaki auri safwan ba mai kaunarki da son farincikinki "me wannan tantirin yake dashi wanda yafi safwan?

"Ke yanzu ko kunya bakiji ba ki rasa Wanda zaki so sai wannan mai wuyan kmr marakin leman dan talakawa Dan matsiyata?

Me yake dashi ? "Me zai baki? Bashi da abinda zai baki tunda shima bai ci ya koshi ba ,wannan rayuwar kike ganin yayi miki daidai?
ga mamakin dady sai jiyo sautinta yayi" ni babu ruwana dady da wani babunsa ,matsayi ko mukami ni shi din kawai nake so, km ni bakin safwan nake ba, kawai dai bazan iya aurensa bane nabar fuad ,ni dai dady kayi hakuri ka amince na auresa shi zuciyata take so muddin ban auresa mutuwa zanyi fu'ad nake so km shine zabin zuciyata"inna lillahi wa inna ilaihi rajiun yashiga furtawa yana maimaitawa tare da maida idanunsa kan momy da hayaniyarsu tashigo daita da suhailat momy kuka ta fashe dashi ita da suhailat ganin dady na fada tana fada akan

nmj da bashi da tabbas .

dady yace yanzu nufinki bazaki auri safwan ba ko me ? Ni dai kuyi hakuri wallahi banason aurensa "ashe kuwa zaki mutu ashe kuwa lokacin mutuwarki tayi kusa matukar baki auri safwan ba sai dai ki canza uba " mayaudariya maci amanar kauna, kin ci amanar safwan ,yaron na yana sonki ba tun yau ba, muryarta cike da shesheka tace "nifa ban ci amanarsa ba amman idan kuna bukatar lallai sai ya auri yar gidan ga suhailat nan kubashi ya aura ,wani marin ya sake d'auketa dashi "kinfi shi ido ne bai ganta ba yace ke yake so shashar banza da wofi maza tashi kibani guri kafin na tsine miki albarka keda zabin naki ...

kafin ta yunkura yayi wani kwallo daita sai ga ta zube ajikin safwan da shigowarsa gidan kenan, tsam ya rungumeta jikinsa batare daya fuskanci iyayenta ba, hankalinsa yayi kololuwar tashi ganin yadda kamaninta ya sauya hawaye ne suka zubo masa lokacin dayaga nata hawayen na tsiyaya daga cikin kumburarun idanun "haba dady zaka kasheta dan tace bata sona?

"Shi fa soyayyar d nan baa ayinsa dole dan Allah dady karka sake dukanta akaina nifa tuni na hakura ya fadi hk tare da mikar da tsaye bisa kafafunta "sorry kanwata kukan ya isa hk babu me miki auren dole"Ba dai fu'ad kike so ba?
Ta daga masa da kyar "to kice ya turo iyayensa "no no karka min hk safwan ba dai iyayensa ba sai dai shi kadan sa tukun , yakarasa mgnr yana juyawa tare da goge hawaye .

suhailat kuka momy kuka hatta safwan kasa rike kukansa yayi ita kuwa uwar gayya ji take idan duk duniya nan zasu taru akanta bazata auri wanda zuciyarta bata so ba fu'ad take so kuma shi zata aura.

********

Bangaren sajida kuwa babu laifi, ta saki ranta kad'an banda murnar rabuwa da emran babu abinda take, sai dai idan ta tuna tarasa budurcinta ,ranta idan yayi dubu yakan baci, acp na zaune a d'akin baccinsa yana saurarон BBC sajida tashigo jikinta a matukar sanyaye tasamu waje ta zauna kusa dashi jigun ranta a dan jagule saboda ganin halin damuwar dayake ciki a dalilinta, kallo daya yayi mata ya dauke idanunsa akanta, sannan cigaban da saurarон BBC, ahankali tasoma magana cikin sanyayyiyar murya" baba kasaki ranka Dan Allah akan yarka, kasamu yakini akaina na maka alkwarin cewar bazan baka kunya baba , ina tabbatar maka babu wani haufi akaina ni kaina nasoma nadamar abunda na aikata ...

"me kike bukatar daga gareni sajida?

"Amatsayina na ubanki nafi kaunar ganinki karkashin inuwar aure amman kika watsa min kasa a ido "Mai kike tunani duniya zatace akaina dake karon kanki?

"Ina dai rokonka baba kayi hakuri ka kasamu yakini acikin zuciyarka akaina ni bazan sake baka

kunya ba....ko fushin karya ma bana iyawa dake driya tayi sosai  sannan ta mike ta bar d'akin cike da matsanancin farinciki mara misaltuwa .

Mmn sudais ce
[11/3, 8:27 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
MRS ADAM
( YAR MUTAN KAGARA)

Page 59 to 60

Not edit

........Sajida ta nufi d'akinta ta fad'a kan gadonta  cike da matsanancin farinciki ji take tmkr tasamu fu'ad tagama , tunani ne ya fad'o mata a rai ta mike zumbur tayi bathroom tayi wanka, ta canja kaya zuwa wasu hadaddun kananan kaya, riga da siket blue da dan ratsin yellow,tasanya abaya ta yafa mayafi  ta fito ,she look very attractive parlour'n kasa ta sauko adaidai lokacin da motocin mahaifinta suka bar gidan,sai aunty nadiya  mai aikin da'aka samo musu ce a tun sanda aurenta ya mutu a zaune ,sajida batayi mata magana ba sai ita aunty nadiyar ce tace, dining fa ya kammala .
"No karki damu aunty,zan fita ne but yanzu zan dawo takarasa mgnr idanunta na  ga duban agogon bango parloun dake walwalin haske kwan fitila ya sake kara haskawa, karfe 12 na safe yanzu ta wuce, aunty nadiya tace sai kin dawo. .
kai tsaye motarta tashiga ta nufi gidansu misna, kmr koda yaushe momyn misna tana kitchen tana aiki domin akwaita da kaunar girki, wanda hkn ke sata tuno da amminta sam itama hk take da son girkin tsiya dan wani lokacin babanta kance "Kyan 'ya tagaji uwarta amman ke sam baki d'aukota a komai ba...
Ita kuma sai tace masa" ai shi ta gado tunda ba asan nmj da shiga kitchen.  ba...
ta gaidasheta kana ta nufi dakin misna straight ,akwance ta tarar daita tana kallo a zeey world misna naganinta ta mike zaune da murnarta ta rungume sajida  ajikinta tana jin dadin ganinta cikin koshin lfy bakamar kwanakin baya ba, itama sajida ta rungumeta tana jin dadi aranta, tana matukar jin dadin yadda misna ke nuna mata kauna sajida tace "wani guri mai mahimmanci nazo ki rakani "a tunanin misna ko gurin shakatawa zasu kasancewar tasanta da son zuwa irin wuraren.

da azama misna ta diro daga kan gadonta tare da daura after dress akan riga da wando datake sanye dashi domin fitowarta wanka kenan , tare suka fito misna na rolling mayafin after dress akanta umman misna tace "sai ina adaidai wannan lokacin?
Sajida tace "umma fita zamuyi amman yanzu zamu dawo, umma tace " karfe 1 ta kusa kuje kuyi sallah sai ku zo kuyi lunch sannan rana ta fara yin sanyi sai ku fita, babu musu suka bi umarninta suka koma d'akin sukayi sallah sannan suka ci abinci Wanda sama sama sajida taci dan ta matsu bata isa inda zuciyarta ke bukatar zuwa ba,
sun fito suna yiwa umma sallama tace "karsu dade .

tafiya suke ahankali sajida ke jan motar muryarta a raunane sajida tace "kawata baki tmbayeni inda zamu ba ?
"tambayar mai zan miki byn nasan wata killa wajen shakatawa zaki.

"No kin sa'ba tsaitin tunaninki ,domin kuwa ba nan zamu ba ,kina jina ko a watanin baya da suka gabata kin sha ganina cikin tashin hankali da damuwa wanda kowa ke bukatar son sanin abinda ke damuna alokacin, amman naki bada wannan kofar ,sai dai a yau zuciyata ta aminta da nasar miki da damuwata ,bisa aminta da zuciyata tayi dake, me'ad itace wacce tafi cancata tasan matsala fiyye da kowa a duniya, sai dai al'amarin damuwata ya danganceta..kina saurarata kuwa?
"Ina jinki sajida sai dai maganarki tasanya kuzarin jikina yin rauni .

"karki damu da furucina nasanki, nasan halinki da zurfin ciki duk wuya duk runtsi akayi sirri dake baza ta'ba jinsa akoina ba shiyasa nasanyoki cikin abinda yashafi sirrikan rayuwata.
Taja numfashi ahankali ta fitar tana mai karya kwana wanda kai tsaye inda tasan fu'ad yake zama tare da abokansa ta nufa daga nesa kad'an da gurin tayi parking ta tsura masa idanunta sosai kmr zata fixgosa gareta, yana zaune tsakiyarsu kabeer suna hira wanda ba kasafai yake sanya bakinsa ciki ba.

kallonsa kawai take bata ko kifta ido, ga wani irin kalar murmushi datake masa wanda ita kanta batasan tanayi ba balle wanda ake dominsa, tsawon lokaci tana zaune tana kallonsa taji an hura mata iska a idanunta, tayi firgigib ta dawo haiyacinta tana duban misna dake zaune a gefenta ," misna a yau nake son shearing wani abu daya danganci rayuwata dake "waye wancan dake zaune tsakiyar maza uku din can sanye da t shirt fari da bakin wando?
tayi mata tmbyr tare da d'auke idanunta akanta ta maida kan fu'ad da bai san wainar da'ake toyawa ba .

Ahankali misna tace "Idan dai har idanuna nagani kmr yadda nayi zato fu'ad din me'ad ne zaune.......
"yauwa yar gari sai dai kinyi kuskuren kiransa da fu'ad din me'ad ne ,kice fu'ad din mai raboz saboda shine mutumin da zuciyata ta kamu da matsanancin kaunarsa, shine mutumin daya hanani walwala da sukuni, shi mutumin da tuaninsa ya dusashe tarin soyayyar emran acikin zuciyata ,har nake ganin duk mazan duniya mata ne shi kawai ne tsayayen nmj... "what ..kina mafarkine sajida?

"Idan mafarki kike maza ki farka "karki manta halakar dake tsakanin iyayenku daku kanka, "meyasa zakiyi hk sajida?

"Gsky banji dadin furuncinki ga abinda aminiyarki take so tmkr ranta ba .."nasani misna amman ya na iya da rayuwata, me'ad ce silar faruwar komai "itace ta nuna minshi daga kallo dayan dana masa narasa gane kaina,"yanzu dai ki taimakeni ta yaya kike ganin zan mallakesa shine abinda nafi bukata daga gareki?

Naunayen ajiyar zuciya misna ta sauke da karfi "azahirin gsky ni banida wani taimako da zan iya miki daya wuce kiyi hkr ki hakura dashi domin shine zaman lfyarmu da kwanciyar hankalinmu kafin mead tasan da wannan zance.
"haba haba sam wannan abu baiyi min dadi ba,aminan juna daku kuna son abu daya......."ki hakura dashi sajida ,a gsky banji dadin yadda kikace saboda shi kika kasa zama da emran ba domin emran masoyinki ne na hakika wanda samun irinsa ke wuya .

"shawara nake bukata daga gareki bawani zance emran ba " matukar shawara kike bukata daga gareni ki cire soyayyar fuad acikin ranki ki fawwalawa Allah komai shi yasan yadda zaiyi da al'amarinsa ,babu mamaki akwai manufar da Allah yake nufi daku ,da har yasa kuka kamu da son mutun daya, mutun dayan kum wanda ya kasance bakowa ba face talaka ...

Sajida ta daina sauraron misna ta meida hankalinta sosai gurin cigaba da kallonsa har sai dataji zuciyarta tasamu natsuwar datake bukata sannan taja motarta ta gabansa suka wuce amman bai san ko su waye ba kasancewar glass din motar baki ne, ta sauke misna a gidansu sannan ta koma gida cike da tunanin misna.
"An kuwa zata iya rabuwa dashi?

"idan ta rabu dashi tayi yaya da rayuwarta?

"kenan rayuwarta zata zamo abar tausayi babu emran babu shi babu budurcinta...... ina da sake.

Zuwan fu'ad biyu amman me'ad batayi kokarin sanar masa da sakon mahaifinta ba ,yanzu ma tsaye suke a harabar gidansu tayo masa rakiya motocin safwan suka sanyo kai cikin harabar gidan, tundaga nesan daya hangosu kirjinsa ke bugawa har zuwa sanda suka isa inda aka tanada domin ajiye motoci ,bayan an yi parking,ya yunkura da kyar yasamu ya fito sanye cikin riga da wando sai yar saman suit dake saman farar longselve, ya kirkiro dariyar dole yakaraso zuwa inda suke alokaci daya zuciyar fu'ad data safwan ta buga rasssssss atare batare da suncewa juna komai ba sai me'ad ce ta bud'e baki tana murmushi "fu'ad ga yayana safwan....safwan yayi saurin runtse idonsa sbd zuciyarsa dake na wani irin harbawa kmr zata fasa kirjinsa dan ji yayi kmr an diga masa ruwan dalma, sannan ta juya ta kalli safwan tace "yaya safwan ga fu'ad Dina....ahankali ya bud'e idanunsa ya daura akan fu'ad daya tsareshi danashi idon kana jiki a sanyaye suka mikawa junansu hannu domin gaisawa " mlm fu'ad ya

gida da aiki?
"Lfy fu'ad yace atakaice saboda ganin irin kallon kasan dayake masa mai had'e da maxurai da rainin wayo da murmushi ahad'e.
Hannunsu na sarkafe cikin juna safwan yace "gsky kanwata kin iya zabe ..."allah ko yaya?
"Kwarai kuwa...da gaske, kin kuwa gaya masa sakon dady ?

Numfashi taja ta sauke da kyar kana tace"Abinda nake shirin yi kenan kashigo "ok kiyi kokari ki sanar masa idan da wata matsala ki hanzarta sanar min "ok yaya na gode da kulawarka .

"No karki damu kanwata any for you ya juya zuciyarsa na farfasa, ya nufi cikin gidan kmr zai kifa tsabar duhun da zuciyarsa tashiga har yayi dayasanin zuwansa gidan bayansa fu'ad ya tsurawa idanu duk bai jiyo ba yana iya ganin yadda numfashinsa ke fita da karfi.
byn shigarsa cikin gidan fu'ad yayi mugu mugun tsareta da ido "kikace wannan mutumin yayanki ne ?
"eh tabashi amsa tana kallon cikin idanunsa.

"Uwa daya uba daya?

" no D'an aminin kuma mai gidan dady ne,"wani abu ne ?girgiza mata kai kawai yayi "yanzu dai kaji da kunnenka dady nason ganinka ya kenan?
"Ok badamuwa zuwa yaushe yake son ganina?
"anytime you are free ,"ok mubarshi nest week saboda gabadaya satinan zanyi busy kema bazaki samu damar ganina ba har sai nagama abinda nake, jin hk yasa ta narke masa fuska kmr zatayi kuka "har next week fa kace , kasan kuwa yadda nake ji idan nayi kwana daya ban sanyaka acikin idanuna ba ?
"Ji nake kmr ana fixgar numfashina ni dai kasan yadda zakayi, ko kazo ko sau biyu ne naganka ,ko kuma ni na sameka inda kake.
Murmushin yayi sannan yasoma rarrashinta sai daya samu ta dawo normal sannan ya wuce.

Kwanakin nan gbdy acikin kunci da damuwa mead tayisa sakamakon rashin ganinsa Dan hk randa yazo da zumar ganin mahaifinta tana ganinsa bata tsaya wata wata ba ta rungume shi ajikinta tana farinciki ,saurin d'auke numfashinsa yayi saboda jin diran nonuwanta bisa kirjinsa atare sukaji tmkr
Wani irin abu yana masu yawo a gabadaya ilahirin jikinsun me kama da shocking wanda take ya haddasawa nata kirjin bugawa yayinda shi km a take kwakwaluwarsa ta d'auki caji , cikin wani irin murya yace " my love you kinzo min da wani irin salo mai tsayawa a zuciya, kar da kisa nayi abun kunya a gidan siriki, a yadda yayi maganar bakaramin rud'ata yayi ba ....jin yanayinsa nason canzawa yasashi zareta ajikinsa yana fitar da wani irin numfashi da kyar da sauri ta ita kuma ta fita daga cikin parlour fuskarta cike da fara'a, itama wani irin kalar numfashi take ,a yanzu ji take ina ma amatsayin mallakinsa take.

"tun bayan fitarta fu'ad yafara jin caji ajikinsa, ahankali yake jin wani feelings na bijirowa a gangar jikinsa ,lips dinsa na kasa ya ciza da matukar karfi kmr zai datse harshensa, sannan

yayi saurin batsar da abinda yake jin yana masa yawo ajiki kana yacigaba da zaman jiranta.

Cikin wasu yan mintunoni da basu wuce biyar ba ta sake dawowa karamin parlour'n dayake zaune zaman jiranta "taso muje zuwa ga babban parlour'n dady inda anan dady zai ganka ,bakinsa d'auke da sallama yashigo cikin hadadden parlour'n ,inda suka iske parlour'n empty babu kowa cikinsa sai k'aran tv plazma dake manne da bangon parlour'n yana aiki acikinsa hannunsa ta kamo zuwa kan kujera "ka zauna yanzu dady zai shigo, gyaran murya yayi mata batare da yace komai ba illa idanunsa dake yawo a sansar jikinta, ta juya cike da rausaya ta nufi cikin gidan tana daddana number safwan kira daya ya dauka "ya'akayi ne kanwata? "kazo yanzu ga fu'ad yazo dan Allah nafi son duk abinda za'a yi kana nan domin nasan zakayi controlling din dady . Tunda tasoma mgn numfashinsa ya nemi dauke amman yayi saurin sanyawa jikinsa jarumtar cewar"ok karki damu gani zuwa just give me some mint.

byn kmr minti 30 sai ga dady yashigo parlour'n yana dingisawa fu'ad naganinsa yayi saurin mikewa tsaye cike da girmamawa yana mai gaishe dashi "uhm kawai dady ya iya cewa sannam ya zauna tare da cewa "kana iya zama.

fu'ad ya Zauna zuciyarsa na d'ardar dan ganin yadda mahaifin me'ad ke kallonsa kasa da sama wanda hkn yake nuna alamun bai yaba da ganinsa ba .
yayinda me'ad tasake dawowa parlour'n tare da tsayawa a bakin kofar shigowa ta tsurawa fu'ad ido dady ya yi gyaran murya kana yace "me za'a kawo maka?
shayi ko lemo ko... "no no dady ba sai an kawo min komai ba ,nagode "uhmm kasha wani abu mana kai kuwa ?

cike da in ina fuad yace "to ruwa ma kawai ya isa .

"ruwa fa?
mahaifin me'ad ya fad'a yana jinjina kai .fuad yace eh shi kawai ya isa.
kai kuwa "ya zakazo gidan masu abun kace ruwa kawai zaka sha any how mead kawowa bakonki abinda ya bukata ta juya, jiki a sanyaye ta nufi kitchen dan sam bataji dadi irin tarban da dady yayi masa ba, byn fitarta dady ya fuskanci fu'ad yana tsare idanu tun kafin yasoma magana safwan yashigo cikin parlour'n cikin sallama sanye cikin kananun kaya wad'anda suka mugun amsar jikinsa sai kamshi dadden turarensa yake bazawa ya gaishe da dady sannan yakarasa ya mikawa fu'ad. Hannu"barkanmu da warhk?
Shima fu'ad Hannu ya mika masa suka gaisa sannan ya samun guri ya zauna shima yana fuskantar fu'ad , yasanya hannunsa daya yayi tagumi yana cigaba da kallon fu'ad "me yafi shi har da me'ad ta zabesa ta barshi?
kyau ilimi tattare makudan kudaden da shi kansa bai san adadinsu ba, duk yafi wannan dake zaune a gabanshi..

"a ina kake da zama sautin muryar dady ta karade parlour'n zuwa cikin dodon kunne fu'ad "ina zaune a gbegulori dake kan titi capito road "uhmm anan kake zaune tare da iyayenka?
"eh ana nake tare da kakata dan tun daga haihuwata mahaifiyata ta rasu byn wani lokaci

shima mahaifina ya rasu yanzu dai ina tare da kakata nake zaune.

"ayya ina mai jajanta maka Allah ya jikansu.

"Ameen na.. na gode dady. Cikin hk mead tashigo ta ajiye tire dake dauke da nauikan abinci ta juya tanayiwa safwan alamar ya taimaka komai yazo karshe sannan tabar gurin.

Dady yacigaba"da dukan alamum kakarka tana riritaka dayawa ?
fu'ad yayi muushin jin dadi tare da sakin jikinsa kad'an dan da adirice yake ,sannan yace azahirin gsky hk ne Sabod tana matsananci sona sosai "ya isa me kakeyi ahalin yanzu aiki ko karatu?
"gsky babu abinda nake ahalin yanzu ina dai kan neman aiki a tun bayan dana gama digri Dina Amman har yanzu ban samu ba shiyasa na yanke shawarar soma sana'ar kasuwancin..

"idan na fahimci maganarka baka Da aikin yi, kai mutun ne dakayi karatu amman baka da tsayayen aikin yi, safwan kana ji fa da sanar da bai kai ga samu ba yake neman diyar babban gida ko dai baiyi karatun bane?

"a'a dady digre gareni nasan zuwa yanzu nasan abinda kake son kace amman na rantse maka da Allah zan kular maka da me'ad sosai fiyye da yadda kake tsammani "uhm kace kayi karatu geo ko history ka karanta? "aa kasuwanci na karanta zaka iya kallon abun wani iri Amman muddin me'ad na tare dani kusan babu abinda bazan iya mata ba, ko maye zanyi domim na bata farinciki da.....
"ya isa hk malam dady ya katseshi yana mazurai da "Karka cikani da wannan surutain banza da wofi "meye matsayinka? "kai fa ka kasance yaro ne mara zuciyar neman na kansa wanda kakarsa ke ciyar dashi tare da bashi kudin kashewa, yayi gantali yayi can yayi gantali yayi nan rayuwar kenan wadan nan takalman da kayan jikinka da machine din dakazo dashi da kudin wa kasiya? mu dubi komai a zahirance mana sannan musa gsky a hurumunta mana "ta yaya kake tunani zan dauki diyata me'ad nabawa mai matacciyar zuciya irinka?
"na d'auki diyar dana fi so na aurawa ga wanda gabadaya rayuwarsa sipili ce a tunaninka hkn zai yiwu?

fu'ad da kansa ke sunkuye ya dago a matukar firgice yana duban dady kamin yayi magana dady yace "ysushe kasan me'ad? "karkari tsawon wata shida.
ran fu'ad ya sake kaiwa kololuwa gurin tashi ganin ga safwan zaune amman yaki takawa dady burki gashi dady bashi alamun saida zancesa hkn kuma still safwan na kallonsa A wulakance yana masa murmushin da bai san ko na mene ba, ya bude bakinsa da kyar yace "yallabai ni dai nasan idan kabani auren yarinyaka zansata farinciki "me kake bukata atare da mutun adali ince na natsuwa nagarta mai kamun kai mara shaye2, to duk ina cikin abinda na lisafa maka, ince duka matsalar akan ta rashin aikin yi ce? "ka zuba ido kagani nan gaba da kayan aiki zakaganni ,zan tabbatar maka da kai.. "meye abun tabbatarwa yaro byn gaka agabana da shirman rayuwarka zaka tabvatar min da kanka ko me?
dady yakarasa mgnr yana murmushi safwan kaji fa, "wai shin wani shirin wasan kwaikwayo

akeyi anan ne ko me?
"wai tabbatar da kansa yake son yi wa uban me'ad yakarasa mgnr yana dry "babban magana kenan "mai yawo a gari babu aiki yake son tabbatar da kansa shi dai safwan bai ce ta tafar ba illa dryr dayake ta kunshewa saboda gabadaya maganganun dady sun matukar yi masa dadi da sanyaya ransa.. "kasani diyata me'ad nada alkwarin auren wani akanta attajiri Wanda ya fika a komai na rayuwar duniya dan hk kwarya tabi kwarya a gidan baka da matar aure period mgn ta karshe kar na sake ganin kafarka gidana..

fu'ad yasoma kokarin mike tsaye "sai anjima yallabai nagode da lokacin daka bani wani irin kallon kaskanci dady yake binsa dashi yayinda har wannan lokacin fuskar safwan kumshe take da dryr mugunta.

jiki a sanyaye fu'ad yakarasa mikewa yana gyara rigarsa ta baya sannan yasoma daga kafafunsa kmr kazar da kwai ya fashewa aciki ya nufi inda yayi parking din machin din kabeer daya aro, ya hau ya zauna amman ya kasa tadashi sai dai ya kwantar da kansa kan mashin din, bai yi auni va sai jin danshi yayi akan fuskasa ya mika hannunsa ya shafo hawaye ne, shi kansa yayi makakin dalilin zubarsu akan mead ne da zai rasa ko kuma akan tozarcin daaka masa ne ?
yafi minti talatin a haka kamin yasoma kokarin tayar da machine ,masu gadi suka bude masa kofar get ya fita, ya yarda bazai samu me'ad ba har abada. shi ba aure yadamu dashi ba da wuri kasancewarsa saurayi da bai taba aure ba, km ba shashanci yake ba balle ya tancance yanada bukatar mace yanzu ko aa, me'ad din kawai yake so, soyayyarta ce tasanyasa son yin aure a halin yanzu.

meyasa mead tayi masa hk ?"me yasa ta boye masa akwai alkwarin auren wani akanta? tayi masa wasa da zuciya da hankali har ya iso gida bai san inda hankalinsa yake ba kuma tmbyr dayake son yayi mata kenan "hakika tayi masa wasa da zuciya, dan bazai iya cewar ta yaudaresa ba ,dan ya yarda da son datake masa na gaske ne, sannan na tsakani da Allah ..

Da yammacin ranar sai ga mead tazo gidansu sakamakon abinda safwan yagaya mata daya yayi masa, da kunneta km taji lokacin da safwan kebawa dady hkr da kokarin shawo kansa daya amince da auren albashi sai su tsaya masa yasamu aiki,inda ta Isamu fuad zaune kofar gidan inna ,yana kallon sararin samaniya, da yadda hadari ya hado agarin,a zahirin gsky zaka dauka yana nazarta yanayin zuwan ruwan saman ne, amman sam abun ba hk yake ba tunanin rayuwa yake, tunani yadda rayuwa take shirin tagaliliya dashi yake, har sanda takaraso garesa bai sani ba sai jin laulausar tafin hannuta yayi saman nashi, wanda hkn yasa shi juyowa ahankali tare da sauke naunayen ajiyar zuciya ganin itace ,sai dai ganinta ya zafafa mikin dake cikin zuciyarsa, atake ransa ya sake dugunzuma, ya cire hannunsa daga nata yana mai basarwa sannan muryarsa a dakile yace"mai ya kawo gareni?
"Dan Allah kibar nan tun raina bai gama dagulewa akanki , banason kusancina dake."to saboda meye fu'ad? "Saboda kin kai ni ga mahaifinki ya tsarkafeni da sarkafaffun tmbayoyinsa marasa maana da tushe , ya bata amsa a matukar fusace yana mai maida idanunsa sama jin har ansoma yayyafi.

"karkayi wannan maganar fu'ad daman irin tambayar da iyaye sukayi kenan , kasa kanka amatsayin mahaifina ka duba Alamarin....dan Allah dan Annabi malam ya isa hk kawai kin gayuaceni zuwa gidanku dan aci mutuncina akaremin tanadi da tozarci ,shi kuma wannan tantirin safwan din yana zaune agurin yana min dariya "ka daina magana ta shirme mana safwan mutumin kirki ne karka tuhumaishi acikin wannan matsalar "oho ni kuma mutumin banza wanda bayada aikin yi, dan jagaliyar titi daya fada soyayya da yar babban gida, in da kace masu kudi kawai suke da alhakin da yancin fadawa soyayya ,da soyayya tayi karanci a duniya, fuad ka daina daga murya mana kana jawo hankali mutane garemu.
"Gara na daga sautin muryarta ansa kece kebibiyata har kikayi silar da yau aka tozartani, banki kowa yafito yasani ba, kece kika tallata min kanki akan soyayyarki ina zaman zamana cikin rufin asirin Allah "dan Allah karkayi magana cikin fushi har da kake wani shir...datse harshenta tayi da karfi takasa karasawa.

".Kwarai kuwa dole kice hk tunda kina son kare gidanku da ahlinki, an wulakantani sam baki damu ba suna kina sona kin wani kwaso shirmen jikinki kinzo kina kara gaya min maganganu banza, sai danazo na fuskanci mahaifinki nagane irin kuskuren danayi ,ba dai aiki ba,to bazan nemanba ,km Zan aureki da rashin aikin nawa domin na tabbatarwa mahaifinki ko babu aiki zan iya kula dake yadda yakamata .
wai mgnr tawa ahlin gidanku suka meida abar dry, wanda wannnan abun daaka min ina da tabbacin safwan yana da hannu aciki kuma shine ya ziga babanki akan hk.

"Fu'ad ka daina magana hk mana, domin magana cikin fushi bashi da fa'ida, sannan ni ina da tabbacin babu ruwan safwan cikin wannan matsalar, "ai magana ce ta gsky idan tazo a fadeta baka da aikin yi, ko kana da? Ta jiho masa tambayar tana kallon cikin kwayar idanunsa wani irin kallo yayi mata ..

"Kuji wawiya da wata wawiyar magana ya furta hkn adaidai lokacin da ruwan sama ya sauko kmr da bakin kwarya,yacigaba "ai ban tabasanin cewar ke din shasha bace sai yau, tun farko da kika nacewa sona aikinsa bana aiki ko baki sani ba ? Shima yayi mata tmbyr yana tsare gira da kamewa "oho zuwa yanzu soyayya da mutuntakan dake tsakaninki da safwan zai iya sa ki mance hk ba..?
"Bari kiji nagaya miki abinda bakisani ba nasan komai tsakaninki da safwan, tundaga farko har karshe ko last week da kuka fita yawon celebrating din birthday dinki ina sane...nasan kunyi soyayya dashi ...,a yanzu kuma yaudararki yake,da furuncin ya janye batun aurenki, kina sona zaki aureni amatsayin danake. .ki tabbatar da kin rabu da safwan rabuwa ta har abada, idan ba hk ba kisawa zuciyarki fu'ad ba rabonki bane na wata ne ,yana gama fadar hk ya juya yasoma daga kafafunsa.
jikinta na rawa tabiyo bayansa tana kiran sunansa fuad ka tsaya dan Allah ...
Bai tsaya ba har sanda ta isa garesa ta riko hannunsa ya juyo a fusace yana dubanta "idan na tsaya na miki meye?"narigada nagama magana period sannan ki tsaya daga nan domin idan kikayi gangancin biyoni,har kikayi silar shigar innata damuwa zan miki abinda bakiyi expecting dinsa daga gareni ba.

juyowar nan da zaiyi yasanya hannuwansa ya goge fuskarsa sai yaga innarsa tsaye a bakin kofa tana kallonsu ,wacce tun da zu take tsaye agurin juyawa tayi cikin gidan, nan shima yashiga ya samu guri ya zauna agefen gadonta batare daya cire kayan jikinsa ba,inna dake sharar hawaye takaraso garesa ta dafa kafadarsa ahankali sannan tasanya dayan hanunta bisa kansa, inda gbdy ta fashe da wani irin kuka mai cin rai tare da rungume kansa a kirjinta shima kukan yake son yi amman ya dake.

***********

Yadda fu'ad ya kwana bai runtsa ba ,haka mead ta kwana juyi akan gadon ta,duk inda ya juya maganganun mahaifinta ke masa kuwa ya yarda ya amince ya saduda ya amince mead ta haramta garesa, soyayyarsu tazama mafarki mai dadi irin wanda dan adam kanyi, ya farka yana mai cizan yatsar kasancewarsa, tunda har mahaifinta yayi wannan hukuncin, dreams are conceived but not all dream 'a are born alive some are aborted, others are stillborn ya juya ya kalli su jabeer baccinsu kawai suke cikin sukuni alamun basa cikin matsalar rayuwa sannan basu san menen kalmar da ake cewa so ba .
Zaune suka iske doctor ya tasa nasreen gaba yana dubanta, da sauri tayo gurin nasreen tana kiran sunan "doc......
Al kuwa nasreen ta zabura ta mike zaune tare da dakatar da uwar ta hanyar cewa "go back mummy I don't want to see you, plz go !!!! Shi kansa doctor sai dayayi shock a zaune agurin,wannan abinda me faruwa gaske ne ko mafarki ne ?
A matukar firgice me'ad da fu'ad suka shiga kallon kallo atsakaninsu suna zare ido. da kyar fu'ad yayi karfin halin cewa "did you hear her? Yana kallon kwayar idanun me'ad.
"Did you hear what she said?
Runtse idanunta tayi hawayen bakinciki biyu biyu na gangaro mata, magana take son yi Amman ko tace zatayi maganar bazata fito ba saboda cikin halin tashin hankali datake ciki ,Dan haka ta bud'e idanunta dake cike da ruwan hawaye ta d'aurasu Akan yarinyarta tana mata kallon karta mata .....
Hawaye sha'be sha'be a kwance a kuncinta nasreen ta sake cewa "I don't want to see any of you here, Plz just go...
doctor ya d'ago ya dubesu yana girgiza kai sannan yace "fatan kunji abinda yarinyarku tace ?
"Yanxu dai kuje daga waje tukun am coming to see you guy's.
"Doctor including me ..?
Fu'ad ya fad'a cike da tsantsar mamaki da tashin hankali, yana duban nasreen dinsa.
a matukar fusace doctor yace "you guy's leave plz.."both of you should leave! Me'ad ta nuna

kofar fita idanunta na kan nasreen dake kuka ,da hannun doctor ya nuna musu hanya alamun hk yake nufi .
jiki a sanyaye me'ad tasoma d'aga kafafunta still idanunta na Kan diyarta wanda zuwa lokacin tuni fu'ad ya bar d'akin dafe da goshinsa .
bayan fitarsu doctor ya sauke naunayen ajiyar zuciya yana me d'aura hannunsa akan bakinsa "ammmmm nasreen ya furta ahankali,"just calm down okay.
"I understand you Amman meyasa kikayiwa iyayenki hk alhalin suna matsanancin kaunar suga kin rayu?
"No doctor don't say that basa sona wallahi ,sun fi son na mutuwa .........
"Kullun cikin fad'a suke a tun sanda kace cikinsu daya zai ajiye aikinsa ,nan tashiga koro masa komai tun daga farko har zuwa abinda idanunta ya gane mata momy'nta na yunkurin aikatawa "shiyasa ni dai ka taimakeni kabani poison na sha na mutu .......
"doctor ya girgiza kansa kawai sannan yace "ki daina furta wannan kalmar bata da kyau ga duk wani cikakken Muslim ,"ko bakinsa duk Wanda yayi yunkurin kashe kansa da kansa amatsayin kafuri zai tashi agurin Allah ba ?
"Dan haka karki sake furta wannan kalmar bata da kyau okay,?
Ta matso wasu hawayen batare da tace komai ba," ya Mike ya bar d'akin zuwa office dinsa, inda yasa ayi masa kiransu ,da gudu me'ad tashigo office din tana goge hawayen idanunta.

Zaune suke agaban doctor gabadayansu a firgici suke, kowanensu da abinda zuciyarsa ke kismawa Akan wannan kiran da likita yayi musu, doctor ya zuba uban tagumin yana sake tunanin zantuttukan nasreen kalma daya ce tafi kowace kalma muni da daci garesa kmr "doctor give me poison I want to die ......
"Wannan Kalmar tayi matukar gigitashi da tsaya masa arai, tsawon minti goma suna zaune still doctor yaki ce musu k'ala Me'ad ta matsu ta matsu bataji abinda doctor yakirasu dominsa ba ,yayinda zuciyarta ta dinga tsinkewa da rawa rawa ,banda zare idanuwa babu abinda take ,ganin shirun yayi yawa yasa me'ad kasa hakuri tace "doctor, what's exactly happened to my child?
"Ina jin tsoro doctor kar wani abu ya sameta ,I think ba ciwonta bane ..? Doctor yayi shr yacigaba da jimami yana ta'be baki .
"doctor wai meke faruwa ne kabarmu zaune cikin tashin hankali Dan Allah ka sanar mana da abinda ke faruwa da yarinyarmu ?
Inji cewar fu'ad.
Ahankali doctor ya kallesu kana ya dukar kansa na minti biyu sannan ya sake d'agowa yace "do you guy's want to know what is going on?
Da sauri suka had'a baki gurin cewa "yes muna bukatar sani .

"Both of you are not good parent to child ." what ?
me'ad ta furta tare da barin bakinta a bud'e .
Fu'ad yace "har dani kake nufi ko da wannan datake zaune kake mgn ?
Doctor yace "dukanku nake mgn , sannan duk inda aka kira iyayen arziki masu son yaransu da son farincikinsu ,idan irinku suka fito wallahi kamata yayi aka maku ayi muku dukan mutuwa ,ko kuma ad'aureku ajikin kujera har ku mutu .... "what suka furta atare?

" yes I mean it inji cewar doctor yana masu kallon banza "saboda gabadayanku mugaye ne sannan baku da halin kirki you are not a good parent at all...for ten years old girl to be considering death as an option..
"what doctor ?
Inji cewar me'ad gabanta na wani irin mahaukacin bugu "yes she ask me to give her poison because her parents do not like her yet you call yourself parents.
"kai kai doctor it can be possible ya dafe goshinsa yana girgiza kai..numfashi me'ad tasoma ja kmr me cutar asm "um umm uhmm sai kuma kuka ya kwace mata, take kuma jikinta ya sake d'aukar rawa ta juya ahankali tana zabgawa fu'ad harara had'e da kallon banza .
bai kulata ba illa muryarsa cike da in ina yace "doctor can I go see her and talk to her?
"You can't see her right now..
"ah!
Suka furta atare suna duban doctor.
Doctor yace "am telling you you guy's can't see her.

Me'ad ta watsawa fu'ad wata katuwar harara kmr idanunta zasuyo waje "ai kaga abinda kayi ko ,kaga abinda sanadin matsalarka zata haifar ko ?
"Bari kaji in gaya maka wani sabon labari ,wallahi wallahi idan wani abu yasamu yarinyarta bazan yarda ba ,Idan kuma ta mutu heeeeeeeee....."kai dai kayi adduar kar wani abu yasamu yarinyarta kawai ,Dan idan wani abu ya ta'ba Ifyrta sakamakon abinda ya faru kasawa ranka kaima mutuwa zakayi......dan wallahi tallahi kotu ce zata rabu da kai ,takarasa mgnr tana kuka "ni nasan wahalar Dana sha akanta tun daga d'aukar cikinta har zuwa yau din nan .."haihuwarta kawai kikayi Amman na fiki son nasreen da bukatar Ita araye "uhmmmmm uhmmmmm!!! Tashiga sauke ajiyar zuciya tana kuka tana jijiga kafarta.

"plz can I go and see her plz? "I need to talk to my daughter inji cewar fu'ad da gbdy ya susuce kuka kawai yake son yi ko shima zai ji sanyi aransa, "nasreen dinsa ke adduar mutuwa, tana bukatar mutuwa saboda matsalar shi da mahaifiyarta..wannan wace irin rayuwa ce?
,"ya Allah karka kashe min ita, ina sonta , ya dafe kanshi tare da dukar da kasa gbdy yasoma jin duniyar tana jujjuyawa dashi "wani irin zunubi ya aikatawa ubangijinsa haka,da abubuwa suke faruwa dashi hk?
Zuciyarsa ce tayi saurin kwa'bersa" karkayi sabo fu'ad kai muslimi da kasan da kaddara me kyau ko akasin hk, ka d'auka duk abinda ke faruwa dakai kaddaraka ce tazo da hkn wanda bazaka ta'ba gogewa ba ,a sukwane ya d'ago idanunsa da suka yi jawur tmkr garwashin wuta yana duban me'ad ..

"Ba yanzu bane lokacin kukanka fu'ad, kajira lokacin da yarinyata zata mutu, ranar zaka sha kallon abinda zai faru atsakaninmu," doctor idan duk damuwar nasreen ni ake cewa naji na yarda na Amince, but na yau babu hannu ciki shine musababbin faruwar komai, Amman wallahi nasreen Dina ta mutu sai duniya tasan damu, Dan ina tabbatar maka gidan tv daban daban za'a dinga watso labaranmu.
"just imagine doctor ya fad'a yana mata kallon banza "that was exactly what I was still talking about, "is this the way you supposed to be doing now?

Tayi saurin girgiza masa kai tana zaro idanuwa "see .. both of you can't see her "
ah fu'ad ya furta yana me bud'e baki "yes wallahi bazan bari ku ganta ba ,hk kawai kuje da maseefarku ku k'arasa yarinya mara lfy ......"Dan girman Allah doctor kabarni ni kad'ai naje naganta nasan zata saurareni, after all ina bukatar ganin yanayin jikinta,ina bukatar jin dumin jikin yarinta.."duka acikin babu wanda zakayi ,ku tashi ku tafi plz ina da abubuwan yi ...

Tsam me'ad ta tashi tasoma d'aga kafafunta tmkr wace bata da laka ajikinta,while hawaye na tsiyaya a saman kuncinta har ta iso harabar asibitin, daya wadatu da hasken wutar lantarki tasamu guri daga gefe ta zauna a kasa still tana cigaba da zubar da hawaye , ahankali ta sanya hannuwanta duka ta rungume jikinta tare d'aga idanunta sama tana kallon sararin samaniya, tana tunanin rayuwa kuka take sosai kmr ranta zai fita ,"wayyohlly Allah nah... ..ina zan saka raina naji dadi?
"Ya Allah ka d'auki rayuwata na huta da ganin tarin bakinciki dake kokarin kusanto rayuwata,
"Allah na rokeka ka kasheni kafin naga abinda fu'ad yake shirin aikata min ....
tana cikin wannan halin fu'ad ya fito yana dube duben nemanta can ya hangota zaune takure da jikinta tana kuka .
ya runtse idanunsa sannan ya k'araso inda take ya tsaya akanta "mead ya kira sunanta da sanyayyiyar murya "me yasa kika barni kika dawo nan kina kuka? Wannan karon Yayi mgnr muryarsa cike da tausayawa sannan ahankali.
Ya matso sosai kusa daita tare da durkusawa agabanta "why did you left me there and weeping outside ?

Bata kula shi ba tacigaba da kukanta tana goge hawaye, wasu na sake gangarowa ya sake matsota sosai kmr zai shige jikinta, "don't do this to me plz ,the doctor has promised us that she will be fine let's keep praying for her, after all ,we are not god dole mujira hukuncin Allah garemu ...
ya kamo laulausar tafin hannuta cikin nasa "dan Allah ki natsu ki kwantar da hankalinki babu abinda zai sameta "am..am scared I don't want lose her takarasa mgnr tana mai sakin wani irin kuka ..
ta kwanto jikinsa tana kuka yanyota yayi jikinsa ya rungumeta tsam ya manna fuskarta daidai saitin zuciyarsa dake bugawa, yasoma rarrashinta "you are not going to lose her ,okay? " InshaAllahu zamu rayu tare da diyarmu, ki daina kawo mata mutuwa, Dan zamu iya mutuwa mu barta babu ruwan Allah.
Cikin halin datake ciki , ta tuno da abinda yake son shuka mata, ai batare da 'bata lokaci ba ta fixge jikinta daga nashi ta Mike tsaye tana kallonsa kafin daga bisani tasoma tafiya cikin sauri tana kuka ,shima ya biyo bayanta yana kiran sunanta "mead ina zaki, ki dawo idan gida zaki na kaiki. tayi masa banza tacigaba da tafiyarta har takarasa bakin titi tana kokarin tsaida abun hawa "karki soma me'ad..karki soma shiga kowace mota.
"Zan shiga so that idan na shiga ka sakeni ,wanda daman abinda nafi bukata kenan daga gareka tana fad'ar hk ta juya a fusace daidai lokacin da wani me adaidaita ya tsaya agabanta yana tmbyr inda zata.
Tun kafin ta bud'e bakinta fu'ad yayi saurin cewa "ka wuce kawai tare muke daita, idan km kayi k'ok'arin d'aukarta sai dai wani ba kai ba ,yakarasa mgnr ya kamo hannuta da niyyar komawa

cikin hospital, tasoma turturjewa" kabarni  fu'ad banason abinda kake min, "me yasa kake son kasheni tun kwanakina basu cika ba ..?
"Kece kike son kashe kanki da kanki ,amman karki damu bazaki mutu yanzu ba ,har sai kinga aurena da matana guda biyu.
"Ina ai bazan so ki mutu tun  yanzu ba  matata, kece fa kikace am your husband for life, har tsufa muna tare ko kin manta da kin furta hkn ?
"Ki tuna idan kuma kin manta gashin na tuna miki,aurena da 'yammatana babu fashi ,zance saki sakanina dake babu shi ,Dan HK muje kisamu natsuwar zuciya.
Ta tattara iya karfinta ta fixge daga rikon da yayi mata ta juya cikin sauri tayi tafiyarta ,sai dai taku daya zuwa biyu yayi ya damketa tare da yin sama daita jama'a kan titi da idanunsu ke kansu suka bisu da kallo, har sanda ya sanyata cikin mota shima yashiga ya kule yana me fuskantarta.muryarsa a matukar sanyaye yace "Keleni me'ad, sannan ki natsu kibani aron hankalinki muyi mgn ta fahimta ."matukar Akan zance aurenka ne bazan ta'ba fahimtarka ba ,ince ba'ayin aure dole?"Dan Allah dan Annabi ka rabu dani da nace ina sonka zan rayu da kai yanzu kuma banayi kaje byn sajida da najma ka k'ara wasu ,ni dai me'ad ban sake komawa aurnka Allah ya had'a kowa da rabon...bata k'arasa ba taji ya buge mata baki "idan kika sake furta wannan kalmar zan zaki had'u da fushina da baki ta'ba ganin ba ,yanzu dai mu ajiye komai har sanda nasreen zata samu lfy aure kuma babu fashi zanyi ,let me tell you good news, ki godewa Allah watakila najma kawai zan aura saboda mahaifin sajida yaki amincewa da batun auren ..tunda yasoma mgnr take kuka har yayi shiru,tana zaune ta dawo tmkr mutun mutumi ,jinta na neman d'aukewa ,Allah sarki a she hk rayuwa zata zo mata?
Ganin hankalinta na neman gushewa yasa ya matsota ya kamo hannuwanta duka cikin nasa yasoma massaging dinsu yana kallon cikin kwayar idanunta dake tsiyayar hawaye, Yasan tana mugu mugun son shi ,sannan yana da tabbacin duk duniya babu macen dazata so shi fiyye daita ..ahankali ya janyota jikinsa yana k'ok'arin rungumeta ,ta kasa saida shi saboda zuwa lokacin gbdy jikinta bai da laka kallonsa kawai kmr wata ta'ba'bbiya ,tsawon lokaci suna manne da juna batare da suncewa juna k'ala ba ,kusan a mota suka kwana makale da juna, sai dai mead bata runtsa ba kwance kawai take ajikinsa numfashi kawai take iya fitarwa shima Dan tasan dole ya fito tunda akwai rai ajikinta.

******
Washegari babu laifi nasreen tasamu natsuwar zuciya, daman firgici da tsoro ne ya haifar mata da suman datayi , sai dai fad'uwar datayi kasa yasa hannunta na hagu ya D'an bugu, har gurin ya kunbura abinka da sickle  cell k'ashinsu bashi da kwari, koman yaya suka ji ciwo yanzu gurin zai kunbura. suna zaune tare daita kowanensu na rike  da hannunta daya ,suna k'ok'arin bata kulawa doctor yashigo dubata yanayin jikinta, sosai ya ji dadin yadda ya isketa atsakiyarsu me'ad na bata apple abaki sannan tayi mata hira, irin sanya farinciki.
Tashi sukayi atare suka tsaya ajikin bango, batare da sun kalli junansu ba,doctor yashiga aikin duba jikin nasreen yana mata wasa.

Kwana nasreen biyu a hospital doctor yabasu sallama, lokacin fu'ad bai nan yana can tare da me gidansa, kai tsaye me'ad hanyar gidansu ta dauka da nasreen, Dan bata jin zata koma gidansu da sunan cigaba da rayuwa fu'ad, zuciyarta cike da bakinciki, wai shin me zatawa

sajida da najma arayuwa ta huce?
Kodayake bata jin najma, tafi jin sajida Dan a yanzu ta sauya shawarar akanta ,Dan har in takashe sajida, bata more rayuwa ba ,tunda bata zauna a duniyar ba balle taga bakinciki, yanzu tafi yarda da shawarar zuciyarta wanda babu tantama abinda zata mata har ta mutu sajida bazata ta'ba mantawa daita ba,gaba idan ance ta kalli mijin wata tace tana so ,ko taci amanar wanda ya Aminta daita bazatayi ba ,murmushin mugunta tayi  adaidai lokacin da ta iso bakin get din gidansu inda tashiga matsa hon, madu gadi na ganin motarta ce suka hau k'ok'arin bud'ewa  cikin rawar jiki, tasanya hancin motarta tana hura hanci, tayi parking a inda aka tanada domin ajiye motoci sannan ta fito har lokacin fuskarta a murtuke take, ta dubi nasreen dake zaune tana kallonta, dan ita a tunanita gidansu suka nufa sai kuma taga momy'nta tayo gidan kakaninta dasu, me'ad ta Dan saki fuskarta kana tace "bby fito muje ...

*"Uhmmm to ga dai me'ad an kwaso jiki an dawo gida uba...ko yaya   zatak'aya da mahaifinta ?" ko kuwa ta manta furucinsa akanta ne?*

Mmn sudais ce
[11/3, 8:29 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
FAIZA HAMMADU BARAU
(YAR NUMAN)

Page 77

......nasreen taji abinda momy'ta ta fad'a sarai amman taki motsawa daga inda take zaune, illa idanun data tsurawa momy'nta tana kallonta cike da tambayoyi.
ahankali Me'ad ta zagayo inda  take zaune tana kallonta "bby let's go now tana me kamo tafin hannunta ta fito daita daga cikin motar, sa'an nan ta meida murfin motar ta  rufe, tasoma tafiya rike da hannun ta.
yayinda ma'aikatan gidan suka shiga gaisheta cike da girmamawa, hannunta kawai ta iya d'aga musu tacigaba da tafiyarta batare da juyowa ba,
Momy tana zaune a parlour'n tana waya Me'ad tasanyo kai cikin parlour'n a matukar birkice bakinta d'auke da sallama, momy  na ganinta tayi saurin katse kiran saboda yanayin data ganta ,wujiga wujiga tamkar wace  tayi shekara tana jinya.
"me'ad lafiya kuwa naganki haka kmr wacce ta tashi a jinya?
"ko kuma kunyi Abind kuka saba ne da mijinki kika kwaso jiki zuwa gida?

momy tajirowa me'ad  wannan tambyar Tana dubanta a matukar tsorace me'ad tasamu guri ta zauna a gefen kujerar da momy ke zaune batare da tace mata komai ba, illa wani tashin hankali data tsinci kanta ciki.
 NASREEN ta isa gurin momy tashige jikinta tana gaisheta ,momy ta rungumeta ajikinta tsam kana tace "ykk nasreen?
 "yana ji jikin naki da zafi ko bakida lfy ne?
 Naunayen ajiyar zuciya me'ad ta sauke kana tace "fitowarmu kenan daga hospital yau kwananmu uku NASREEN babu lafiya Tak'arasa mgnr muryarta na rawa kmr zatayi kuka.
momy tayi Shiru tana kare mata kallo had'e da nazarin yarinyarta, a kallon da take mata ta fuskaci tana cikin matsananci damuwa da tashin hankali, yayinda ita kuma me'ad din tashiga share hawaye wasu na gangaro mata...

"To meye kuma abun kuka ?
" ko ciwon ne yayi tsanani?
 Me'ad ta girgiza mata kanta wasu sabbin hawaye na sake gangarowa bisa kuncinta.
 "  meke damunki me'ad dan banji dadin ganin yanayinki ba ? " sannan meye damuwarki  ahalin yanzu da kike zubda hawaye ko duk akan matsalar ciwon  NASREEN ne?
ta sake girgiza kai kawai tana share hawaye, momy ta fuskanceta sosai hankalinta a matukar tashe "ke me'ad ki bud'e idanunki ,ki saka cikin nawa ni mahaifiyarki ce da duk  duniya  baki da kmr ni  kuma nice nazama dole nasan damuwarki da abinda ya kawoki gida adaidai wannan lokacin daya kamata ace kina gurin aiki ne ko gidan aurenki "ki sanar dani damuwarki da abinda ke damunki domin  Nasan mataki  d'auka..

me'ad ta kalli momy fuskarta cike da tsantsar damuwa da tashin  hankali still hawaye na tsiyaya daga cikin idanunta tace "momy  ina cikin babbar matsala ,ina cikin damuwa da tashin hankali, momy na cuci kaina da kaina na yaudari kaina,na zalinci kaina, na jawo kaina maseefar datafi karfina.... Momy nayi aure batare da farincikinku ba ,most especial dady, banyi muku biyayya akan aurena da fu'ad ba , gashi ayau an wayo gari komai na neman  ta'bar'bare min, narasa gane komai nawa ,rayuwa na neman juya min baya ,
"ahalin yanzu na dawo gida ne saboda bana jin zan iya cigaba da rayuwar aure da fu'ad .......
 jin wannan maganar yasa jikin momy yayi sanyi ta gyara zamanta tana duban me'ad cike da matsanancin  tashin hankali, sannan tace "amman  meye dalilinki na fad'ar duk  wad'an nan maganganun  hk  ?
"abinda akayi shi tsawon shekarun goma sha meye na dawo shi ahalin yanzu?
"sannan meye dalilinki na cewar bazaki sake rayuwar aure da fu'ad ba wani mummunar abun yayi miki ? Momy ta tambayeta jikinta na wani irin rawa haka zalika gabanta na fad'uwa ..

me'ad ta kalli momy ganin damuwa kwance akan fuskarta ,yasa wani irin tausayin mahaifiyarta ya saukar  mata, ta sauke naunauyen ajiyar zuciya sannan ta kwashe duk abinda ya faru  ta gayawa momy.

momy tayi wata irin zabura daga zaunen datake rungume da nasreen ta mike tsaye kana ta zaunar da nasreen  jikinta na d'aukar kyarma , dan maganar ta bugi zuciyarta matukar ,

ahankali tasoma kai kawo acikin parlour'n, lokaci guda kuma ta koma ta zauna ta kalli me'ad tace" yanzu ina najma take sannan a wani hali Sajid take ciki?
"momy nagaya miki na barsu agidan ,dan tunda abun nan ya faru ban sake taka kafata cikin gidan ba ,kinga sai suji dadin yin aurensu da tushe .
"shikena me'ad to yanzu meye abun yi?
me'ad tayi murmushi me tattare da takaici abinda sajida tayi mata ,sannan tace "momy kada ki damu ni nasan yadda zanyi da Sajida ,wallahi Momy sai tayi datasani tunanin auren fu'ad arayu....

"datasani uwar me zatayi tunda ke bakiyi dakinsani ba a aurensa da kikayi ? Wannan Sautin muryar ta katse mata hanzari ,ko ba'a gaya mata ba tasan sautin muryar mahaifinta ne yashigo parlour'n ,atare suka jiyo daga ita har momy suna mamaki jin Furucinsa.
Ahankali ya tako har zuwa inda suke yana tafi da hannunwansa Duka cike da tsansar jin dadin ganinta cikin damuwa da tashin hankali"ku daina mamakin jin abinda na fad'a "arayuwa kowa abinda yake so yake da burin mallaka, "kmr yadda kikayi tsayin daka kikace duk duniya babu wanda yayi miki sai d'an talaka dagin matsiyata, itama hkn ce zata kasance daita Dan hk banga abun tada jijiyoyin wuya ba .....

"Me'ad.... !!! dady Ya kira sunanta har sau uku in a serious thought wanda yasa kirjinta bugawa da sauri batare da tasan da hakan ba, "na'am dady ta amsa masa wasu hawayen na ciccikowa a idanunta sannan tasanya kwayar idanunta cikin nasa zuciyarta na sake lugud'en bugu da karfi saboda fargaban jin abinda zai sake fad'a.
" yanzu dai me kika zo yi gidana ?
"hope ba kashe aurenki kikayi ba akan mijinki zai aure aminyarki da yar aikinki?

"idan kashe aurenki kikayi ko yaji maza maza ki tashi ki bar min gidana, dan babu masaukinki acikinsa.
" idan kina tunanin zaki kashe aurenki ne ki dawo gidana ki zauna kiyi saurin canza tunani ,dan idan kin kashe aurenki har abada bazaki zauna tare dani ba. "idan kin manta sharrud'ana akanki bari in tuna miki .
" yaji ,mutuwar aure alkahari kowani iri ne damuwar rayuwa ,yasameki bazaki tunkaro hanyar gidana ba," kikace kinji kin gani kin yarda kin amince , kika zabi auren d'an matsayata akan mu iyayenki da mukayi silar zuwanki duniya.
"daman kuma wannan ranar nake zaman jira zuwanta wanda nasan komai daren dadewa zata zo gashi tazo kuma na godewa Allah datazo ina raye cikin koshin ..
" dan haka tun wuri ina shawartarki ki tashi ki koma gidanki, idan ba sakinki yayi ba, idan kuma ya sakeki ne sai kin nemi gurin zama amman ba'a gidana ba.

"haba dady wace irin mgn ce haka ? "da me kake son taji?
"Ina ruwana da abinda zataji, nace ina ruwana lokacin danake rokonta ta auri safwan me tayi min?"in ce komai ya faru ne akan idanunki ?
"kamata yayi ka duba lamarin da rabon dake tsakaninsu , idan basu auri junansu ba ,ta yaya kake tunanin za'a samun rabon NASREEN ?

"NASREEN din banza ina ruwana da wata nasreen?
"kuma wallahi bari kiji ingaya miki ni nan me d'aurawa mijinki aure ne da sajida matsawa tana son shi da gaske shima kuma yana sonta , ke koni sajida tace tana so zan aurenta balle wani mijinki din banza da wofi ,oya zo ki bar min gidana kije ki rungumi matsalarki ,ki bar rayuwarmu, dan tuni na manta da na haifeki arayuwata ,a halin yanzu diya daya gareni itace suhailat yar albarka yarinyar kirki kuma InshaAllahu zatayi albarka saboda tana min abinda nake .....
cikin kidima da tashin hankali me'ad ta durkushewa agaban mahaifinta tana wani irin kuka "dan girman allah dady kayi hakuri ka yafemin , na yarda nayi kuskure arayuwata,Amman na tuba dady karka min haka ,karka juya min baya, banida wad'anda suka fiku ,ka yafemin nasan hakinka ne ke bibiyata ya fixge karfarsa daga rikon datayi masa.

"baki ga komai ba tukun me'ad sai ranar da kikaji na d'aura auren sajida da mijinki ,kijira abinda zai biyo baya sai fu'ad ya zame miki annoba arayuwarki sai ya tarwatsa rayuwarki da farincikinki ,ke hatta wannan aikin da ni nasan wahalar dana sha kafin ki sameshi da har kike tinkaho da dashi, wallahil azim matsawr ina da haki akanki shima sai yabar hannunki kmr yadda Fu'ad ke shirin barin hannunki ......
"ki tashi ki bar min gidana ya k'arasa mgnr cike da hargagin 'bacin rai ...
Kuka me'ad take sosai tana Jan gwiwowinta tana bashi hakuri ,momy ma ta durkusa agabansa tashiga bashi hkr. "kayi hakuri Dan girman Allah kabarta ta zauna tare damu ,yanzu ina kake tunani zata ga yarinyar mara lfy atare daita ?
"khadaji ....dady yakira sunanta a zafafe "na'am dady. Ta amsa masa jikinta na rawa.
"a iya tsawon arayuwamu, mun ta'ba samun wata matsala dake ?
momy tayi saurin girgiza kanta tana jujuya hannuwanta alamun dai yayi hakuri .
"to karki bari musamu matsala akan wannan yar isakar yarinyar mara jin magana .
"gidan nan ma tukun naki ne ko nawa ?
Momy tayi saurin girgiza masa kai tare da cewar "naka ne.
"to nagodewa Allah daya kasance nawa ne ba naki ba, kuma lokacin dana tashi gidansa baki sanya sisin kwabonki ciki ba ,Dan haka bana bukatar ganin me'ad cikinsa taje can gurin wad'anda take tunani sun fini daraja agurinta, sannan ya fuskanci me'ad sosai yana huci "minti biyu kacal nabaki ,ki d'auki yarinyarki kibar min gidana bana bukatarku cikinsa, hakuri tashiga bashi amman sam yace bai san da zance wani hakuri ba sai ta bar masa gidansa .

Ta mike ta tashi tsaye jikinta na rawa ta janyo hannun NASREEN ta rike cikin nata gam kmr wace za'a kwacewa ita, tasoma tafiya tana kuka ,momy na kuka , hatta NASREEN kuka take sosai tana tausayawa momy'nta "yanzu saboda ta auri dady'nta yasa babanta yayi mata wannan wulakanci, daman grandpa dinta bayason auren iyayenta ?
Hakuri take son bashi Amman tashin hankali datake hangowa tattare da momy'nta da ita kanta yasanya ta kasa magana sai kukan datake har da shesheka.

Jikin momy na 'bari tabiyo bayan me'ad tana kuka tana kiran sunanta....shi kuwa dady ko ajikinsa, Sam bai ji wani abuba dangane da halin da ta tsinci kanta ba.
me'ad ta tsaya tare da cewa " momy ki daina kuka ki koma kawai duk abinda ya faru dani ,ni na

jawowa kaina  na zabi d'a namiji akan mahaifina ,na fifita soyayyar fu'ad akan ta mahaifina, yau wa gari ya waya?
""yanzu ina zaki?
"duk inda Allah yayi momy zan tafi na bar rayuwar kowa, zanje nayi sabuwar rayuwa tare da diyata, zan rungumi kaddarata....
"amman ki rokon min dady yayi hakuri ya  yafe min abinda nayi masa wallahi nayi danasani arayuwata, ki min addua momy ko zan daina jin rad'ad'in da zuciyata ke min ... ta juya tacigaba da tafiya har ta isa jikin motarta tashiga ta tayar , ta fito daga cikin gidansu tana wani irin kuka.

Gudu kawai take shararawa akan titi, duk hanyar data gani ,bi take  saboda bata San inda zata ba ,banda bugawa bubu abinda zuciyarta keyi, kuka take sosai tana dukan sitiyari motar "me yasa nayiwa mahaifina abinda nayi masa akan soyayyar fu'ad ta furta a fili?
" me yasa ban bi zabinsa ba nace lallai sai fu'ad zan aura gashi komai na neman birkice min ? Ta sake fashewa da wani sabon kukan ,hakika na cuci kaina, iyaye duk lallacewarsu sun wuce wulakanci ,ballanatana irin nawa iyayen da samun irinsu ke da wuya, dady uba ne har da rabi ,wanda ke  maye gurbin uwa idan tana raye ko amace .
"sun haifi ne sun min gata ,mahaifina ya inganta rayuwata sosai   yabani abinda duk wani d'an Adam zaiyi tinkaho dashi arayuwar duniya ,bai rageni da komai ba a tun tasowata ,komai nace shi za'ayi .
",me yasa nayi masa abinda nayi masa?
" me yasa banyi masa biyayya ba alokacin dayace na auri safwan? " why why why !!! Me'ad meyasa nayi abinda nayi ?
"Wayyohlly Allah na cutar da kaina, Kuka take sosai Sam ta manta da nasreen dake   zaune agefenta sai  da taji yarinyar ta riko hannunta a matukar afirgice tare da sakin razananniyar k'ara sannan taja birki da karfi ta tsaya cak tana Jan ajiye zuciya, hawaye sha'be sha'be kwance Akan fuskarta, itama nasreen din  kukan take sosai  har lokacin da shesheka ,tana jin tausayin dady'ntan sosai fiyye da mahaifiyarta , Amman ayau tausayin momy'nta ne ya rinjayi  nashi har batasan a mizanin dazata ajiye hkn  ba, rungumeta me'ad tayi  ajikinta tana kuka "am sorry bby gudun danake ya tsorotaki ko.. ?
Nasreen ta d'aga mata kanta al'amun Eh tana kuka.
"am sorry na daina bazan sake ba kinji bbynah, ta d'aura idanunta akan agogon fatan dake d'aure da tsinyayar hannunta , lokacin shan maganin nasreen din yayi ,Dan HK ta kai hannuta sit din baya ta d'auko ledar maganinta da ruwa ta balla ta bata ta sha sannan ta mai daita ta kwanta akan kujera, itama ta meida bayanta akan kujerar datake zaune akai, byn tayi baya kad'an daita, ta runtse idanunta still hawayen idanunta  suki  tsayuwa  har lokacin nadama ce fal cike da zuciyarta.

Kusan minti talatin tana  gurin  tana zance zuci wayarta ta d'auki k'ara sauti me dadi da ta'ba zuciyar Wanda ya saurara,ko bata duba wayar ba, tasan ko waye me kiranta, sakamakon sautin dataji "fu'ad dinta ne ,dan shi kad'ai tasanya wannan sautin saboda matsayinsa gareta ," mutumin data sadaukar da rayuwarta da komai nata akansa, mutumin da shine silar 'batawarta da mahaifinta,a yau tayi datasanin a had'uwarta dashi a wancen lokacin" duk duniya tasani kowa yasani babu halittar da mahaifinta ke so sama daita Amman   an wayi gari sanadin

had'uwarta da fu'ad komai ya canza, soyayyarta ta juye zuwa kiyayyar da batasan ranar gushewarta ba..
Wani kukan ne ya kufce mata tasanya duk hannuwanta ta toshe bakinta ,"tarasa fu'ad rashi na har abada, sannan tarasa soyayyar mahaifinta, ga aikinta datake ganin shine gatanta da rufin asirinta shima tana nema rasashi adalilin takasa samun natsuwar zuciyar gabatarwa.
akalla bazata tuna karshen shigarta office dinta da sunan yin aiki ba, gashi tun rashin Ifyr nasreen bata taka kafafunta zuwa cikin ma'aikatar ba, ko kiran chairman bata samu damar yi ba ,batasan me zai biyo bayan faruwar hkn ba ,tun yanzu tacire rai da tsammanin da aikinta bisa kaidodinsu ,na ko fashin rana daya mutun yayi zai fuskanci babbar matsala da chairman.
"zuwa yanzu tasan komai ya rigada ya tsaya mata ,shikenan rayuwarta zata zamo abar tausayi mara amfanin ..
Fu'ad yakira wayarta sau babu adadi ,Amman batayi yunkurin d'auka ba sai hawayen datake zubarwa .
jiki a sanyaye nasreen takamo hannunta"momy !!! dady na kira ,should I pick the call?
"No......tace mata atakaice tana me runtse idanunta"why momy ki d'auka mana.......," koni na d'auka plz...?
"Pick....ta fad'a saboda batason k'arin damuwa akan wacce take ciki .

Nasreen ta d'auki wayar tare da cewa "hello dady nah.
" hello my bby How are u doing ?
"Am fine dady .
"Ina momy'nki take ?
"gata a kusa dani tana kuka,Jimmmmm yayi da ransa sannan yace "okay bata wayar.....
nasreen ta miko mata wayar "momy dady yace nabaki..
Me'ad taki kallon inda take ballanatana ta amsa wayar hannunta ,"momy plz now ki amsa wayar dady'na.
Sam me'ad taki, " ta amsa tace masa me byn cutar da yayi mata ?
"Me zatacewa mayaudarin irinsa?
"Mayaudari maci amanar kauna ......"Har abada wata kalma bazata sake shiga tsananinsu ba, kowa yaje yayi rayuwarsa ....
yana jin yadda nasreen ke mata nacin ta amsa wayar Amman taki , tswon minti biyar wayar na tafiya sannan nasreen ta meida wayar zuwa kunnenta tana sauke numfashi "dady........
"taki amsa ko ya fad'i hkn Dan yasan abinda zata ce masa kenan ?
"Don't worry bby, yanzu kuna ina, na dawo hospital doctor yace yayi discharging naki ,na dawo gida bangan bbynah ba,gashi nayi missing dinki ,I want to see ur beautiful face, tayi murmushin jin dadi sannan tace "ai daga hospital gidan grandpa muka wuce nan tashiga koro masa duk abinda ya faru akan idanunta ,fu'ad ya samu guri ya zauna yana mai runtse idanunsa yana jin wani irin zallar 'bacin rai da tunda yazo duniya bai ta'ba jin irinsa ba, wani irin tafarfasa zuciyarsa ke masa "why me'ad ? Ya furta a raunane.
"Me yasa zata masa hk.? Ahankali ya hau sauke numfashi cike da takaicin dabbancin abinda me'ad tayi masa, ya d'auka iya shekarun da sukayi tare shi daita sun zama abu daya, sannan sun wuce wannan nevel din ,tazama shi shima yazama ita, sun chakud'e guri daya ta yadda duk runtsi duk wuya babu wanda zai ji kansu balle mahaifinta, daya fito ya nunawa duniya bayason

zamansu tare, Sautin muryar nasreen dayaji cikin dodon kunnenshi ne  yasa yayi saurin bud'e idanunsa "dady da gaske ne zaka auri aunty sajida da najma me aiki  Dan kayiwa momy'na kishiya dasu?
Yayi shiru kawai ya kasa bata amsar tambayarta, sai ma d'aura hannunsa da yayi ya dafe goshinsa dashi yana shashshafawa ahankali  ahankali ,while kirjinsa na  bugawa da sauri sauri.

"daddy matukar da gaske zaka auresu ne ,plz change your mind, dan banason kayiwa mamana kishiya saboda banaso ganita cikin damuwa, saboda nima zan shiga cikin damuwa yanzu haka kirjina ciwo yake min dady tak'arasa mgnr kmr zatayi masa kuka .....
Muryarsa  a matukar kasalance yace "bby kina bukatar kulawa  wanda momynki ta kasa tsayawa ta baki, ni kuma amatsayin na mahaifi ba hurimina bane ,wannan hanyar kad'ai ce zatayi min maganin matsalata saboda nasan idan na auresu zasu kula dake shine dalilin....
 " Amman ki za'bawa dady'ki mutun daya acikin auntynki sajida ko najma wanda kike son na aura ta zauna tare dake amatsayin second momy dinki, wace zata cigaba da kulawa dake da dady'nki..
 "ni banason dukkansu ,ni banason kowa ni nafi son mummy'na kawai ..........
ya sake runtse idanunsa gam" yanzu kuna ina?
 " zanzo na sameku na dawo daku gida, ta d'aga kanta tana duban yanayin gurin ta cikin mota, idanunta ya sauka akan wani green sambod da aka rubuta *main land bridge*  Dan hk ta sanar masa a matukar firgice ya bud'e idanunsa ,gabadaya ya gigice ya kid'eme muryarsa na rawa yace "main land  bridge?
"Yes dady shine abinda nagani ,yace  "ki sa wayar a handafree.
Aiko take nasreen tayi abinda dadynta ya umarceta cikin d'aga  murya yace"me'ad kina hauka ne, dazaki kai min yarinya har main land bridge?
"Wai meyasa kike son meida kanki wawiya ne akan yar kankanuwar matsala?
 Tayi masa banza taki cewa dashi komai ,shi km  ya dinga zuba mata bakaken maganganun ta inda yake fita bata nan yake fita ba still tana jinsa taki cewa komai, Dan idan tace zatayi mgn zagi ne zai fito daga cikin bakinta da hk tacigaba da sauraransa kawai take tana jin zallar 'bacin rai na ratsata, hawaye na bin kuncinta ji take a duniya yagama tozartata, ya gama wulakanta da abinda yake son mata,ganin taki kulasa yasa  ya sausauta muryarsa,
"Kiyi kokarin dawo min da yarinyata so that ke ki cigaba da zama agurin tunda abinda kika za'barwa kanki kenan .
yana gama fad'ar hk ya katse kiran,Wanda  alokacin ita kuma tayiwa motarta key dan tasan Sarai zai iya zuwa ya samesu agurin tunda yaji inda suke.

 me gadin gidansu takira taji ko fu'ad din na gida , ya tabbatar mata da yanzu ya fita, hasashenta ya tabbata kenan, zuwa zai yi ya amshi nasreen din ya barta da tarin bakinciki da damuwa, kai tsaye gidansu ta nufa, bata tsaya bata lokaci ba tashiga ta dibi abubuwanta datasan masu amfani ne gareta, dana yarinyarta ta kulle kofarta ta fito tashiga mota tabar gidan.

 Yayinda fu'ad Yayi maya tafi sau hud'u akan main land bridge, ya hau ya sauko Amman bai ga alamun tsayuwar motarta ba ko alamun wata motar daban ba ,gashi yana kiran wayarta taki

d'auka haka ya hakura ya koma gida yana jin zallar bacin rai yana shiga gidan jikinsa yabashi tazo gidan . Da sauri ya fito ya isa gurin me gadi yana kwalla masa kira ,me gadi ya k'araso ya tsaya agabansa "maman nasreen tazo ne byn fitata?
"Eh yalla'bai tazo bata ma dade sa fita ba wani irin takaici yaji kmr ya d'aukeshi da mari, a fusace ya juya ya komai cikin gida yana huci gabadaya ya rasa meke masa dadi ,hankalinsa ya sake tashi so yake yasoma neman inda najma take Amman bashi da natsuwar zuciya a kalla ya kusan minti goma tsaye yana tunanin mafuta ya duba agogo karfe karfe biyar ta kusan ciki" ina bai ga ta zama dole duk yadda zaayi sai yaga me'ad da nasreen tare da dawo dasu gida sake bazama yayi ya fito harbar gidan kallo daya zaka masa kasan baya cikin natsuwarsa yashiga motarsa aguje ya bar gidan.

*********

A bangaren mahaifiyar me'ad kuwa kuka take a tun fitar me'ad gidan ,taso kiran fu'ad Amman ta kasa saboda a yadda zuciyarta ke cike da 'bacin rai zata iya gaggaya masa komai yazo bakinta ,abinda bazata so faruwarsa ba kenan atsakaninta da surinkinta ,me mutuntata da ganin kimarta, ita batace kar ya kare aure ba ,"amman meyasa sai sajida da najma?
Tasan zai auresu ne Dan kawai ya kuntatawa zuciyar mead dinta...
gidan yayi shiru kmr anyi mutuwa Dan koda suhailat ta dawo daga makaranta taji labarin abinda ya faru mutuwar tsaye tayi agurin, itama hankalinta yayi mugu mugun tashi..
ta dinga mamakin cin amana irin na sajida a ganinta har gara auren najma akanta.....

Bangaren me'ad kuwa yawo ta dingayi acikin gari, daga wannan titi zuwa wancan titi,tarasa inda zata taji sanyi aranta ,tayi tunanin zuwa dangin momy'nta Amman sai taga kmr zata tonawa kanta asiri ne, a yanzu ta d'auki darasi me girma a zamanta da sajida, bazata sake yarda da kowa ba arayuwarta ,zata koyi rike sirrikanta ,zata bawar cikinta damuwarta bazata sake sharing secret dinta da kowa ba bayan mahaifiyarta, itama Dan tasan bazata gayawa duniya bane ko ha'intarta sai dai ta d'aurata bisa turba .daga karshe zuciyarta ta bata shawarar takama hotel kawai ta cigaba da rayuwarta har zuwa sanda mahaifinta zai sauko ya amsheta ,bazatayi fushi dashi ba ,haka zalika bazata gaji da rokonsa ya yafe mata ba, har sanda zai furta ya yafe mata.

Dan hk Kai tsaye wani had'ad'en hotel ta nufa me suna city hotel, cikin Dan kankanin lokaci ta isa kawataccen hotel din Wanda hotel ne ,na isasu ta d'aki ,daya daga cikin mai'aikatan hotel din yayi gaba rike da key'n d'akin ita kuma tabiyosa abayan rike da hannun nasreen ,byn ya bud'e mata d'akin ta mika masa key'n motarta domin shigo mata da kayanta, ya amsa juya cikin sauri, suka shiga ta meida murfin kofar ta rufe .
Komai na agyare neat a acikin Had'add'en d'aki .
Ko cikakken minti biyar baayi ba maaikacin yashigo da akwati kayansu ya ajiye ya sake fita, ita kuma takarasa tayiwa kofar key tare da barin makuli ajikin kofar ta dawo ta tsaya atsakitar d'akin tana k'arewa falle d'akin daya kallo wanda ya k'awatu sosai , doguwar kujera kwaya daya ajiye , da TV bango sai air condition ,babban wardrobe na zuba kayan sawa daga gefe, mirrow da bedside, daga can bangaren toilet ne me murfin glass .
d'aki ne mai matukar kyau da fad'i ,ta d'auki lokaci tsaye tana k'arewa d'akin kallo sannan ta

K'arasa  ta kunna ac tare da rage karfinsa saboda nasreen ,
Jikinta  a matukar sanyaye ta janyo hannun nasreen jikinta ta rungume yarinyar naji dumin jikinta muryarta a sanyaye tace "muje bbynah kiyi wanka  nasan kin gaji dayawa ko?
 Murmushi nasreen ta sakar mata sannan ta sake shigewa jikinta, "momy meyasa kika kawomu nan ?
"Mu koma gida nasan dady zai shiga damuwar rashinmu, plz momy mu koma ...
"Shiiiiiii kiyi shiru da zance komawar nan har abada nasreen bazan komawa mahaifinki ba ,idan kuma kinfi sonshi da son zama tare dashi  akaina fine I can take you to him right now. "Ki kwantar  hankalinki zamuyi rayuwa kmr muna gida kinji bby, zan siya miki duk abinda kike ,zamu dinga kallon TV tare muna enjoy ki manta da wani dady okay"taja hannunta suka shiga bayin tayi mata wanka da ruwan zafi ,tana tsaye akanta tayi alwala suka sake fitowa tare daita daure da towel.
tsab mead ta gyarata ta sauya mata wasu kayan masu kauri, ta Mike mata  hijabi, "kiyi sallah kafin na fito, sannan ta juya ta sake komawa cikin  bayi.

Mmn sudais ce
[11/3, 8:29 AM] El~hajj: 💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
FAIZA HAMMADU BARAU
(YAR NUMAN)

Page 78

........tsaye tayi acikin bathtub din ,ruwa na  tsiyaya akanta zuwa sansar jikinta,Wanda ke saukar mata da natsuwa kad'an saboda    har wannan lokacin bakinciki abinda sajida da fu'ad ke shirin yi mata, yaki barin zuciyarta da gangar jikinta, "ta yaya zata iya sharing din fu'ad dinta da wata macen ,macen ma aminiyarta da suka taso tare... ?
"Suke yin komai nasu  tare sannan babu abinda bata sani ba na sirrukan rayuwarta....
"A gurinta Fu'ad ba kmr sauran maza bane ,daban yake acikin mazan datake kallo , sannan natsatse ne kamili Wanda yasan ciwon kansa ,tana son shi fiyye da rayuwarta sai dai bata jin zata iya ganinsa yana rayuwa  tare da wasu matan byn ita,tafin son duk runtsi duk wuya su kasance tare suka k'arasa rayuwarsu .
Ahankali take tuna moment dinsu dashi ,duk da ba wani  bashi had'in kai  takeyi ba  ,amman hkn baya hanata jin dadin abinda yake mata. "Anya kuwa zata iya rabuwa dashi kmr yadda ta

fad'a tayi rayuwarta ita kad'ai sai yarinyarta?
"Anya kuwa ba wata cutar Kan zata sake yiwa rayuwarta ba ?
Tayiwa kanta tambayar tana jin jikinta yana sauyawa, ahankali take jin feelings dinsa na bijiro mata duk da bata tsamaci zata ji hkn ba akansa, a wannan tsayuwar datake komai na rayuwarsu ke dawo mata daki daki cikin kwakwaluwarta ,yanzu ace agida ne kuma suna zaune lafiya dashi zai shigo bayin ,ya tsura mata kyawawan idanunsa masu maseefar burgeta da tsaya mata arai ,yana kare mata kallo ko kifta idanunsa baya son yi daga karshe kuma ya k'araso gareta ya riko kugunta yana me had'eta da jikinsa tare da shafa kirjinta yana goga mata gashin dake zagaye da fuskarsa zata lafe akirjinsa , koda kuwa bai yi niyyar yin wanka ba ko kwanciyar aure daita ba ,ganinta tsaye babu kaya zai janyoshi yayi koda kuwa acikin bayi ne yayinda ita kuma zata shiga tutturesa tana kukan shagwaba ita tagaji bazata iya da jarabarsa Amman ba zai ta'ba kyaleta ba har sai yacima burinsa akanta duk yadda tayi ta yakice tunaninsa abun yaci tura haka tayi ta tunaninsa ..

ganin tunaninsa daya d'arsu a zuciyarta yaki barin tayi abinda yashigo daita ,yasa ta sauke naunayen ajiye zuciya sannan tasoma sa'bawa jikinta sabulu ,sai dai duk inda ta gogo sabulu ajikinta sai taji kmr tafin hannunsa ne ke yawo ajikinta Dan haka tayi
Shap shap tayi wanka ta d'auro alwala ta fito ,koina a d'akin ya kama kamshi room freshener da'akayi amfani dashi .
jakar kayanta ta bud'e ta ciro doguwar riga ta sanyawa jikinta ta k'arasa inda pray mate yake ta tada sallah byn ta idar da sallah s ta janyo akwatin kayansu ta fiddosu daya bayan daya tasoma jerawa cikin wardrobe nasreen na tayata miko mata, wasu suna hirarsu cikin farinciki duk da ita ba wai nufinta tayi hkn ba ,Amman ya zame mata dole ko dan kwanciyar hankalin diyarta da lafiyarta ,batayi sha'awar kunna makeken TV dake makale da bangon d'akin ba ,Amman saboda ta d'bewa nasreen kewa yasa ta tashi taje ta kuna ta dawo tacigaba da aikin jera kayan.

byn tagama jira kayansu ta tmbyi nasreen ko zata ci abinci Dan ita bata jin cin komai ,yarinyar tace " ba yanzu ba sai zuwa anjima momy , Dan kafin me'ad ta yanke shawarar zuwansu hotel ta sai mata snacks taci a mota .

Kwanciya tayi akan gadon tabar nasreen na kallo ,ahankali ta runtse idanunta domin ta samu hutu da natsuwar zuciya, Kafin lokacin sallar magri tayi ,tunanin mijinta ne ya sake sanyo kai cikin zuciyarta dama gangar jikinta, wani irin sabon yanayi ta tsinci gangar jikinta ciki yayinda wani feelings dinsa yashiga bijiro mata idanunta har sun sauya, da kyar tasamu ta yakice shi ta Mike ta janyo system dinta data jona a caji ta kunna tasoma dudduba sakonin da aka turo mata ,cikin haka kiran chairman din company din datake aiki yashigo wayarta, take gabanta yashiga dukan uku uku ,da kmr karta d'auka Dan bata son K'arin tashin hankali akan Wanda take ciki ,ammam ta sanshi tasan halinsa shima ba kwanwar lasa bane ,Akan company dinsa babu abinda bazai iya yi ba ,Dan HK tayi saurin sanyawa jikinta kuzari ta d'auka ta manna wayar a kunnaneta tana gaisheshi a natse ya amsa tare da cewa "muna bukatar ganinki gobe by 10 :am atakaice tare da katse kiran ,jikinta yayi sanyi kmr wace akayiwa wanka da ruwan sanyi ,gbdy takasa cigaba da operating system din dake gabanta, ta ture system din gefe ta

janyo nasreen ta rungume ajikinta hawaye na gangarowa daga cikin kwarnin idanunta ,"jikinta na bata aikinta ya kusan zuwa karshe.....har aka kira sallah magariba tana makale da nasreen tana jin karfin gwiwa a duk sanda ta rungumeta yayinda take cikin damuwa,ahankali ta zameta daga jikinta ta kwantar a saman cinyarta ta tsura mata ido kawai tana kallonta wani irin kaunar yarinyar nabin jikinta bacci take har lokacin tana sauke numfashi ahankali, ta Mike ta tashi taje tayi alwala bayan ta idar da sallah bata tashi ba tacigaba da zama tana lazami tarenda kaiwa Allah kukanta.

*********

Misalin karfe tara na dare mumy ta samu dady ad'akinsa cikin yanayi na rarrashi take ce masa "dady sam abinda kayi bai kamata ba ,yakamata kabi komai ahankali hannunka baya ru'bewa kace zaka yanke ka yar duk abinda me'ad tayi maka duk lalacewarta bazaka ta'ba canzata amatsayin diyarka ba ,kalaman daka furta mata a yau din nan yayi muni dayawa.....

dady yasoma magana cikin 'bacin rai "ina amfaninta arayuwata?

"Meye amfanin D'an da bai jin maganar iyayensa da yi musu biyayya?

"Ni tsine mata ma naso yi tabi uwa duniya kowa ya huta ,dady yana fad'ar hk numfashinsa ya fara sama sama sai faman haki yake ,mummy tana ganin hk ta fara salati game da waige waigen Kafin kace me tuni dady ya fara fita haiyacinsa ,mummy tayi matukar rud'ewa sakamakon numfashinsa daya tsaya a matukar gigice ta kwallawa suhailat kira itama tashigo d'akin a rud'e tayo gurin momy dake jijigasa , tare da taimakon sulahait suka dawo da dady parlour'n, ruwa sanyi mummy ta dinga shafa masa sannan ya dawo haiyacinsa ya jike sharkaf da ruwa kwance ya ganshi ajikin momy wacce idanuwanta tuni sun dade da yin luhu luhu saboda kuka, dady ya d'ago idanunsa ya kalli momy da take faman tofa masa adduoi, da kyar dady ya iya bud'e bakinsa "wai ,abinda nake tunanin ne ya faru..?

Mummy tace " a'a babu abinda ya faru ina dai tunanin BP dinka ne ya tashi bara nai ma doctor waya yazo ya duba ka.

Jikin momy na rawa ta tashi daga gun datake zaune tana rungume da dady tmkr wani karamin yaro ,bedroom dinta ta nufa ta d'auko wayarta dake ajiye akan gado ta fara lalubo lambar cikin kankanin lokacin takira doctor ya d'auka ,ta fad'a masa duk halin da'ake cikin doctor yace "gashin nan zuwa .

Doctor Peter ya faka motarsa ya fito da sauri ya nufi hanyar da zata sadashi da parlour'n dady ,Amman a wannan lokacin momy tai masa jagora zuwa bedroom din ,doctor ya fito da kayan aiki yasoma dubashi ,byn ya gama ya kalli mummy yace " "madam ya'akayi hkn ta faru jininsa ya hau dayawa sosai ?

"yakamata ku kiyayye 'bacin ransa domin ya samu cikakkiyar lafiya mai dorewa mumy tace "doctor yanayin rayuwa ne kawai Amman za a kiyaye InshaAllahu. Doctor

Ya bar magunguna da dady zai yi amfani dasu ,allurar bacci akayi masa domin ya samu ishashen bacci sannan yakama gabansa .

Ta bangaren fu'ad shima yana cikin tashin hankali mara misaltuwa, duk inda yasan zai ganta yaje har dama inda bayi tunani ba, hankalinsa yayi maseefar tashi yarasa inda zai sa ransa yaji

dadi shi kam a yadda yake ji acikin ransa bazai iya hakura da neman me'ad ba ,kodan tilon diyarsa mara lafiya har hawaye ya zubar aranar ya samu guri gefen titi yayi parking din motarsa ya d'aura kansa a saman sitiyari yana kukan tausayin halin da nasreen dinsa Zata shiga a sanadin wannan tashin hankali, yasan me'ad bawani kulawa zata bata yana jin tsoron ya rasata, ya dade agurin sannan ya tada motarsa yayi hanyar gida ,koda isa gidan kasa zama yayi sai faman zariya yake acikin parlour'n sakamakon sautin bugun zuciyarsa daya addabi kunnensa "wayyohlly Allah nah ya furta yana me rike kugunsa da hannu daya .....

Daren ranar kuwa kwana me'ad tayi nafila Sam takasa runtsawa , saboda tashin hankali datake ciki yafi karfin tunaninta , tunanin mahaifinta yafi komai addabar zuciyarta, tayi shiru agurin tana lazimi tana jin kmr takirasa ta sake bashi hakuri ,daga inda take zaune ta mika hannunta ta d'auki wayarta tasoma neman layinsa ,takira wayarsa yafi sau biyar ba'a d'auka ba kawai ta rushe da kuka tana cigaba da addu'a, sai kusan ukun dare bacci 'barowa yayi awon gaba daita.

Washegari da wuri ta tashi ta shirya nasreen cikin uniform din school itama ta shirya kanta ,ta tasota gaba, tana gaba tana binta abaya har reception,ta bada makulin d'akin domin killaceshi sannan suka fice .

kai tsaye wani had'ad'en restaurant suka nufa tayi musu order abinci, ta turawa nasreen abinci agabanta tare da yin tagumi ta tsura mata ido "ki ci abinci ..... "Momy ke meyasa bazaki ci ba ?Tayi mgnr muryarta na rawa kmr zatayi kuka "kici kawai nasreen bazan iya ci ba .......
take idanun nasreen ya cicciko da kwalla "why momy.....ta fad'a hawaye na gangaro mata"tun jiya banga abinda kikaci ba ,idan bazaki ci ba nima bazanci ba takarasa mgnr hawaye na biyo kuncinta sharrrrrr ..
me'ad tayi saurin kai hannuta saman fuskar nasreen tana goge mata hawaye ", no my bby dont cry I will eat tasoma k'ok'arin dibar abinci ta kai bakinta "gashi ina ci kema ki ci kinji bbynah banason damuwarki ina matukar sonki duk da dadynki nagani kmr banasonki ,adalilin ban ajiye aikina ba Wanda hkn bashi zai nuna bana sonki ba ,nice nayi silar zuwanki duniya idan wuya ake ci naci idan dadi ne naci" ta yaya mutun zai d'auki ciki har na tsawon wata tara yayi na kuda ya haifi d'ansa ace masa bai sonshi .....
"ki daina d'aukar maganganun mahaifinki, abaya nasan nayi sakaci , rashin kulawa dake Wanda bashi yake nufin bana sonki ba ....ina sonki nasreen fiyye da kaina sannan a shirye nake Dana sadaukar da rayuwata akanki, akan mahaifinki nayi komai har sanda na mallakeshi matsayin miji gareni ,ina kuma ga ke dani kad'ai nasan azaba da wuyar Dana sha tun daga haihuwarki har zuwa yanzu.
Ta k'arasa mgnr tana bata abinci abaki suna ci tana kwantar mata da hankali har suka gama tayi dropping dinta a school takama hanyar zuwa office,Akan hanyarta ta zuwa aiki duk inda taga Almajiri sai ta tsaya tabashi sadaka maganin maseefa ..

Ahankali ta Sanyo hancin motarta cikin ma'aikanta tsirarrun mutanen da suka yi sammakon zuwa suka bita da kallo , inda take jikinta ya bata akwai abu dake tafiya a kasa, wata irin damuwa me tattare da tashin hankali ne sukayi mata diran makiya ,amman hk bai hanata

sanyawa zuciyar Kwarin gwiwar ba ,ta nufi gurin data saba ajiye motarta tayi parking tana fargaban fitowa ,kusan minti talatin tana zaune works nata faman shigowa ciki har dasu mudansir da ma'aruf suka fito atare suna kyalkyake dry da alamun suna cikin nishadi suka shiga cikin ma'aikatan batare da sun lura daita ba.
tana zaune tahir shima yashigo ya wuceta.
ahankali ta fito da system dinta tasoma operating domin k'arasa tura sakonin da'akayita turo mata daga daren jiya zuwa safiyar yau din nan ,bata fito ba har sai da taga shigowar chairman sannan ta fito adaidai karshen dogon korido ta had'u da mudansir yayi saurin k'arasowa inda take ya amshi jakar hannunta da system, ita kuma tacigaba da tafiya ta nufi hanyar office dinta da niyyar shiga ta gani ko zata daina jin zafin dayake mata.
Mudansir yabiyo bayanta da Dan hanzarinsa "madam yau fa akwai meeting da chairman "nasani ta bashi amsa atakaice tana kusa kanta cikin office dayake tun shigowar mudansir ya bud'e, wanda ya zamemasa kaida .
ai da wani irin sauri me'ad ta fito daga cikin office dinta kmr zata hantsila tana furta kalmar "inna lillahi wa inna ilaihi rajiun lahaula wala kuwata illa billa....
Shi kuwa mudansir kad'an yarage bai kyalkyale mata da dryr mugunta ba saboda yadda yaga tafito aguje kmr mota ....

numfashi take fitarwa ahankali tana jin zafi ajikinta, tayi saurin barin jikin kofar Dan tiririn dake ta'ba fatar jikinta, ta nufi conference room, koda ta isa ta iske chairman zaune tare da mataimakinsa Wanda yakasance ba indiye ne ,shine na biyu a company sai ita, duk sauran wad'an da ke zaune agurin akarkashin ikonta suke, ahankali ta samu guri ta zauna a natse zuciyarta na bugawa ,wannan shine karo na farko da za'a yi taro ta tsinci kanta cikin matsanancin fad'uwar gaba ,duk taron da za'a yi cike take da natsuwar zuciya da kwarin gwiwar tare da isa da mallaka da nuna ita din wata ce acikin ma'aikatar ,sai gashi yau babu wannan zarra da isa da mallaka sai tsagwaron tsoro dankare da zuciyarta.

Shiru ne yabiyo bayan zamanta , kafin daga bisani chairman yayi gyaran murya yasoma magana cikin kwararren turancinsa wanda bazaka ta'ba cewar ya had'a jinsi da hausa fulani ba"acikin yan kwanakin nan abubuwa dayawa sun faru Wanda yasa dole mu tautauna akai, Abu na farko da campay tasoma fuskanta shine karancin income din da company bai samu ,ta hanyar sakacin manager. Me'ad ta d'ago idanunta da sauri ta d'aura akansa tana kallonsa , chairman ya fuskanceta da kyau kana yacigaba da mgn "sakacin rashin tsayuwarki akan aikinki da rashin bawa aikin mahimmanci yana kokarin janyo mana babbar hasara, a halin yanzu dakatarwa ce tafi dacewa dake ,Amman saboda wannan shine karo na farko da muka ta'ba samunki da wasa da aiki, yasa zamu yi sausaci akai ,Dan hk daga wannan lokacin bama bukatar sakaci ko rashin bawa aikinki mahimmanci, Dan idan muka sake samun rashin ingancin tsayuwarki aiki zamu sallameki......
tunda chairman ya fara magana ta nemi miyo ko daya tarasa abakinta, zuciyarta ke wani irin bugawa da sauri sauri ,duk karfin ac dake aiki acikin conference room din ,hkn bai hana gumi tsatsafo Mata ba..
take furucin mahaifinta yashiga dawowa mata "aikin da kike takama dashi Wanda ni kad'ai nasan irin wahalar Dana sha akansa kafin ki sameshi shima zai bar hannunki ......

"inna lillahi wa inna ilaihi rajiun kawai take furtawa a zaunen dake agurin gumi na sake tsatsafo mata , iya abinda ta iya fahimta kenan daga bakin chairman duk sauran maganganun da yacigaba dayi babu abinda ta fahimta hatta Wanda sauran ma'aikatan suka taunana bata fahimci komai ba ,sakamakon zuciyarta data tsaya ta daina aiki na wani lokaci ...

Lokacin da zuciyarta tacigaba da aiki ta dawo cikin hanlinta ta nemi kowa tarasa acikin conference room din sai ita kad'ai zaune ,ashe tuni taron ya watse .
runtse idanunta tayi sosai, wasu zafafan hawaye suka shiga kokuwar zubo mata "me ke shirin faruwa da rayuwata ?

"gidana babu dadi ,bani da jituwa da mahaifina , aikina na neman subuci min ,tabbas wata maseefa na kusanto rayuwata "ya Allah ka kawo min sauki cikin lamarina ,ya Allah karka barni haka, na tuba Allah kasanyaya zuciyar mahaifina akaina ya yafe min abinda nayi masa ,domin nasan bakinsa ne ke bibiyar rayuwata,
ta Dade zaune agurin tana kuka ,ganin kuka da tunani bazai bar kanta ba yasa da kyar tasamu ta mike tsaye tare da gyara zaman mayafinta zuciyarta bata shawarar ta nemi mutane suje su bawa mahaifinta hakuri ya yafe mata, mahaifin sajida shine mutun na farko da zuciyarta ta hasasho mata Amman ina bazata taka kafafunta zuwa gidansa ba, 'yarsa tayi mata katangar karfe Dan wannan gidan har abada bazata sake sanya kafafunta cikinsa ba ,ta kofar baya ta biyo Dan batason jama'a su ganta ,Dan zasu fahimci halin da take ciki ..

kmr jira ake duk inda ka yi acikin ma'aikatar maganar me'ad ake da irin matakin da chairman yace zai d'auka akanta, su mudansir kuwa ansamu abinda ake so ,sai murna suke har da rawa kmr wad'anda akayiwa albishiri da gidan aljannah " kai mutumina wallahi ina cikin farinciki mara misaltuwa ka koma gurin malamin nan naka ya sake k'ara wutar aiki, ayi ayi akoreta wallahi ban so uzirin da chairman yayi mata ba ,naso yayi mata me gabadaya ne injin cewar ma'aruf..
wata uwar dariya mudansir ya kwashe dashi "sha kuruminka abokina komai daki daki yafi ka zuba ido kasha kallo muna nan za'a yi mata me gabadaya..
Tahir ya saukar da ajiyar zuciya daman kuma tun da suka soma mgn bai tsoma bakinsa ba sai yanzu yace "gsky na fara jin tausayinta me zai hana abarta hk idan ka lura tayi sanyi ba kmr lukutan baya ba .
"Kunji shirme banza ,kai ta tafi can kabawa mutane guri ,da alamun ka soma sauya ra'ayinka na bukatar matsayinta daka furta tun farko?
"Ko ban sauya ra'ayina ba nima da wasa na fad'a mgnr , ina ni ina matsayinta, ku kanku kunsa wasa nake yi bazan ta'ba samun matsayinta ba sai wani ikon Allah.
Maaruf yace "mudansir rabu da da wannan shirmammen banza da alamun cutar hauka tasoma kama.....
ai bai kai ga karasa mgnr ba tahir ya cakumi wuyan rigarsa da iyakacin karfinsa "ni ne cutar hauka ta kama,?
"ni zaka cewa hk saboda kai Mara imani ne da tausayi " ina zamu da hakinta ?
"Meye ribarmu idan munyi sanadin rabata da aikinta da har zaka dangantani da kalmar hauka?
Mudansir yayi saurin shiga tsakaninsu "haba tahir meye hk ne ?
wasa yake maka fa bai kamata ka d'auki zafi ba ma'aruf ya fizgo mgn da kyar yace "rabu dashi

ance masa me cutar hauka yayi duk uwar da zai yi ,mahaukaci dolo sauna dakiki..tahir ya kai masa mari sai ga jini ya balle abakinsa abu kmr wasa suka dinga zagin kansu da son yin dambe, da kyar mudansir yasamu ya rabusu tahir yana huci yace "ni... ni ...na cire hanuna acikin shirinku daman kuma ba dani akaje gidan malam ba ,daga yau babu hannuna cikin shirinku duk abinda zaije yazo karku sani ciki azzalume Kawai ya fita yana banko musu kofar da karfi .
suka tsaya sororo suka bi kofar da kallo kirjinsu na mahaukacin bugu"kaji abinda wannan D'an iskan ya fad'a ko ? Ma'aruf ya fad'a yana naushin iska "rabu dashi shima zan gama dashi wata killa kafin ita tabar aikin shi zai rigata barin aikin.

Kai tsaye tahir harabar ma'aikanta ya nufa inda ya iske me'ad tsayen tana zariya abar tausayi, kunnenta manne da waya "wallahi ta bani tausayi ya fad'a acikin zuciyarsa yana jin kmr yaje ya sameta ya sanar daita abinda aka yi mata,Amman yana jin tsoro saboda yasan halinta, yasan yadda take da saurin d'aukar zafi, karshen abun ya juye ya dawo kanshi ,shi kad'ai .
kad'a kansa yayi kawai ya kama gabansa ya koma bakin aikinsa .

************

Zaune Alhaji ediris takai yake agaban amininsa kuma abokin shawararsa mahaifin sajida suna fuskantar juna kafin daga baya yasoma mgn a natse cikin sanyayyiyar murya "me yasa zaka hanata auren abinda take so, ?
"A ganina daga me'ad har sajida abu daya ne agurimu ta wani fannin ma har gara sajida tunda duk rashin son da batawa emran ta hakura ta auresa daga baya Allah ya kawo rabuwa atsakaninsu, Dan haka banga dalilinka na hana auren fu...ya datse harshensa yakasa karasawa saboda baya tunanin zai iya karasa sunan wannnan D'an matsiyatan, shi kansa bazai so sajida ta auresa ba saboda irin tsanar da yayi masa Amman domin kuntatawa me'ad zaiyi tsayin daka ruwa da tsaki akan yaga yaron ya aureta shi da yasan inda zai ga najma har ita sai yabata makudan kudi ta auresa , kawai dan yaga me'ad cikin bakiciki kmr yadda tayi silar jefa safwan da shi kansa da har yanzu wannan bakinciki yaki barinsa.

"abinda bazai ta'ba yiwuwa bane wannan Al cin amanar kauna da yarda ne Sam sajida baza ta'ba auran mijin me'ad ba har abada ...iniji Cewar mahaifin sajida .
Dady yace "ta ina aurensu yazama cin amana ?
"Gsky ni banga wani cin amana ba acikinsa ba.

Mahaifin sajida yace "Ko babu cin amana ai ana barin halak Dan kunya, "banda wannan halak din mahaifin me'ad ya fad'a yana furzar da iska .
muhawura ce tashiga tsakaninsu kowa na kawo hujjarsa Akan auren daga karshe dcp aliyu ya Mike ransa a matukar 'bace ya bar parlour'n saboda idan yacigaba da zama agurin zasu raba gari ,da shi da amininsa da Allah kad'ai yasan tsakaninsu .

Mahaifin me'ad bai bar gidan ba har sai daya gana da sajida inda yake ce mata "ta gayawa wakilan fu'ad su zo su sameshi idan sun tashi ,ita kanta sai alokacin tasan tayi kuskuren son

mijin  aminiyarta  , Amman yazatayi da tata zuciyar datayi kudin balan kamuwa da matsanancin soyayyarsa?

Bayan kwana biyu sajida tasamu me gidan fu'ad da maganar zance aurenta da fu'ad, Amman ta boye masa gurin Wanda zashi neman aurenta,"yace karta damu InshaAllahu zaije ....fu'ad Wanda ya kasa samun natsuwar zuciya gabadaya ya tattara zance wani auren najma da sajida dayake son yi gefe saboda bulayin neman me'ad da sanyin idaniyansa ya taho  guest house din me gidansa inda yafi tunanin zai samesa ya nemi izinin agurin aikinsa domin samun gano inda iyalinsa Suke,yashigo cikin parlour'n dayake zaune yasamu guri ya zauna yana sauke naunayen ajiyar zuciya tare da dafe goshinsa sannan ya gaishe dashi .
Ya amsa yana ajiye magazine din dake rike a hannunsa,yana dubansa "yanzu nake shirin nemanka nan ya karo masa abinda sajida ta bugo ta gaya masa. wata mummunar tashin hankali ya tsinci kansa ciki take gefen  kansa ya Sara ya d'ago agigice yana dubansa batare dayace masa komai ba me gidansa yacigaba da mgn yanzu sai ka sanar min da inda gidansu ita dayar yarinyar take sai ayi abun gabadaya a huta ,sosai fu'ad ke kallonsa da idanunsa da suka gama canza kalla har lokacin sunan mutumin dayaji yafito daga cikin bakinsa yake masa yawo acikin kwakwaluwarsa "to me hakan yake nufi da mahaifin me'ad yabada goyon bayan wannan aure?
Zuciyarsa tabashi amsa da ya yana nufin abubuwa dayawa .
a matukar zuciye ya runtse idanunsa yana tsuma bai tsaya gayawa me gidansa matsayin mutumin dazaije gurinsa neman aure ba ....

Mmn sudais ce💗💗💗💗💗💗
'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
JIDDATULKHAIRI
MARUBUCIYAR
MATAR  DATTIJO

Page 79

......Jikinsa ne yacigaba  tsuma , kansa gaba ɗaya ya kulle, yayi mamakin jin abinda mai gidansa ya fad'a mishi, hankakinsa gaba  daya yagama tashi ,xuciyar sa ta shiga rud'ani, "wai me surukin  nashi yake nufi da shi, ?
"wane irin zato surukin nasa yake masa, ?
"me yasa ya gwammace kar'bar auren sajeeda alhalin lokacin da zai aure me'ad kin amincewa

yayi ? Tambayoyin da ya rika yiwa xuciyarsa kenan .
"Yasan zai yi hkn ne Dan kawai ya bak'antawa me'ad rai .. ..

A fusace ya mike zai bar parlour'n, cikin natsuwa mai gidansa ya kira shi "fu'ad ina zaka je haka,? Tsayawa yayi yana haki batare dayace masa komai ba .
" me yasa naga yanayinka gaba daya ya canja? Dawo ka zauna"

A hankali cikin nutsuwa fu'ad ya dawo ya zauna yana fuskantar mai gidansa. "Gaya min menene damuwar ka fu'ad, naga daga yin wannan Maganar gaba daya ka canja daga farin ciki zuwa akasinsa, hankalinka ya tashi damuwa ta bayyana a idanunka, fad'a min idan akwai wata matsala ne musan yadda zamu shawo kanta "

Sunkuyar da kai fu'ad yayi sannan ya fara yin magana cike da ladabi da girmama ga mai gidan sa
"Yalla'bai shi fa wannan mutumin da zai kar'bi auren sajeeda ba kowa bane face mahaifin me'ad"

Wani irin shock mai gidan nasa yayi lokacin da yaji wannan maganar, "mahaifin me'ad fa ?" Ya maimaita yana kallon fu'ad cike da neman K'arin bayani

"Kwarai kuwa yalla'bai mahaifin me'ad ne ,"Abinda yake ƙara d'aure min kai shi ne ta yadda zai yi ya amshi auren sajeeda alhalin a da can baya lokacin da xan auri me'ad 'ke'kashe ƙasa yayi yace baxan aureta ba, to yanzu kuma wane dalili ne zai sa ya amince na auri sajeeda tabbas nasan akwai wata manufa a cikin zuciyar shi".

Shiru mai gidansa yayi yana nazarin Wad'annan maganganun da fu'ad ya fad'a masa, bayan sun kammala maganar da zasu yi ne suka yi sallama fu'ad ya tashi ya bar me gidansa zaune yana mamakin abinda ke shirin faruwa.

Yana fitowa harabar gidan Motar shi ya bud'e ya shiga sai yaji kamar baxai iya yin driving din ba saboda wannan Maganar da aka yi masa ,tambayar kansa ya shiga yi me Mahaifin me'ad yake nufi da wannan batun da da'akazo masa da shi da rana tsaka, ?
tunani ya rika yi gami da nazari, ba ƙaramin caji ƙwaƙwalwarsa ta rika yi ba a haka har ya isa gida wanka yayi ya sake fita neman me'ad sai bai samu ganinta bai yi tunanin zuwa gurin aikinta ba ,saboda yasan halinta ,kad'an daga cikin halinta su siyar da hali agurin shi kuma abinda bazai so faruwarsa kenan ba .

A ɓangaren me'ad kuma, har yanzu tana fama da matsalar da ita kanta bata san asalinta ba, ba kuma ta san dalilin da yasa ta tsinci kanta a wannan halin ba,sannan har wannan lokacin bata daina tunanin hakunci da chairman din office din su ya fara tunanin yanke mata ba ,ta hanyar dakatar da ita amma sbd kwarewar ta ga iya aikin da jajircewa wajen tsayawa tayi aikin yadda ya kamata yasa ya d'aga mata kafa gabadaya ta fige ta rame tafita haiyacinta ban da kuka babu abinda take ..

Hankalinta kullun sake tashi yake ganin yadda kullum matsalarta gaba take yi bata baya ,hkn yasa ta sake dagewa da addu'a da sadaka da kiyamullaili a kan Allah ya kawo mata karshen wannan matsalar da take ciki, duk da wannan jajircewar da take wajen addu'a da sadaka still dai har yanzu bata iya xama a office dinta domin gudanar da aikinta kamar yadda yakamata ,yayinda tsakanin su mudansir da tahir amintarsu ta dawo sama sama ko nace ta kusan Yankewa, saboda kusan kowa yanzu harkar gabansa yake sai dai a kasan zuciyar mudansir yana jin cewar bazai iya barin tahir hk ba sai ya bisa da bita da kulle.

sajida zaune a d'akinta tana tunanin yadda aurensu zai kasance da fu'ad , ita tana jin idan duk duniya zasu had'u akanta matsawar fu'ad ya amince da aureta zata aureshi ko da kuwa mutuwa me'ad zatayi ,ita Sam bataji kunyar ko tsoro acikin dady'n me'ad zai kar'bi aurenta ,a ganinta ma meye aciki Dan ta auri fu'ad?
"Tana son shi bugu da kari kuma ita me'ad tayi wasa da damarta ta hanyar rashin kulawa da gidanta, yanxu hk tana da labarin duk abinda ya faru daga korar da mahaifinta yayi mata har zuwa neman da fu'ad ya haukace agari yana yi akanta, gashi ita tasan hotel din da me'ad take gaya masa ne kawai ba zatayi ba ,tana nan tana jiran yagaji da nemanta ya hakura ya dawo haiyacinsa suyi aurensu a wuce gurin Dan ta najma me sauki ne ita me tasan yadda zatayi daita a karshe matukar ya aureta bazai ta'ba tunanin wani aurenta ba hatta me'ad din karon kanta zatasa ya manta daita arayuwarsa ,tana cikin wannan tunanin kiran khalid yashigo wayarta,taja dogon tsaki tare da furta another problem sannan ta d'auki wayar "meye ne zaka dameni bafa nason takura
"Ki fito ina jiranki a harabar gidanku ya fad'a atakaice tare da katse kiran .

khalid matashin saurayi ne D'an kimanin shekaru a shirin da shida zuwa da bakwai ,abokin aikinta ne dake bibiyarta da sunan friendship har ta kai daya fito fili ya bayyana mata sirrin dake ransa , Amman fur taki amince masa asalima sai yanke halaka tayi dashi saboda bataga wani abin so ajikinsa ba ,kuma tun daga ranar bata sake barin sun had'u da junansu ba balle ya karanto shirme ,shi kuma babu abinda yake kwadayi da son gani kmrta .duk da bata sanar masa ba yasan komai akan yadda take mugu mugun son fu'ad .

Ta fito sanye cikin wando da rigar body hook Wanda ya matse jikinta sosai ,A tsaye ta sameshi jikin motarsa dake kusa da nata motar ,ya hard'e hannuwansa duka akirji, tun sanda ta fito ya tsurawa surar jikinta idanunsa,yana kallonta daga sama har kasa yake kare mata kallo tsab irin macen da yake burin so da mallaka kenan arayuwarsa ,ji yake duk duniya babu mace me kyawunta sannan yana ji tmkr ya isa gareta ya rungumeta akirjinsa , yanayin yadda yake kallonta kwata kwata baiyi mata ba ,Dan har ya sata jin wani iri ajikinta saboda gabadaya ya tsurawa nonuwanta idanunta kmr zai cinyesu , kallo daya tayi masa ta d'auke idanunta akansa ta haye saman motarta ta zauna tana kallon wayar hannuta batare da tace masa komai ba Khalid kyakkyawa ne shima sai dai bai kai fu'ad a komai ba , gyara tsayuwarsa yayi tare da matsowa gabanta still rungume yake hannunwansa a kirjinsa ahankali yasoma mgn cikin sanyayyiyar muryarsa "plz sajida kinsa na dad'e ina binki ta hanyoyi daban daban , ina sonki kuma tsakanina da Allah ,ki manta kowa ki bani damar na shigo cikin rayuwarki dan Allah....

Ta busar da iskar bakinta idanunta har lokacin yana kan wayarta, kanta  tashiga girgizawa sannan d'ago ahankali tana dubansa a yatsine kana tace " Khalid  Kake ko wa ?
"Wai  me kake tunani Akaina ne?
"meyasa ba zaka fahimceni ba sannan ka fahimci ina  na dosa ,?" Try  to understand me Khalid ....."bana son ka bana kaunar wata halaka da kai kuma halakar da mukayi abaya ta mutunci Allah yasanya mata albarka Amman dan Allah ka fita cikin rayuwata , saboda kai ba irin namijin danake so bane ,you not  can of man I like"
" am not can of man ?ya tambayeta yana tsareta da manya  idanunsa "yes of course ta bashi amsa tare da shayi ko wata fargaba ba sannan ta maida idanunta kan wayarta tacigaba da abinda take.

muryarsa cike da rauni da in ina yace "meye bambamci tsakanina da kalar namijin da kike so?
"khalid.....bana tunanin yau ne zan fara gaya maka wannan mgnr ,I have my type, ina da type din namijin da nake so , wanda zuciyata take so da muradi  ba kai ba ,kuma zan tabbatar da na bawa xuciyata abinda take so tak'arasa mgnr tana  hura masa  iskar  bakinta me zafi  sannan ta tsaresa da idanunta "just forget about any love you have for me coz I can't love you kaje gaba da rayuwarka watakila zakayi cath up wata tasoka but not me ....

 "but ai ni ke zuciyata ta za'ba kuma take muradin rayuwa daita ina sonki saji...."enough khalid don't ever say that rubbish again..bazan ta'ba sonka ba koda kuwa zaka mutu ka dawo sajida nada ra'ayin mijin datake so okay ,"ina son namiji kamili natsatse wanda yasan darajar da ciwon kansa, dogo baki me faffad'an kirji me sex eyes me haiba da Kammala, ma'aboci kyau wanda a duk sanda  na kallesa zanji Feelings dinsa na ratsani ...
" idan na kallesa zan ji dadi acikin zuciyata sannan  zai sani na jini a new level ba kai ba me zaka min ?
"me zanji a tattare da..... ...?

"common short up there my friend karki tozartani akan wannan  sifoffin da kika lisafa ... ni meye na rasa ajikina ?
" meye banda shi acikin abubuwan da kika lisafa?

ta kai hannunta ta gyara gashin kanta daya zubo gefen fuskarta sannan tace "karka fad'i abinda kasan  ba haka bane, da kace duk abubuwan dana lisafa kana dashi khalid ta ina ?
"Ina suke ?
"ina abinda na lisafa?
"Sam ni banga komai ba danake so na namiji ajikinka , da kana da abinda na lisafa da yanzu mun wuce gurin ,abu na karshe da zan gaya Maka ka bar rayuwata ..
Muryasa  a matukar sanyaye yace plz sajida wallahi ina .."

"Ka daina ronkona plz   Dan ba zaka ta'ba samun abinda kake so ba kalleka fa D'an Allah wani gaja gaja da kai .
 kai yanzu bakiji kunyar cewa Kana sona ba a girme na girmeka nesa ba kusa ba Khalid me zan ji aurenka ...? zai yi mgn ta katseshi ta hanyar cewa "stop beging me khalid kaje kaso wata plz..

ya sauke naunauyen ajiyar zuciya tare da zura hannunwansa duka cikin aljihun wandonsa yana fitar da wani hucin Numfashi me gyaraye da tsagwaron 'bacin rai"ammm.. amm naji baki sona sai mijin aminiyarki kike so, saboda shi ne wanda ke da dukkanin tsifofin da kika lisafa ,tell me i want know?
Ta d'ago fuskarta a d'aure tana dubansa shima kallon cikin idanunta yake cike da isgilanci rainasa din datayi "khalid am not long interested on you just live my life plz ...
ya juyar da fuskarsa kad'an yayinda dryrta ta subuce masa yayi murmushin mugunta sannan ya juyo ya fuskanceta "dole ki waskewa mgnta saboda kinsa nasan komai , auren cin amana kike kokarin yi amman bari nagaya miki wani good news, ki hakura ki aureni saboda nasan duk abinda kike bukata daga cikakken nmj wallahi zan miki ,Zan iya cika wannan bombom din naki tsab da zan mararki Dan hk ki daina rainani yaro ne ni a zahirance Amman baki San badini na ba ..kuma ki rubuta ki ajiye a inda bazai goge ba ni ne zan aureki as ending .......
A matukar tsawace tace "plz just go tana nurfafashi tmkr me cutar asma " i don't want see you near me ta fad'i hk cikin murya mai rawa ala'mun tana son yi masa rashin mutunci "
"sajida ...yakira sunanta muryarsa a kasalance "khalid can you live plz ? "dole ne nace bana yi bana sonka bana kaunarka bazan iya soyayya da kai ba ka bar rayuwata mana "naji amman yakamata ki duba girman son danake miki ki bari muyi ...."no no we are not talk to anything just go ...get out ..live ..bye... ta fad'a a matukar harzuke tana me dafe gefen kanta data ji yasoma Sara mata "plz i beg you sajida tayi saurin d'aga masa hannu out bey tana nuna masa kofar get da hannunta.
jimmmmmm yayi yana kallonta sannan ya meida hannuwansa duka cikin aljihun wandonsa yasoma d'aga kafafunsa kmr kazar da kwai ya fashewa aciki tsaki taja ta gyara zamanta tayi consentret akan wayarta datake aikin turawa fu'ad text message tana jin lokacin da me gadi ya bud'e masa get ta juya a matukar fusace "you stupid man if you ever open get to that stupid boy you wil see what wil happen to you," a'a kunji min jaraba da maseefa irinta primature... karami yaro dashi sai jarabar naci ko ya zaiyi dani oho?
"nace banayi banayi !! ana so do.... shiru tayi ta kasa karasa mgnrta taja tsaki kawai ....

cikin sauri fu'ad ya fito daga cikin d'akinsa yana waya sanye da farar singlet da wando sai dai ya d'aura rigar t shirt a saman singlet din bai sanya botira ba "okay ina jinka tana wajen har yanzu ?
Can bangaren kabeer yace "tana wajen Amman kayi sauri da alamun ta kusan gama abinda tazo yi .."dan Allah ka tsayar min daita . Kabir yace "kaima kasan halin wannan rikitacciyar matar taka ba tsayawa zatayi ba ,yanzu ma data ganin bazata tsaya ba .", okay ganin nan zuwa suna tare da nasreen ne ?
"A'a injin cewar kabir cikin sauri fu'ad ya isa ya bud'e motarsa yashiga ya kunna tare da danna hon.....da karfi me gadi ya bud'e masa ya fita aguje.
sai dai yana zuwa yashiga bud'e idanun yaga ta inda zai ganta ,kai tsaye inda kabir ya gaya masa ya nufa da sauri Amman bai ganta ba Dan hk yak'araso gurin kabeer yana riko hannunsa "ina take kabeer ...?
Cire hannunsa kabir yayi cikin nasa yace "wallahil yanzu nan ta wuce naso na bita sai dai banzo da mota ba ,goshinsa ya dafe yashiga zagaye gurin tare da ya furta Allah yana me runtse idanunsa "why me'ad me yasa kike son ruguza mana rayuwarmu alhalin kinsa muna

bukatar juna ..?
Da sauri ya sake dawowa inda kabir yake tsaye yana dubansa cike da matsanancin tausayawa "wani hanya tabi kabir ...?
Kabir ya nuna masa hanyar da tabi ..yabi hanyar da kallo  yana tunanin yabita ne ko ya fita harkarta ya hutawa rayuwarsa, shi daman ba saboda ita bane yake wannan wahalar...
Jiki a sanyaye  ya k'arasa jikin motarsa yana kokarin bud'ewa  kiran sajida  yashigo wayarsa ya ciro wayar daga aljihun gaban rigarsa yana duba screen din wayar,number da  ya gani ne yasashi Jan tsaki , kmr bazai d'auka ba sai kuma ya d'auka "uhmmm meye kuma?
"I lost a lot of things arayuwata amman banaso kaima na rasaka  fu'ad  hope sir malik ya isa maka da sakona?
"Wani banzar sako kenan "sajeeda ya kirata ransa  a matukar 'bace"karki k'ara min matsala da damuwa akan wanda nake ciki ,wai ma Sajid me kike nufi dani  ne ?
"Babu komai sai alkairi kuma InshaAllahu zai tabbata ,tun da har ka furta tare da  amincewa aurena wannan kawai ya isheni  nacigaba da rayuwa har zuwa sanda zamu mallaki juna sannan kuma karshen matsalata tazo  ,ka daina zurfafa tunaninka ,ka daina damuwa  I promise zan baka dukkanin kulawar dakake bukata ,zan baka kulawar daka rasa saboda irin son Da nake ma ...
"common that was not  on fear, sajida bakya sona ki duba kiga yadda nake cikin tashin hankali akan matsalar gidana nasan kinsa komai amman ke k'ok'ari kike kawai a d'aura mana aure.
"Tabbas aurenmu shine agabana kuma shine abinda nake buri a halin yanzu sannan zanyi  Iya kokarina naga na mallakeka  , yanzu dai kana ina ,Dan ina son mu had'u da kai akwai maganar da zamuyi very important"

"bani da lokacinki a halin yanzu neman inda matata da yarinyata nake "ta kwashe da wata uwar dry sannan tace  "ka sani ko nasan inda matarka take da yarinyarka just try and come...jikinsa yayi sanyi yasoma ya rage murya "Dan Allah ko kinsa inda take ne ki gaya min ...?
"Uhmm a'a ban sani ba ,Amman ka dai kazo akwai Wanda yasani "rubbish ya furta a harzuke ganin raina masa wayo take son yi akwai siyar data sake shirya masa ,shi kuma ya ranse ba zai sake barin su had' u ba either ko tazama matarsa ko km sun rabu ..."ba zaka zo ba kenan ?"yes of course banzo  wawiya kawai maciya amana ke auren ma na fasa inga uban da zai sani aurenki ...ta saki wata razannaniyar k' ara tare da durowa daga saman gadonta tana furta "what?
"Abinda kunnenki yaji shi na fad'a na fasa aurenki kibar rayuwata simple as that "
Muryarta na rawa tace" Dan girman Allah Allah fu'ad kar ka fasa au..sai kuma kiyi ya katse kiransa tare da shigewa motarsa ya bar gurin aguje..

**********

Yau takama Monday Wanda ko bature na tsoron ranar da girmamata rana ce da duk wani ma'aikaci ke jin tsorota da taka tsantsar daita  ,me'ad  tana zaune acikin motarta kmr koda yaushe tana tunanin yadda xata bullowa wannan matsalar da ta addabe ta , taji an kwankwasa glas din motarta  da  sauri ta d'ago kanta, tare da bud'e murfin mota ,daya daga cikin staff din company ne ya bayyana agabanta bayan sun gaisa yake fad'a mata cewa chairman yana son

ganinta a office din sa.

A sanyaye ta fito daga cikin motar tare yiwa motar key , da sallama ta shiga office din tare da neman kujerar da ke ajiye a gefe ta xauna gabanta na wani irin fad'uwa , bayan sun kammala gaisawa da chairman ya shiga jefa mata wasu tambayoyi.

"Har yanzu na kasa ganin wani canji daga gare ki me'ad ,dan Allah ki fad'a min abinda yake damunki bana so ki boye min komai, Ni dai nasan da ba haka kike ba sam ban sanki da sakaci ko wasa da aiki ba, me yasa Yanzu abubuwa suke neman tabar'barewa Company? Ina jiran amsa daga gare ki kuma bana so ki boye min gaskiyar abinda ke faruwa da ke.

Kuka mai tsanani me'ad ta shiga yi, sai da tayi kukan da ya ishe ta sannan ta zayyana mishi dukkan halin da take ciki.
Ya tausaya mata sosai kuma yayi alƙawarin insha Allah matsalar da take ciki da mahaifinta yazo ƙarshe godiya tayi masa, yacigaba da mgn yana duba file din su ma'aruf "kinsa cewa wannan rashin zamamki cikin office dinki , sammu akayi miki ?
mead ta d'ago kanta a matukar firgice tana dubansa cike da mamaki da matsanancin tsoro, "kina mamaki ko ,?tayi saurin d'aga masa kai alamun Eh "karkiyi mamaki mead akan samu irin haka .
bakinta na rawa tace " ni kuwa wa nayi laifi da har zai min samu akan aikina ?
Chairman yace "kina son sani ko su waye ?
Jikinta na rawa tashiga girgiza masa alamun eh"
"okay ina zuwa "ya d'auki wayarsa ya kira messenger cikin minti biyu yashigo jeka ka cewa acp ya shigo min da yaran nan kafi ya wuce dasu "okay sir ya fita da sauri ..

Ahankali taji an bud'e kofar gabadaya ta kasa juya saboda jikinta daya d'auki rawa har sai da charman yace "ki juya mana kiga yan iskan da suka miki aika aika da kokarin rabaki da hanyar abincinki "
jikinta na cigaba da kyarma ta soma juyawa ahankali har ta juyo gbdy idanunta ya sauka akan tahir da mudansir da ma'aruf dukanindu hannunwansu da handcuff, take gabanta yayi wani irin dukan uku uku yashiga fad'uwa tashiga nunasu da hannunta bakinta na rawa "ku..ku ne kuka min sai kuma ta rushe da kuka "laifin me na muku da kuka shirya min wannan munakisar?
"A halin yanzu ba sai kayiwa mutun komai ba zai nufeka da sharri inji cewar chairman "wasu mutane suna nan su kawai basa son ganin cigabanka ,sun fi so kullun suganka kana bara akan titi 'acp a wuce dasu sannan ayi musu azaba me rad'ad'i har sai sun gaya muku malamin dayayi musu wannan aiki, if possible ma a asakasu a under ground har sai sun fad'a Dan babu yadda banyi dasu ba, alokacin Dana kamasu suna tad'in Dana takurasu ne ma sukace tare da tahir akayi komai "
Acp yace"Karka damu kana zaune zamu zo maka da good news. "Okay nagode sosai tare da mikawa acp hannu sannan suka juya suka bar office din .

Wani irin kuka me'ad take kmr ranta zai fita chairman nacigaba da bata hakuri"ba kuka yakamata kiyi ba illa ki godewa Allah da asiri ya tono if not ,hk kina ji kina gani aikinki zai bar

hannunki "nagode nagode har bansa kalar godiyar da zan maka ba ,a yau na k'ara sani duniya ba'akin komai take ba, nasan watakilla sunyi min hk ne saboda yadda nake takura musu  akan aikinsu ,kuma fa ni ina yi musu hkn bada wata manufa ba sai Dan su tsaya akan aikinsu kar ya subuce musu Amman babu komai nagodewa Allah daya nuna min su a tafin hannuna  ......

Tun daga wannan lokaci chairman ya nemi manyan mutane wad'an da yasan suna muamula da mahaifin me'ad Sannan ya nemi mahaifin sajeeda domin shine kan gaba a komai  agurin mahaifinta,domin  a zauna da shi a bashi hakuri a roke shi gafara a kan laifin da me'ad tayi masa.

sunje kmr yadda  Chairman ya bukata sai dai da kyar alhj ediris ya yarda me'ad tashigo masa gida .
Bayan sun gama gaisawa suka soma magana akan abinda ya kawosu"alhaji jabir  yace "alhj ediris abinda ya kawo mu akan batun yarinyarka me'ad ne..
Dady yayi sauron katse masa  maganar ta hanyar cewa "ni bani da wata yarinya me'ad arayuwata ,yarinya daya gareni kuma sunan suhailat Dan hk kayi wata mgnr ban da  wannan"

da sauri me'ad tashiga  Jan gwiwowinta tana kuka "Dan girman Allah dady kayi hakuri ka yafe min ,kayi hakuri wallahi nayi nadama ka daina cireni acikin ya'yanka ...kuka take sosai tana bashi hakuri "Dan Allah ku bashi hakuri  ya yafe min wallahi na tuba bazan sake ba, ku gaya masa duk abinda yake so zanyi masa bazan sake ketare zancesa ba, na tuba dady nabi Allah da manzonsa nabinka ka taimakeni ka taimaki rayuwata banida kamarka ,kaine ubana, bani da wani uban dayafika kamin komai arayuwa ka inganta rayuwata ka gatantani kayi min komai ,kayi  hakuri nasan ban kyauta maka ba .....
"Banice yakamata nayi maka abinda nayi ba .....,Amman banida yadda zanyi ,bani da yadda zanyi da kaddara data gitta akaina, kayiwa darajar Allah kace ka yafe min ko al'amurana zasu daidaita jikin jama'ar dake gurin yayi sanyi hk ma dady karan kanshi .
Sai dai yayi shiru yana aikin  jijiga kafarsa, nan kowa yashiga topa albarkacin bakinsa, wannan yayi nasiha yayi shiru ,wani ma yakama da kyar dai akasamu jikinsa yayi sanyi gbdy , ya sauke naunayen ajiyar zuciya Wanda ke nuna ya sauko.

mahaifin sajida yace "me'ad matsa kusa da mahaifinki sosai ki sake  rokosa gafara kinji " cikin rawar jiki ta sake  tsugunna har ƙasa ta roke shi gafara, bai yi gardama ba yace zai yafe mata amma tare da sharad'in kowa yayi tsuru tsuru agurin suna kallonsa tare da mamakinsa "

Mahaifin sajida ne yayi karfin halin cewa "wani sharadi ne wannan ?
"Sharadina shine zan raba aurenta da fu'ad saboda ni fu'ad din ne gaba daya bana  sonta dashi ......."na tsine  shi na tsani  naga suna tarayya da 'yata , indai har tana buƙatar yafiyata to tabbas sai ta rabu da fu'ad..
kuma rabuwa ta har abada idan har ta amince da haka zan yafe mata kuma za ta zauna a gidana  ta ci-gaba da rayuwa tare dani kmr can baya amma fa batare da auren fu'ad ba..

Mmn sudais ce💗💗💗💗💗💗

'YAN CINKI
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

*AYSHA  A BAGUDO*

~DEDICATED TO~
JIDDATULKHAIRI
MARUBUCIYAR
MATAR  DATTIJO

Page 80

......'kwa'kwaluwarta ce ta tsaya ta daina processing na wani lokaci kafin  daga baya ta cigaba da bugawa, ji take mgnrsa ba iya cikin kunnuwanta kad'ai suka  tsaya ba har cikin zuciyarta take jin komai ,ta sake matsowa sosai kusa da mahaifinta wasu zafafan hawaye suka shiga gangarowa akan kuncinta.

Tafukan hannuwanta ta d'aura a saman  kafafuwansa dady Cikin mataanancin kuka, gabadayan idanunta dake zubar da ruwan hawaye ta tsurawa mahaifinta tana kallonsa tana son ya karyata mata abinda taji ya fito daga cikin bakinsa, yace "mata wasa yake mata ba gaske bane ,saboda  d'acin kalmar tafi kowace kalma muni da zafi me  ta'bo zuciya da wuyar mantawa , Amman sake maimaita kalmar da dady  yayi ya tabbatar mata da iyakacin gaskiyarsa yake nufin raba aurenta da fu'ad a.

take  ta dinga furta kalmar "inna lillahi wa inna ilaihi rajiun  "shikenan ta faru dani takare ta fad'i hk acikin ranta cikin matsanancin tashin hankali" yaushe ne zan sake samu 'yancin da rayuwa mai dadi kmr rayuwarta ta baya ?
,tun kafin jamar gurin suyi yunkurin mgn tashiga fad'i" shikenan shikenan !!! dady naji na amince na yarda da wannan sharad'in naka matukar zaka ya femin  , domin ni yanzu  nafi son farin cikinka a kan farin cikin kowa, duk abinda kake so shi  zanyi ,bani da za'bin daya wuce naka ..
Tana mgn tana kuka zuciyarta na rawa da  gargadinta a kan abinda take shirin aikatawa rayuwata ..
"tana son fu'ad tamkar  ranta, kuma bata jin cewa xata iya ci-gaba da rayuwa ba tare dashi ba,Amman a halin yanzu  ta za'bi farincikin mahaifinta akan ta cigaba da zama dashi ,zata cigaba rayuwarta  babu shi acikin duniyarta , ta gwamaci ta yiwa mahaifinta biyayya a karo na farko ko rayuwarta zata daidaita    ,koda kuwa rabuwa da fu'ad din  zai zama   silar barinta duniya.....
a yanzu ta yarda ta fad'a kowane irin yanayi ne matukar dai mahaifinta zai yi farin ciki ya amshita amatsayin diyarsa sa'banin shekarun baya ,da ya fita lamarinta   ......
"xata yi k'ok'arin k'arasa  fitar da ragowar soyayyar fu'ad daga cikin xuciyar tayi rayuwarta da

iyayenta da tilon diyarta.
Kanta a sunkuye ta cigaba maimata mgn "Daddy na yarda ..,dady na amince duk Abinda kake so a halin yanzu zan yi, ba ni da wani buri a rayuwata sama da na faranta maka, sama da na kyautata maka nayi maka biyayya a kan duk abinda kake bukata daga gare ni, duk abinda kake so xan yi maka shi Daddy....
Takarasa mgnr tana wani irin kuka me ta'ba zuciya kuka take sosai tmkr ranta zai fita gabadaya duniya ta cukud'e mata waje daya bata ta'ba hk tashin hankali irin wannan da take ciki yake da muni da ciwo ba ,ta d'auka rashin son da dady yakewa fu'ad zai tsaya a iya hk ne ,ta d'auka rad'ad'in tuni ta tsaya a wancan lokacin ,ta d'auka ko darajar samun nasreen atsananinsu zai sauk'ak'awa zuciyarsa kiyayyar fu'ad .....
Amman da kalamansa na yanzu ta fahimci komai ya sauya agareta ,ta gane ita din ba kowa bace, tasoma fahimtar talaka marashi da galihu ya fita kwanciyar hankali sau dubu.
yanzu wakilla najma datake kallo mafi kaskancin gani akanta tafita kwanciyar hankali da walwala .
"yau din tazo mata da tashin hankali da rud'anin rayuwa maramisaltu "ya zatayi da kaddarar data gifta mata da rayuwarta gabadaya? Parlour'n ya d'auki shiru ,gabadaya jama'ar dake zaune acikinsa sun rafka uban tagumi, ban da sautin kukan me'ad bakajin sautin komai acikin parlour'n .....

Yayinda Mahaifinta yaji dadin jin kalaman daya fito daga bakin 'yar tasa, a nan take ya fahimci me'ad dinsa ta sauya ,ta samu natsuwa, ta k'ara hankali fiyye da lokutan baya, sannan da gaske take nufin nadamar abinda tayi masa a baya ,sannan a halin yanzu yasan ko zuwa gaba yace mata "ga abinda yake son tayi masa tayi batare da sa'bawa umarninsa ba.
cike da matsanancin farinciki da jin dadi yace "me'ad na yafe miki duniya da lahira Allah kuma yayi miki albarka, Sannan amatsayina, na mahaifi gareki ina umartarki daki baro hotel din da kika kama ki dawo gidan ubanki da zama .

Alhaji gali yayi saurin sauke hannunsa dayayi tagumi dashi tare da numfasawa yace " yanzu alhj ediris wannan d'ayen hukuncin daka yanke kana ganin abune me bulewa, raba ma'aurata da rana tsaka alhalin suna son junansu..? "Ni aganina hkn bai kamata ba ,idan shi yaron laifi yayi maka kamatayi a nemeshi ya baka hakuri ba rabashi da matarsa ba alhalin tana son shi ...
Da sauri me'ad ta d'ago idanunta da har wannan lokacin basu daina tsiyayar ruwan hawaye ba tace "No.....dady kubar hukuncin da mahaifina ya yanke akaina kawai kada ku tursashi ,ni koda ina son fu'ad zan iya rabuwa dashi, ballanatana ahalin yanzu babu d'igonsa sonsa ko daya araina ni dai ku taya sake bawa mahaifina hakuri, nagode nagode da kulawarku gareni ,yadda kuka tsaya kuka gyara tsakanina da mahaifina, ina muku adduar allah ya biya muku bukatunku na alkairi, nagode nagode har bansan irin godiyar da zan muku ba ..
jikinsu yayi mugun mugun sanyi babu wanda ya sake yunkurin cewa komai bisa lafazin bakin me'ad ,hk kowanensu ya tashi jiki a sanyaye suka soma mikawa juna hannu suna sallama da juna tare da k'ok'arin barin parlour'n,a tare suka fita har me'ad kowane yashiga motarsa itama tashiga nata motarta da niyyar d'auko nasreen daga school sannan .

kasa tukin tayi ta gangarawa gefen titi tayi parking tare da d'aura kanta saman sitiyari ta fashe

da wani irin gigitaccen kuka, gbdy tasoma datasanin barin gidan mijinta datayi
...kuka take sosai yayinda zuciyarta ke sake bud'ewa a wajajen ,da duk ciwoka suka samu muhalli, jikinta yayi mata sanyi,zuciyarta ta dinga tsinkewa har take jin tmkr batayiwa kanta adalcin rabuwa dashi ba,"ina Zata sake samun madadinsa?
"Ina Zata samu jarumi jajjirtaccen miji irinsa ?
bata San lokacin data d'auka tsaye agurin ba zuciyarta ke mata zafi had'e da tsinkewa ahankali take sake jin ciwon abinda fu'ad din yayi mata , sai da taci kukanta ta koshi sannan ta tada motar tabar gurin .

a kan hanyarta ta dawo gida bayan ta d'auko nasreen, yarinyar take tambayarta abinda ke damunta "momy me ke damunki da alamun kina cikin damuwa koma nace kmr kinyi kuka ko..?
"Bby banyi kuka ba idona ke min ciwo ,hk gefen kaina kmr zai fita kimin addua kinji bby .... ta k'arasa mgnr tana meida hawayen da yayi k'ok'arin zubowa .
nasreen ta d'aura hannunta akan na momy'nta dake Kan giyar mota sannan muryarta a raunane tace " momy allah ya baki lfy ,but ki daina damuwa,Dan Nasan damuwa ne akan auren dady ko?
" but momy ina tabbatar miki dady ba zai auri daya daga cikinsu ba ,saboda dady najin mgnta ba zai yi abinda banaso ba ,nagaya masa banason yayi miki kishiya da aunty sajida da najma. ..
girgiza kanta kawai me'ad tayi "yaro duk inda yake yaro ne ... hanyar da nasreen taga me'ad ta d'auka ne sa'banin masaukinsu yasa ta sake fuskantarta sosai "momy ina kuma zaki kaimu ba hotel zamu ba ,? Tayi uwar tmby jikinta na rawa rawa "Dan Allah karki kaimu gidan grandpa yacika fad'a dayawa sannan kuma bayason dady'na nima...."short up there my friend I don't want here any from you just keep your mouth short ...tacigaba da tukinta batare da ta sake kallon inda take ba .
yayinda nasreen ta sakar mata kukan ita baza taje gidan grandpa ba, gara ta kai ta gurin dadynta.....
kukan datake yana ta'ba zuciyarta kuma batason kukanta saboda ,da zaran jikinta ya d'auki zafi shikenan .. ciwonta zai tashi Amman babu yadda ta iya da rayuwata ,hkn datayi shine kwanciyar hankalinta da samun natsuwarta ,duk ita tajawo komai daya faru dasu sai dai bata bakinciki da hukuncin da mahaifina ya zarta akanta ...
har suka shigo harabar gidan kuka nasreen take, taki fitowa daga cikin motar sai da me'ad ta zagaya ta fito daita tashiga turturjewa ita sam bazata shiga cikin gidan ba "Dan Allah momy karki shiga dani banason gidan ....plz momy .

alhj ediris dake saman barandarsa tsaye idanunsa ya sauka akansu sai yau yagama k'arewa yanayin yarinyar kallo , kyakkywace kmr me'ad dinsa ,sai dai kusan yanayinta na ubanta ne ,abubuwa kad'an ta d'auko na uwarta ....
Haushi ne yakamashi ganin yadda ake dambe daita akan bazata shiga gidansa ba, to me hkn yake nufi kenan...?
Ransa a matukar 'bace ya saki wata razananniyar tsawa tare da cewa "ki barta anan kishigo abinki idan bazata shigo ba ,wata irin gigicewa nasreen tayi tare da kwakume me'ad ajikinta "Wayyohlly Allah momy tsoro nakeji .....momy momy tsoro nake ji ki fita dani daga gidan nan tsoro nake ji .....

ahankalin  me'ad yayi mugu mugun tashi take hawaye ya balle mata yashiga gudana a saman kuncinta, ahankali ta rungumeta ajikinta tashiga shafa mata kanta zuwa bayan ",cool down my baby nothing wel happen to you, just trust your mom....ki saki jikinki babu abinda grandpa zai yi miki he really loves you rarrashinta ta dinga yi yayinda har lokacin idanun dady ke kansu, ya kasa d'auke idanunsa akansu jiki a sanyaye me'ad ta yunkura tare da d'aukarta ta rungume kasancewar nasreen din  bata da wani girma gashi babu kiba sai zallar farin fata da tsagwaron kyawun  data d'auko daga iyayenta. .....
suna shiga cikin gidan me'ad ta kwantar da nasreen akan doguwar kujera 3 siter tana shafa kwanta yarinyar ta runtse idanunta gam batason ganin kowa har lokacin bata daina furta "tsoro take ji ba a fitar daita daga gidan .

Me'ad tasamu guri ta zauna a gefen kujerar da momy ke zaune ta zuba uwar tagumi tana zubarwa da hawaye saboda duk abinda ya faru acikin kunnenta akayisa "Sam bataji dadin furucin dady ba ,Amman tasan tana yin wata mgn nata ne zaiyi zafi .
me'ad ta kai hannunta zata cire tagumin datayi kenan  suhailat tasanyo kai cikin parlour'n dawowarta kenan daga exam dinta karshe daga shi za'a turasu bautar k'asa.
 da sauri ta k'araso ta rungume me'ad tana murnar ganin sai dai ganin yanayinsu ya sanyayar mata da gwiwa tayi tsuru tsuru tana kallonnsu zuciyarta na wani irin bugawa "aunty me'ad momy lfy na ganku wani iri ko wani abu ne ya faru da dady byn fitata?
Kuka momy ta fashe dashi sannan tashiga koro mata duk abinda ya faru .
wata irin zabura suhailat tayi tana furta kalmar inna lillahi wa inna ilaihi rajiun  sai maimata kalmar take hankalinta a matukar tashe cikin tsananin rud'u ,tana duban me'ad da wata irin gigitaccen duba muryarta a sarke tace " me ya zanyo kikayi  mummunar wannan tunanin anti?

Me'ad ta cije le'benta alamun damuwarta ta kai makura "ai kinga irinta ko anti?" kinga irin taurin kan naki ba ?
"gashi zaki yi sanadiyar kashe auren dake kad'ai kika San irin wahalar da kika sha akansa .
"watakilla da kinyi hakuri kin zauna ad'akin mijinki  da yanzu duk hkn bata faru ba, Dan nasan ko bade dady zai yafe miki wallahi tallahi matsawar aurenki ya mutu ki sani kin yanki tikitin zawarci na shekara Goma sha.... ko fiyye da hakan ga dai karamin misali nan akan aunty sajida banda sauran mata da basamu sani ba ,me'ad tayi saurin runtse idanunta saboda sunan sajida da suhailat ta ambata.

Suhailat tacigaba da mgn " kin guji mijinki Dan zai k'ara aure ke yanzu a tunaninki idan aurenki ya mutu mara mata ne zai zo yace yana sonki zai aureki?
Sam ki canza tunani ki koma kibawa dady hakuri ya janye wannan  furucin NASA ...suhailat takarasa maganar da sheshekar kuka Wanda ya k'ara dama lisafin me'ad har ta kasa kuka illa girgiza kai kawai datake kmr wata kadangaruwa.."take ciwon so yashiga   dawainiyya daita a zaune datake ahankali ta sake  runtse idanunta gam fu'ad zuciyarta  tasoma hasko mata ," ta yaya zata iya rabuwa dashi ? Anya kuwa bata yaudari kanta ba ? Ta bude idanunta tare da zubawa suhailat ido gbdy ta kasa mgn suhailat ta sauke wata ajiyar zuciya mai bayyanan ne ciwo akirji "bari naje nasamu dady Dan Allah ya sausauta rayuwarma guda na wace ,idan da sauran zama tsakaninku sai rabo yazo ya kasheshi azo ana kuka.....

ganin ta yunkura ta Mike me'ad tayi saurin meidata mazauninta "kiyi hakuri suhailat karkije ni kad'ai nasan kunci Dana shiga a sanadiyar fushinsa gareni, yau nasamu da kyar ya sauko har ya sake amincewa dani amatsayin diyarsa, Dan Allah karkiyi abinda zai sa a sake maimata tarihi fu'ad dai ni na kawoshi nace ina sonshi a yau kuma nace banasonshi .....
dan kowa ya d'auka wata halaka ko dangantaka bata ta'ba shiga tsakaninmu ba ..
tana gama fad'ar hk ta mike hawaye nabin kuncinta tashige d'akin momy ta fad'a kan gado, ta kwanta ruf da ciki ta fashe da wani irin gigitaccen kuka "na barka bari na har abada kai din ma baka cancanci na sake butulcewa mahaifina akanka ba ,kai din maci amanar kauna ne gareni Allah yasa rabuwarmu tazama alkairi a rayuwata Allah ya had'a kowa da rabonsa na alkairi.....

**********

Bangaren mahaifin sajida kuwa daga gidansu me'ad kai tsaye gidansa ya nufa ana k'ok'arin bud'e masa get idanunsa ya sauka akan Khalid da wasu daga cikin security's din bakin get ke dambe dashi na lallai sai an barshi yashiga gidan ,ai kuwa ana k'arasa bud'e masa ,atare suka shiga gidan .bayan direbansa yayi parking a inda aka tanada domin ajiye motoci da sauri ya fito batare daya rufe murfin motar ba ya k'araso bakin kofar da mahaifin sajida yake ,ya bud'e masa kafafunsa yasoma sanyowa waje sannan gangar jikinsa ta bayyana inda gbdy security's suka caaaa akansa kowanensu na rusunawa cike da girmamawa shima Khalid yakaraso yayi kmr yadda sukayi mahaifin sajida yabishi da kallo yana tunanin inda yasansa Amman duk tunaninsa yayi bai gano inda yasan yaron ba ,juyowa yayi ga security ganin K'arin bayani yake nema daga garesu yasa suka shiga rige Rigen gaya masa abinda ke tafe da Khalid ya jinjina kai yana sake karewa yaron kallon tsab yaro ne karami sosai Dan nesa ba kusa ba yasan sajida ta girme masa zatayi kani kusan na uku dashi hannun mahaifin sajida ya d'aga musu alamun suka gamansu sannan yace wa Khalid "biyo yaro ,yana gaba khalid na biye dashi abaya har cikin wani rantsentsan parlour'n dayaji kayan more rayuwar duniya yace ya zauna yana zuwa ,shi kuma yak'arasa ciki ,Khalid ya zauna tare da yin balance yana murza tafukan hannuwansa tsanyi ac Dana murna na ratsashi tmkr Wanda akayiwa albishiri da an bashi auren sajida.

Mahaifin sajida nashigowa parlour'n sautin muryarta yasoma jiyowa cikin fad'a "Dan iskan yaro kawai ko me zanyi da kai ?
"me zan ci da kai yaro karami da kai sai tsaurin ido ,okay Dan kaga ranar farko kayi nasarar shigowa, shine yau ma ka kwaso jiki kazo Allah yasa suyi maka dukan mutuwa su karairaka useless kawai, tana ganin mahaifinta tayi saurin waske tana susa tsakiyar gashin kanta sannan tayi masa sannu da zuwa ,ya amsa ransa a sake sannan yashiga d'akinsa bayansa tabi da kallo tana adduar Allah yasa bai ga Khalid ba .
shigarsa d'akin bai fi minti goma ba ya sake fitowa ya nufi inda Khalid yake bayan ya bada umarnin akawo masa abun motsa baki . Yashigo bakinsa d'auke da sallama, Khalid na ganinsa ya sake rusunawa had'e da amsa sallama ,mahafin sajida yasamu guri opposite din Khalid ya zauna
yana fuskantarshi, tsawon minti goma yana zaune yana kallon Khalid tare da nazarinsa ,me aiki tashigo rike da tire ta janyo karamin stood ta ajiye tiren akai ta juya .
"meye ne sunanka mahaifin sajida ya fad'a yana gyara zamansa?

Cikin rawa murya yace "Kha..Khalid ismail money mis road ne sir.." dady ya maimaita sunan saboda yasan Ismail mony mis road, ya jinjina kai kana yace
"malam Khalid ga abun motsa bakin nan kasoma dashi tukun muyi mgn "
"a koshe nake dady "kai kuwa kasha ko kad'an ne "ok na gode sosai ,yasa hannu ya tsiyaye tattaciyar ruwan inibi acikin cup ya cur'ba kad'an ya ajiye cup, yana sake gyara zamansa shima ya fuskance mahaifin sajida kmr yadda yayi masa kuri da ido . "Kace Khalid Ismail mony mis road kai din D'an cikinsa ne ?
"Eh ....."ikon Allah"
" me ke tsakaninka da sajida diyata?
Batare da 'bata lokaci ba Khalid ya zayyane masa komai ."ka tabbatar kana sonta ?
Khalid yace "sosai ma dady sai dai ita din ce kmr take raina ni a cewarta na...."ka manta da duk wani raini kai dai ba dai kana sonta ba kuma kana da inda zaka ajiyeta ba ?
Khalid ya girgiza kansa alamun Eh " to ka turo min mahaifinka muyi magana ta kunne da kunne dashi yana gama fad'ar ya Mike "kayi k'ok'arin ka ci duk abinda aka kawo maka sannan ya juya ya fita daga parlour'n, ai ko babu kunya khalid ya zauna ya take cikinsa ,Dan yana son cin irin abubuwan Amman mugun son kudinsa daya gada Gurin mahaifinsa baya bari fitowa yayi yana d'ad'd'agawa security's kafad'u ,a zuwan shima yanzu wani ne acikin gidan.

*************

Sajida fu'ad zaune agaban me gidansa, yayinda fu'ad sai faman cika yake yana batsewa tare da zabga mata harara ,saboda ya tsani yadda take zuwa kawo complain dinsa ga uban gidansa, daya zame masa tmkr uba garesa.
Cikin murya kuka tasoma mgn "sir Malik ka taimakeni kar zance aurenmu ya rushe gbdy narasa gane Kan fu'ad aka. " dakata dakata !! Munafuka ta yaya zaki gane kaina, muguwa azaluma maci amanar kauna?
sir kana kallon yarinyar nan katuwar muguwar makira ce ta bugawa ajarida, kwata kwata batasona da matata, sannan son datake ikirari tana min karya ne.......
"Saboda zaka fadi hk ?
Inji cewar sir Malik "na karyata hkn ne saboda ina dalilina ,Dan da ace son gsky sajida take min da ta tausayawa rayuwata ta gaya min inda matata da 'yata suke....
Kallonta sir malik yayi "ke kinsa inda matarsa take ne ?
Tayi saurin girgiza masa kai alamun eh "
"Kaji ko Amman tana kallona agari ina yawo bulayin nemanta ta kasa gaya min to ni kuwa me zanyi dake sajida?
"Bari nagaya miki wallahi wallahi bana sonki kuma ban taba jin digon sonki a zuciyata ba ,na dai amincewa aurenki ne saboda yanayin da kike k'ok'arin ganin kin sanyani ciki alhalin ni ba ma'abocin hkn bane . Sannan baki son matata sajida.."karka ce wallahi ina .."short ya buga Mata tsawa "ta ina kike sonta?
" tambayarki ki gaya min baya ga zuga min ita da kike okay kin d'auka ban sani ba ?
"Kisani bazan ta'ba aurenki ba ,ke ko mutuwa me'ad tayi bazan aureki ba ..."karka fad'i sir malik yayi saurin katse shi " wallahi wallahi aaaaaaaa karka rantse "wallahi bazan aureta ba wannan shine maganata takarshe daita yana gama fadar hk ya Mike ya bar parlour'n, durkushewa tayi agurin tana kuka "Dan Allah kataimakeni kace masa ya dawo duk abinda yake tunani ba hk

bane ,wayyohlly Allah kuka take kmr wata karamar yarinyar "ki kwantar da hankalinki zan rarrasheshi zan sa yayi kaffaran rantsuwar  da yayi InshaAllahu ke dai ki cigaba da addu'a idan da rabo sai ayi da wannan maganar ya kwantar mata da hankali ta wuce.

********

Bayan mead ta dawo gida da sati daya , fu'ad yasamu labari tana gidansu  ,Dan haka yayiwa gidan diran makiya , inda ya iske dady a parlour'n farko na gidan ya hakince acikin kujera , yashigo bakinsa d'auke da  sallama , zuciyarsa babu wani fargaba ko tsoro ya gaishe da dady cike da girmamawa ,Wanda iya sallamar kawai dady ya amsa shima aciki , ya samu guri ya zauna batare da anyi masa izini ba .

parlour'n ya d'auki shiru kusan minti talatin dady bai tambayi abinda ya kawosa ba, hk zalika shima fuad bai yi mgn ba har sanda nasreen wacce tagaji da jiran , tasanyo kai cikin parlour'n Dan  shigowar mahaifinta ya faru ne akan idanunta da gudu tashige jikinsa tana murnar ganinsa "I miss you my special dady.....shima rungumeta yayi tsam ajikinsa yana sauke naunayen ajiyar zuciya kana yace "I really miss you too my special bby how  are you doing ?
"Am fine dady wani irin sanyin dadi ne yake jin yana ratsashi , yayinda zuciyar dady kad'an yarage batayi bundiga ba ,tsabar takaici da taanarsa ga fu'ad..

